[6/21, 9:53 PM] Mugiratmusa66: 🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥
*MAYYA CE*
🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥

*INTELLIGENT WRITER'S ASSOCIATION ®*✍🏻
_[Onward together]_

*Written by Mugirat Musa*

*DEDICATED TO SIS NAJER'ART*

_Bismillahir rahamanir rahim_

*PAGE 1*

Wasu yara ne ke wasa su uku,,, yaran bazasu wuce shekara goma sha uku ba zuwa sha hud'u .'Dayar ce mai suna Fatima ta dubi 'yan uwan wasanta Maryam da Fadila,,, tace "Maryam ya kamata muje gida yanzu fa,, mun dad'e sosai muna wasa gashi rana ta fara fitowa ".Fadila tayi charab ta chafke maganar tana hararar Fatima,, sannan tace "ke idan kin gaji da yin wasa ne mu bamu gaji ba,, saboda haka ga hanya nan ki wuce zuwa gida babu wanda ya tareki ".Fatima ta dubi Fadila duba na rashin son fad'a,, tace "haba Fadila dad'ina dake akwai saurin fushi,, ni dama wasa kawai nakeyi muku na fad'i haka ne saboda kada a nememu arasa a gida "."To wa

ne aiki ne zamuyi idan muka koma gida,, nidai gaskiya ban gaji da yin wasa ba ".Cewar Fadila cikeda rashin son maganar.
Sai asannan ne Maryam ta dubi Fadila tace "ya isa Fadila abar maganar,, kada abin ya zamar muku fad'a a tsakaninku muji kunya. Amma ai gaskiya Fatima ta ke fad'a ba k'arya ba ".Fatima tace "k'yaleta Maryam ai ya riga ya wuce adaina tunawa "."To shikenan babu komai ai ".Cewar Maryam dayake ita yarinya ce nutsattsiya mara son magana sosai,, sunyi shiru dukansu na tsawon lokaci,,, can dai Fadila ta katse musu shurun tace "ku zo mu fara 'yar chahu muna gamawa muyi gida ko,, amma nice ta farko ".Fatima da Maryam suka gyara zamansu domin suji dad'in wasar,, Fatima tace "ni ce ta biyu "."Ni kuma ta uku ".Inji Maryam cikeda natsuwa da kwanciyar hankali.

Suna tsakar wasarsu cikeda matuk'ar jin dad'i da nishad'i sosai,,,daga ganin yadda sukeyin wasar suna cikin walwala da farin ciki. Sun jima sosai suna wasa can dai suna batun tashi gidajensu,,,,saiga Iya Gwamma tazo wucewa zuwa gidanta. Ta zo zata wuce ne sai kuma ta dawo baya wurinsu Maryam,,, suna ganinta suka durk'usa su uku suna cewa "Iya ina kwana,, ya gida?.Lafiya k'alau 'yan uku masu kamada juna,, kuma 'yan matan gobe mi kukeyi anan ne? ".

Suka had'a baki wurin cewa "wasa mukeyi Iya Gwamma,, mi zamuyi miki Iyarmune ko wani abu kikeso mu siyo miki ne?".Iya Gwamma ta tsura musu idanu na wani lokaci tana kallonsu,, irin kallon na k'urilla da bai dace ba. Baki da hanci ta saki tana musu kallon kwad'ayi,,, da k'urilla nason cimma wani buri nata. Can dai da k'yar ta daure ta b'oye damuwarta da kwad'ayinta,,tace "muje gidana in baku kud'i ku siyomin biredi da madara shagon Mande ".

Fadila tayi saurin cewa "to Iya su Fatima ku tashi muje gidan Iya mu amshi kud'i,, mu siyo mata biredi da madara ".Maryam da Fatima jikinsu duk yayi mugun sanyi tsoro da fargaba ya bayyana a cikin zuk'atansu,, su kansu basu so zuwa ba amma babu yadda suka iya. Kamar suce basu zuwa ba amma ba zasu iya kallon tsabar idon Iya Gwamma ba,, suce ba zasu iya ba saboda ko banza tayi jikoki dasu. Can dai Fatima ta tattaro dauriya tace "to Fadila, Maryam tashi muje mana kinyi shiru lafiya dai? ".Maryam itama ta mik'e tsaye tace "Lafiya k'alau Fatima ".Tana kakkab'e jikinta da yayi k'asa saboda wasa,, su ma su Fatima suka kakkab'e jikinsu,, Iya Gwamma ta dubesu tace "ku wuce muje zuwa gidan na gaji da tsayuwa ".

Suka ce "to Iya ".Iya Gwamma ta sasu agaba suna tafiya,, ita kuma ta tsaya abayansu tana k'are musu kallon k'urilla tasa lasar baki da fitar da halshe,,, su Maryam suna tafiya suna fira

cikeda matuk'ar jin tsoro da fargaba akan abinda kan iya faruwa dasu. Saboda maganar gaskiya da sunsan Iya Gwamma ce zata biyo ta inda suke,,, da tuni sun cikama bujensu ko zanensu iska. Domin Iya Gwamma ta shahara wurin maita da kuma sata a cikin unguwarsu,,, babu wanda baisan da zamanta ba sannan babu inda sunanta baije ba akan ita *MAYYA CE*.

*********************

*****Acan gidansu Maryam kuwa Mama Sa'ima ce zaune da yayan Maryam mai suna Mubarak,,,, suna firarsu ta tsakanin uwa da d'a. Yaya Mubarak ne ya dubi Mama Sa'ima yace "Mama tun d'azu muna fira banga giftawar yarinyar nan Maryam ba,, wai ina taje ne kuma? ".

"Hmmm Mubarak sun fita tun d'azu itada su Fatima,, gashi yanxu har azahar tayi basu dawo ba ".Inji Mama Sa'ima fuskarta tana bayyanar da damuwa.

Saida gaban Mubarak ya buga da k'arfi,, ya bada rasssss! Sannan ya tattaro natsuwarsa wuri d'aya,,, domin kada ya tashi hankalin mahaifiyarsa. Ya dubeta duba na natsuwa ya tausasa halshensa,, yace "Mama ki kwantar da hankalinki Insha Allahu suna waje suna wasa,,, kuma yanzu nan zanje ince su dawo gida hakanan. Ai wasan ya isa yau sai kuma gobe ".

"Da kako k'yauta Mubarak kayi sauri kaje kace ta dawo gida hakanan,,, saboda ina tsoron kada Alhaji ya dawo bai sameta gida ba. Nasan ni zai azama fad'a ni kuma ban aiketa ba wurin yin wasan banza ba ".Cewar Mama Sa'ima cikeda damuwa da tsoro..

Mubarak ya dubi uwar yace "ki daina damuwa Mama yanzu nan zan turo k'eyarsu,, insha Allahu Alhaji ma bazai san ta fita ba ".

Uwar tace "to Allah yasa tun can ka fara dukan shegiya domin Maryam agaskiya batajin magana,, kullum ina gaya mata idan ta fita wasa ta daina kaiwa azahar bata dawo gida ba. Amma tayi kunnen uwar shaggu da maganata saboda tana son babanku ya sani gaba ya cimin mutunci,,, wallahi yau kam sai jikinta ya gaya mata zata yabama aya zak'inta ".Ta fad'a cike da jin haushin Maryam.

Mubarak ya mik'e tsaye sannan ya dubi mahaifiyarsa,, cikeda lallashi yace "kiyi hak'uri Mama Maryam bazata koma dad'ewa awaje ba,,, yanzu zanje in korosu su dawo gida wlh amma dan Allah kada ki duketa Mamanmu ".

"Naji bazan duketa ba ,,, saboda kai ka haifarmin 'yar ko Mubarak ".Inji Mama Sa'ima cikeda sababi da masifa.

Mubarak ya sassauta murya yace "ba haka bane Mamanmu,, ganin nayi bugu baya magani sai dai addu'a da nasiha Allah ubangiji ya shirya mana zuri'armu. Kuma ya huci zuciyarki yake mahaifiyata,, kiyita hak'uri damu wata rana sai labari ".

Jikin Mama Sa'ima yayi matuk'ar sanyi akan maganar Mubarak,,hak'ik'a tasan duk abinda ya fad'a gaskiya ne babu k'arya acikin maganarsa. Kuma tasan Mubarak yaro ne mai natsuwa da iya kalamai masu dad'i da kwantar da hankali ga mai sauraronsa,, sannan yanada kaifin tunani da hangen nesa,, Mama Sa'ima ta numfasa tace "na hak'ura Mubarak Allah ubangiji yayi muku albarka,,, sannan ya shirya mini ku shirin addinin musulunci ".

"Amin Mamanmu,, toni zan wuce yanzu ".Cewar Mubarak.

Maman tace "Allah ya kiyaye hanya Mubarak yasa kayi saurin ganosu ".

Mubarak yace "Amin ".

Yaja k'ofar gidan ya bud'e tareda da fita,,, domin ya koro su Maryam su dawo gida hakanan..

*********************

Su Maryam suna tafiya suna fira har sukazo bakin k'ofar gidan Iya Gwamma,,, sukaja suka tsaya suna jiran harta iso dayake sun fi ta saurin yin tafiya kunsan abu da tsohuwa. Suka zauna suna hutawa can saiga Iya Gwamma ta iso tasa makulli ta bud'e musu k'ofar gidan,,, ta umurcesu dasu shiga cikin gidan dayake yara ne sosai babu wanda yasan ciwon kansa. Suka kutsa kai zuwa cikin gidan tareda Iya Gwamma,, suna shiga babu kowa cikin gidan sai komattsai da raggad'ud'an Iya Gwamma. Babu abinda ke tashi cikin gidan sai k'amshi soyen nama da k'arnin jini,,, dayake su Maryam yara ne babu abinda suka fahimta gameda Iya Gwamma .

Iya Gwamma ta tura ganbun d'akinta ta shiga cikin d'akin,,, ta d'an jima sosai sannan ta fito da kud'i ga hannunta d'ari uku da hamshin. Taba Fatima kud'in tana shafar hannun Fatima da wayo da wayo,,, tace "gashi ku siyomin biredi na d'ari da hamshin madara ta naira d'ari,,, inada sugar da bonbita naira d'arin da ya rage ku d'auka na baku "..

Fatima tace "mun gode Iya amma da kinbar kud'inki,,, ki k'ara ki sayi wani abu ".

Iya Gwamma tazo wurin kan Maryam tana shafa cikin dabararsu ta mayyu,, tace "Ayya 'yar nan k'yautace na baku kuma ba'a maida hannun k'yauta baya ".

"dallah rufe mana baki! Munce kibar kud'inki amma kinzo kinata damunmu da surutunki na banza,, bamu son kud'inki ko ana amsar k'yauta dole ne "Inji Fadila cikeda fitsara da tsiwa.

Iya Gwamma ta dubeta cike da tsananin mamakin rashin tsoronta,, ta bugi Fadila da wasa tace "amma yarinyar nan bakida kunya,, kinsan koni wa cece nayi fa jikanya dake yarinya".

Fadila itama ta dunk'ule hannunta cikeda rashin kunya,,, tayima Iya Gwamma mugun bugu a bayanta. Saida Iya Gwamma ta zabura da k'arfi! Tana mamakin k'arfin hali da rashin tsoro irin na Fadila. Fadila ta harari Iya tace "ina ruwana da kin yi jikanya dani tsohuwa,,, sannan sanin koke wa cece bayada wani amfani gareni! ".Tana murgud'a bakinta.

Hak'ik'a Fatima da Maryam sunyi matuk'ar jin tsoro da firgita! Akan abinda Fadila tayima Iya Gwamma,,, babu abinda jikinsu keyi sai makarkatar tsoro da fargaba. Can dai cikeda masifar tsoro suka had'a baki wurin cewa "dan Allah Iya kiyi hak'uri wallahi haka Fadila take da tsiwa ".

Iya Gwamma idanunta sukayi jawur saboda b'acin rai zuciyarta sai tafasa takeyi akan bak'in ciki,,, jijiyoyin kanta sukayi rud'u rud'u akan b'acin rai. Can tayi ajiyar zuciya na bak'in ciki ta daure tace "babu komai yaran nan amma ta sani taci alfarmarku,,, da wallahi bazata sake yima wani rashin kunya ba,,,amma ta je duniya ce zata ga abinda zai biyo baya! "".

"Mtsss aikin banza! Babu abinda zan gani sai alkhairin Allah,, kurwata kur! Kici kanki kisha bak'in ruwa ".Cewar Fadila tana tofar da yawu,, cikeda masifa da bala'i. Su Maryam ne sukaja hannunta da k'arfi suna bata hak'uri,, suka nufi hanyar zuwa shagon Mande suna tafiya Fadila tana ta masifa da bala'i,,, haka suka kama bata baki suna lallashinta. Suna isa shagon Mande dole tayi shiru suka siye abinda ya kaisu sannan suka juyo zuwa gidan Iya Gwamma.

Suna dawowa suka ba Iya Gwamma aikenta,, sannan su Fatima suka k'ara bata hak'uri akan abinda ya faru. Ta nuna musu babu komai ai tareda yi musu godiya sosai. Sannan sukayi juyawarsu zuwa gidajensu. Bayan fitarsu ne Iya Gwamma ta k'yalk'yale da dariyar mugunta harda fad'uwa k'asa akan makirci,, can tace '"hak'ik'a Fadila kin kawo kanki gidan mutuwa! Sai kinsan kinyi mini rashin kunya. Ko 'yan uwanki da basuyi min komai ba,,, bazan tab'a k'yalesuba balantana ke mara mutunci,, zakiyi nadamar abinda kika yimin a rayuwarki! "Hhhhhhhh haka dai Iya Gwamma ta cigaba da surutunta na son ganin bayansu Maryam..........

_More comment more typing_

_Mugirat Musa_😍
,
[6/21, 9:53 PM] Mugiratmusa66: 🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥
*MAYYA CE*
🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥

*INTELLIGENT WRITER'S ASSOCIATION ®*✍🏻
_[Onward together]_

*Written by Mugirat Musa*

*DEDICATED TO SIS NAJER'ART*

_Bismillahir rahamanir rahim_

*PAGE 2*

***Iya Gwamma ce ta kama surutunta na hauka,, mai cikeda bak'in ciki da b'acin rai akan abinda Fadila tayi mata. Can naga Iya Gwamma ta shiga cikin wani d'akin da yake gefen d'akinta da take barci da saka kayayyakinta,, tana shiga ciki ta fito da wata k'warya cikeda jinin mutane. Ta samu wuri saman tabarma ta zauna tanata sambatu da maganganu irin na masu sihiri da tsafi,,, ta jima tanayi saiga rugugin tsawa da hayak'i! Suna bayyana ruwan jinin dake cikin k'warya suna chanza kala daga ja zuwa kore-kore. Nan da nan naga ruwan jini sun fara tururin tafasa,, kamar an azashi saman wuta. Nayi duba zuwa ga idanun Iya Gwamma sunyi jawur kamar barkono,, ga jijiyoyin kanta sun mik'e tsaye rud'u rud'u halittar jikinta gaba d'aya ta chanza,, ko'ina a cikin jikinta gashi ya k'ara tsawo zago -zago kamar k'aho,,, bakinta babu abinda ke fitowa sai wuta mai mugun zafi. Can naga tayi wasu d'alamisai na tsafi saiga photonsu Maryam su uku ya bayyana a cikin k'warya,, suna tafiya zuwa gidajensu. Iya Gwamma tayi duba cikin k'waryar jini da idanunta jawur kamar kan jaki,,, tace" saina kasheku! Saina cinye namanku d'anye yara! Zan nuna muku ba'a yima mayyu rashin kunya akwana lafiya,,, hhhhh na kama kurwarsu ni Gwamma jikar mayya d'iyar *MAYYA* .Saina banbance muku atsakanin aya da tsakuwa,,, k'ananan marasa kunya kawai daku! ".

Haka dai ta cigaba dayin sambatunta,, tana tofe -tofe a cikin k'warya. Saiga inwar kurwarsu Fadila ta bayyana a cikin k'warya,, Iya Gwamma ta k'yalk'yale da dariyar muguntа da kuma farin ciki mara misaltuwa na cikar burinta....

*********************

Su Fadila suna tafiya suna firarsu cikeda walwala,, kamar babu abinda ya faru dasu agidan Iya Gwamma. Basu jima sosai ba suka had'u da yaya Mubarak,, bayan sun kawo wajen garkar

gidajensu. Yaya Mubarak ya dubesu cikeda matuk'ar mamaki yace "Yara manyan gobe ina kuka shiga ne,, tun d'azu nake zagayar gari nemanku ".

Maryam da Fatima suka sunkuyar da kansu cikeda fargabar da irin amsar da zasu bashi,,, tsoro da fargaba  ne ya bayyana k'arara akan fuskokinsu. Su biyu ne suka dubi Fadila domin sunsanta  wurin rashin tsoro da dauriya,, da iya tsara k'arya da gaskiya akan lamarin rayuwa. Fadila ce ta numfasa tareda k'yafta musu idanu akan su saki jikinsu,, kada yayi saurin gano abinda zata furta k'arya ne. Su Maryam suka gyad'a mata kai alamar to,, duk da yake babu abinda sukeyi sai wuru -wuru da idanunsu alamun rashin gaskiya duk ya bayyana a fuskokinsu.

Fadila ce tayi murmushi mai k'ayartar da fuskarta tace "yaya Mubarak wasa mukaje gidan k'awarmu Hassana,, shiyasa ne kayi nemanmu baka ganmu ba ".

Mubarak yayi shiru na minti biyu yana nazarin maganar Fadila,, amma acikin zuciyarsa ko kad'an bai aminta da maganarta ba. Domin kuwa kallon d'aya yayi musu ya gane basuda gaskiya,, amma dayake shi ma d'an zamani ne ya nisa sannan yace "Ok ba matsala amma dan Allah ku daina dad'ewa awaje,, wurin yin wasa domin kuwa yanzu zamanin nan namu ya lalace. Akwai abubuwa da yawa da zasu iya cutar daku wanda bana fatar haka,, saboda zuciyata bazata iya d'aukar hakan ba ".

Fatima taja dogon numfashi tace "insha Allahu yaya zamu kiyaye maganarka,, ai domin muje gidansu Hassana ne yasa muka dad'e sosai".

"haka ne gaskiya yaya Mubarak ai da tun d'azu mun dawo gida ".Cewar Maryam.

Mubarak yace "to 'yan k'annena na yarda daku nasan ba zakuyi abinda za'a ce Allah yayi wadaran da halinku ba,, saboda haka ku wuce zuwa gida ".

Fadila tace "zamu kiyaye yayanmu karka damu ".

"Allah yasa da gaske kukeyi ".Inji Mubarak.

"Amin Yayanmu ".Cewar Fatima da Maryam atare cikeda sanyin jiki. Yaya Mubarak saida ya raka Fatima da Fadila har bakin k'ofar gidansu,, dayake gidansu d'aya baban Fatima shine yayan baban Fadila. Bayan yah Mubarak yaga shigewarsu cikin gidansu,, yazo yaja hannun Maryam yana yimata nasiha tareda maganganu masu lurassuwa cikin hikima da iya magana..

*********************

Mubarak ne da Maryam suka shigo cikin gidan,, tareda da furta sallama a bakinsu. Mama Sa'ima ta amsa musu yayinda take k'ok'arin kwashe sharar da ta kammala yanzu nan,,, tasa parker ta kwashe sharar tana zubawa cikin kwandon shara. Alokacin ne Mubarak da Maryam suka k'araso cikin tsakar gida,, suka samu wuri suka zauna saman tabarma. Mubarak ya dubi Mama Sa'ima yace "sannu da aiki Mamanmu "."Yauwa Mubarak".Inji Mamansu bayan ta fito daga wurin kwandon zuba shara,, ta zauna kusaga Maryam ta harareta tace "sannu Maryam sarkin yawo,, Mubarak gidan uban wa kagansu? ".

Maryam ta sunkuyar da kanta cikeda matuk'ar tsoro da fargaba! Tace "Mama dan Allah kiyi hak'uri gidansu Hassana mukaje wasa ".

"tabbas haka suka gayamin Mama,,,tayi ba dai-dai ba ayi mata hak'uri bata sakewa ".Cewar Mubarak.

Mama Sa'ima tace "naji Mubarak amma wallahi Maryam ki kiyayeni ! Inba rainin wayo da hankali ba,,, ki fita daga cikin gidan nan tun safe baki dawo cikin gidan nan ba sai yanzu bayan azahar. Saboda bak'yajin maganata to zan gayama babanki nasan shi ,,,zakijin maganarsa saboda kinajin tsoronsa mara jin magana kawai ".

Maryam ta fara zubarda hawaye ,,,muryarta tana rawa tace "na tuba Mama ki rufamin asiri kada ki gayama baba,,,,wayyo wayyo Allah! Wayyo kaina wallahi Allah bana k'arawa komi kikace shi zanyi Mama. Yaya Mubarak ka taimaka ka k'ara bata hak'uri kaji ".

Yaya Mubarak ya dubeta cikin tausayawa da k'aunar k'anwarsa,,, yasa hannu ya jawota ya rungumeta a jikinsa yana lallashinta. Yace "ya isa ya isa Maryam share hawayenki Mama zata hak'ura kinji,, kuma idan Allah ya yarda bazan bari ta gayama Alhaji abinda ke faruwa ba ".

"To Yaya ".Cewar Maryam tana shessheka tana ajiyar zuciya,, saboda kukan da tayi.

"to tashi uwar son jiki kije kiyi wanka sannan kici abinci,,, nidake ne a cikin gidan nan matuk'ar kikace bazakiji maganata ba,,,,sai rayuwarki tayi matuk'ar b'aci sosai wawuya wadda bata san ciwon kanta ba"..Inji Mama Sa'ima cikeda matuk'ar b'acin rai sosai.

Maryam ta mik'e tsaye tayi hanyar zuwa d'aki domin tayi wanka,,, sannan taci abincinta..

Alokacin ne Mubarak ya k'ara cewa "Mama ayita hak'uri k'urciya ne wata rana zata daina,,, sannan nima zan k'ara saka mata idanu sosai ".

"hmmm haka ne Mubarak amma zamanin nan abin tsoro ne,,, ya zama dole mutum ya k'ara lura da d'iyansa. Saboda mayyu sunyi yawa a cikin mutane sosai kowa ka gani yaci magani ne domin yayi kud'i,, ko ya cimma wani buri nashi wurin bid'ar abin duniya sai mutum ya zama maye kowa ya kama gudunsa,,, kuma ba ko'ina ake amso maganin ba illa wurin bokaye da 'yan

bori. Mutane sun manta da cewa babu mai talautawa da azurtawa idan ba Allah kad'ai ba. Sun manta da cewa babu mai iya ba mutum abinda Allah bai bashi,,, da ace wani bawa yana iya azurtar da d'an uwansa da ya fara azurtar da kanshi kafin kuzo neman taimako wurinsa. Ba'aganshi walak'ance cikin k'azanta da datti ba ".Inji Mama Sa'ima.

Mubarak yace "haka ne gaskiya Mama Allah ubangiji ya bamu ikon bin gaskiya da kuma gyarawa,, wad'anda suka b'ace Allah ya daidaitasu akan hanyar gaskiya ".

Mama tace "Amin summa amin Mubarak ".

Suka cigaba da firarsu cike da tsananin jin dad'i da nishad'i sosai,, sunyi nisa cikin fira ne saiga sallamar Alhaji Suleiman ya shigo cikin gidan. Suka amsa masa  Mubarak ya gaidashi tare da yi mishi sannu da zuwa,,, ya amsa mishi fuskarshi cikeda fara'a da murna sosai. Mama Sa'ima itama tayi masa sannu da zuwa ya amsa mata,, ta amshi kayan da ke hannunsa suka shige cikin parlourn d'akinsu.

Mubarak ya jima sosai yana tunani akan al'amarin rayuwa,, sannan daga baya shima ya shige cikin d'akinsa. Ya shiga cikin toilet yayi wanka sannan ya sanya singlet da guntun wando domin shan iska,, ya kunna  vedio ya sanya American film ya fara kallonshi cikeda natsuwa da kwanciyar hankali....

*Ku biyoni sannu domin jin ko wa cece Iya Gwamma,,, da kuma jin tushen labarin*.

_Share&Comments_

~Muje zuwa~
[6/21, 9:53 PM] Mugiratmusa66: 🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥
*MAYYA CE*
🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥

*INTELLIGENT WRITER'S ASSOCIATION ®*✍🏻
_[Onward together]_

*Written by Mugirat Musa*

*DEDICATED TO SIS NAJER'ART*

_Bismillahir rahamanir rahim_

*PAGE 3*

**Yaya Mubarak yayi nisa sosai a cikin kallon American film d'in da yakeyi,, ko k'wakk'waran motsi bayayi sosai saboda yadda ya mayar da hankalinshi kacokam a wurin kallon vedio. Da gani babu tambaya kasan yanajin dad'in kallonshi,,, hankali kwance yake gudanar da komai

nashi..

Ab'angarensu Mama sa'ima kuwa suna shiga cikin d'akin,,, ta taya Alhaji cire kayan jikinsa. Bayan ta gama cire masa kayan tas ta barshi da singlet da guntun wando,, sannan ta ja hannunsa kamar yaro k'arami ta kaishi cikin toilet tareda had'a mishi ruwan wanka,, bayan ta gama duk abinda ya kamata ta fito ta bar Alhaji domin yayi wankansa. Tana fitowa ta k'ara gyare bedroom d'in tareda sa ma d'akin room freshner mai k'amshin dad'i matuk'a,,,, sannan ta fitoma Alhaji jalabiya fara da zai saka a cikin gida tareda da feshe jalabiyar da perform mai k'amshi,, sannan ta samu wuri ta zauna a cikin d'akin tana jiran fitowar uban 'ya'yanta..

Bayan minti goma sha biyar saiga Alhaji ya fito daga wanka,, yazo kusaga Mama Sa'ima. Tana ganinshi tayi murmushi sannan ta d'auko lotion mai k'amshi ta fara shafa  masasannu sannu cikeda nuna matuk'ar kulawa ga mijinta. Babu abinda Alhaji yakeyi sai lumshe idanu ma'ana yana jin dad'in yadda take bashi kulawa,, bayan ta kamalla shafa mishi mai  neta d'auko jalabiyarsa ta sa mishi,, tana gama sa mishi suka zauna a tare suna fuskantar junansu. Alhaji Suleiman ya dubeta duba mai cikeda k'auna da son matarsa yace "Ummu Maryam Allah ubangiji yayi miki albarka hak'ik'a ke mace ce ta gari mai biyayya ga mijinta,, ina alfahari da kasancewarki matata uwar 'ya'yana,,,nasan nayi dace da farin cikin rayuwata mai sona kuma mai son farin cikina,, da gudun b'acin raina banda tamkarki a cikin zuciyata ".

Alal hak'ik'a kalaman Alhaji Suleiman sunyi matuk'ar sanya Mama Sa'ima cikin tsananin nishad'i da farin ciki sosai,,, sunbi jini da jijiyoyin jikinta suna shawagi a cikin zuciyarta. Ta dubi Alhaji cikeda matuk'ar nishad'i sosai tace "Amin ya Alhajina kasani biyayya ya zama wajibi agareni nayi maka muddin ina numfashi a doron k'asa,,, kaine silar farin cikina hasken idaniyata,,, idan ban faranta maka ba waye zan farantawa aljannata tana k'ark'ashin tafin k'afarka fa mijina,,, idan ka d'aga k'afa in shiga idan ka take shikenan! Taya zanyi sakaci har na tab'e Abban Mubarak,, ina matuk'ar alfahari da kai Alhajina ".

Alhaji ya rik'o hannunta yana murmushin jin dad'i,, sannan yace "haka ne matata idan har miji

ke d'agama matarsa k'afa ta shiga aljanna,, to ni tawa k'afar a d'age take matata kuma insha Allahu zaki shigeta ".

"Ina godiya Alhajina,, to ya kasuwar? ina fatar ana samun ciniki sosai ".Inji Mama Sa'ima..

Alhaji Suleiman yace "lafiya k'alau Alhmdlilah,, agaskiya ana samu ciniki sosai ".

Mama Sa'ima tace "masha Allah komai yayi k'yau matuk'a,,, dama haka ake son ji Allah ubangiji ya k'ara taimakawa ya bada sa'a da nasara "..

Alhaji yace "Amin amin Ummu Maryam,, ina yaran nan suke ne Mubarak da Maryam d'in? ".

"hmm Mubarak yana d'akinsa Maryam kuma na barota ta gama cin abinci zata kwanta,,, kasan yaran idan suna gida kodayaushe suna cikin d'aki shiyasa ba'a sanin suna nan ko basa nan ".Cewar Mama Sa'ima..

Alhaji yace "haka ne musamman Mubarak akwai shi da son zama cikin d'aki kamar mace,,, shiyasa ma bai fiye son zaman shago ba,,, Maryam ko taso zaman d'aki ai ita mace ce gidan wani zataje ".

Mama Sa'ima tace "ai zai saba da zaman shago saboda namiji dole ya fita ya nemo,, Maryam kuma ai lamarinta sai addu'a saboda akwaita da rashin ji wallahi ".

Alhaji ya harareta da wasa cikin tsokana yace "a'aaa kada ki sanyama 'yata ido barta tayi rashin jinta,,, ai komai yanada lokacinsa addu'a dai zamu dinga yi akan Allah ubangiji ya shirya mana yaranmu "..

"kunfi kusa kodayake bakason a ce ga laifin Maryam,, addu'a takobin mumini ce Allah ya shirya mana zuri'armu ".Inji Mama Sa'ima.

Alhaji yace "Amin yanzu dai naji magana ba'a dinga takurawa 'yata ba,, ana cewa tayi kaza kaza ba "..

Mama tace "kaidai ka sani da dad'in bakinka ".

Yace "harda ke kinsan inada mana "..

Mama tace "nasan mi? ".

Alhaji yace "inada dad'in baki mana,, kuma har kin yaba ".

Mama tace "rashin aikin yi dai ".Tana murmushi sosai..

"da ni dake bamuda aiki yi ba ".Fad'ar Alhaji yana dariya sosai..

Mama kauda kanta tayi gefe guda,, tana ta dariya sosai mai cikeda matuk'ar farin ciki da walwala,, Alhaji shi ma yana tayata dariya tareda da jifanta da kallon soyayya da k'auna...

********************

***Agidansu Fatima kuwa suna isa cikin gidan sukayi sallama,, aka amsa musu suka samu uwayensu zaune wuri d'aya suna fira cikin farin ciki da nishad'i. Su Fatima suka samu wuri kusaga iyayensu saman tabarma suka zauna,, bayan sun zauna ne sukayi shiru basu ce komai ba saboda sunsan sunyi laifi...

Iyayen nasu sai firarsu sukeyi kamar basu gansu ba,, can dai Fatima da yake batada hak'urin yunwa ta bud'i baki da k'yar tace "Umma yunwa nakeji fa,, tun safe rabon dana koma saka wani abu cikin bakina ".

Mahaifiyar Fatima mai suna Nusaiba ta banka mata wata uwar harara,, sannan ta bud'i baki tace "to sabon salo inda kukaje ne baku ci abinci ba,, na aikeki yawon gantali da sakarci ne ? Da zaki zo kina damuna yunwa kikeji yau naga bak'ar munafuka,,, salon ubanki yaji yace ina miki horon yunwa ko,, Fatima Fatima! Ki fita daga cikin idona mai yawon sakarci da wawanci ".

Mama Nafisa mahaifiyar Fadila ta harari su Fadila,, tace "k'yaleta Nusaiba ai gara ita tayi magana,, wannan mai taurin kunne _(ta nuna Fadila)_ ko magana batayi ba saboda tasan batada gaskiya,,,gameda shegen yawon nan saina saka ki cikin turmi nayi miki dakan tankwan d'an bashirwa! Munafuka 'yar iskar yarinya ".

"Ni banga dalilin yawon banza ba miye kuka nema kuka rasa ne? Saboda Allah salon ku jawo

ma kanku wani mugun abu! Ga mayyu a garin nan kamar tsaki,,, saboda haka zamu d'auki mataki akanku tunda bakujin magana ".Inji Umma Nusaiba.

Mommy Nafisa tace "mataki ya wuce musa Fadil ya basu matsiyacin kashi idan suka koma,, saboda naga sun raina Nabila basajin tsoronta kwata kwata,,,ni wlh idan rayuwata ta b'aci ina iya yi muku mugun bugun walak'anci da halaka,, saboda naga lalama batayi muku musamman ke Fadila mai kunne roba ".

Umma Nusaiba tace "ba wani Fadila aiko ba ita kad'ai zakiyima fad'a ba,,, ko Fatima ba baya ba wurin rashin jin magana ba,,,mu samesu rana d'aya mu basu kashin k'warai ko zasuyi hankali "..

Mommy Nafisa tace "naji amma ai tafita rashin jin magana,, amma nasan maganinsu ".

"babu wani ta fi ta duk d'aya suke ".Inji Ummu Nusaiba.

Fatima ce ta tattaro dauriya,, tareda marairaice fuskarta tace "Mommy,, Umma dan girman Allah kuyi hak'uri Insha Allahu bazamu sake ba,, dama gidansu Hassana ne mukaje shiyasa muka jima sosai bamu dawo ba ".

"munsan munyi kuskure ayi mana afuwa,,, bazamu k'ara aikata  kwatankwacin haka ba ".Inji Fadila..

Mommy Nafisa taja mugun tsoki mtssss! Saboda ita akwaita da saurin d'aukar zafi da wuri,, ta juyar da kanta wani gefe domin kada suga fuskarta. Umma Nusaiba ce taja dogon numfashi tace "komai ya wuce yarana ubangiji Allah ya k'ara shiryaku,, Nafisa baki ce komai ba ".

Mommy Nafisa tace "ai kin riga kin gama magana Nusaiba,,, nima na hak'ura Allah ubangiji yayi musu albarka ".

Su Fadila sukace "amin mun gode sosai Iyayenmu ".Suka mik'e tsaye atare suka nufi cikin d'aki domin suyi wanka suci abincin rana,, iyayen mata suka cigaba da firarsu cike da walwala da annashuwa mara misaltuwa..

*ASALIN LABARI*

Maryam 'ya ce ga Alhaji Suleiman da Hajiya Sa'ima,, asalinsu 'yan nijar ne kasuwanci ne ya kawosu Nigeria acikin garin Gumi Zamfara state. Suleiman da Sa'ima 'yan uwan juna ne domin kuwa auren zumunci akayi,, sun taso ne tun suna yara suna matuk'ar k'aunar junansu fiye da yadda kuke tunani. Sun taso gidan mutunci masu nagarta da son zumunci,,,a familynsu sun kasance sunada had'in kai da kuma k'aunar juna babu gulma ko hassada da nuna k'yashi. Komai nasu a had'e yake abin burgewa da sha'awa matuk'a,, idan ka shiga cikin gidan da yake babban gida ne ba zaka iya gane wani banbamci ba,, saboda ba zaka iya gane wannan d'an wa ne ba ko d'an wance ce ba saboda had'in kai da zumunta,,, hak'ik'a famili ne mai matuk'ar k'aunar juna da yarda da 'yan uwa...

Sun had'a auren Suleiman da Sa'ima domin zumuncinsu ya k'ara k'arko,, masha Allah akayi dace ko su yara ne masu biyayya da k'aunar juna. Sun bada had'in kai cikin tafiyar da rayuwar aurensu cike da aminta da juna da zaman lafiya na hak'ik'a,, kowanensu yana k'ok'ari wurin ganin ya farantama d'an uwansa tareda k'yautatawa juna domin samun farin ciki da annashuwa mai d'orewa har abada ....

_Share &Comments_
[6/21, 9:53 PM] Mugiratmusa66: 🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥
*MAYYA CE*
🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥

*INTELLIGENT WRITER'S ASSOCIATION ®*✍🏻
_[Onward together]_

*Written by Mugirat Musa*

*DEDICATED TO SIS NAJER'ART*

_Bismillahir rahamanir rahim_

*PAGE 4*

Domin samun farin ciki da annashuwa mai d'orewa har abada,,, zamansu zama ne na fahimtar juna da amana,, tausayi da tsananin shak'uwa a tsakaninsu. Dukansu suna k'ok'ari wajen ganin sun sauke hak'k'in dake bisa kansu na aurratayya,, Suleiman ya kasance mutum ne mai sauk'in kai da tausayin na k'asa dashi bayada rowa ko k'yashi ko kad'an. Yanada son bayarda k'yauta da taimako gashi kuma mai tsananin biyayya da ladabi ga mahaifansa,, haka itama Sa'ima mace ce wadda batada matsala a rayuwarta,, tanada kirki da k'yakk'yawan d'abi'u tanada son

mutane da yawan fara'a. Haka take kowa nata ne babu ruwanta da shiga sabgar daba ta taba,,,, shiyasa lamarin aurensu yazo da sauk'i matuk'a saboda shi bayada matsala hakama Sa'ima batada wata matsala..

Haka suka cigaba da gudanar da rayuwar aurensu cike da jin dad'i da farin ciki mara misaltuwa,,, kowanensu yasan abinda ya dace ya kamata zaman lafiya ya wanzu a cikin gidan aurensu. Babu abinda sukeyi sai sunyi shawara tare su kashe tare su binne tare babu mai jin sirrinsu,, Alhaji Suleiman kasuwanci yakeyi tun anan nijar kafin harakar ta bunk'asa sosai .Itama Sa'ima tana saisuwa su kayan miya cikin gida irinsu,, maggi star racco,, daddawa,, maggi ajino motto,, gishiri,, kanwa,, sabulun wanka da wanki,, k'uli -k'uli,, tankwa da dai sauran kayayyakin miya..

Sunyi wata biyu da yin aurensu saiga ciki ya bayyana a jikin Sa'ima,, sunje asibiti an auna wata d'aya da satittikka zo kuga murna da farin ciki a fuskokin wad'annan bayin Allah. Bayan sunje gida suka sanarda 'yan uwa da abokan arzik'i duk wanda suka fad'ama sai yayi murna da farin ciki sosai,,, zo kuga farin ciki da nishad'i a cikin zuciyar iyayensu Alhaji Suleiman. Haka dai Sa'ima ta cigaba da samun kulawa ta musamman ta b'angare biyu iyayenta dana mijinta,, duk abinda take so shi akeyi mata na daga abubuwan ci da abinci mai gina garkuwar jiki,, haka abubuwan ke tafiya cikeda matuk'ar kulawa da tarairaiyarta. Shima kanshi uban gayya wata kulawa ya k'ara bata yana shagwab'ata da tarairaiyarta hundred percent,,, haka dai Sa'ima ta cigaba da rainon cikinta da bashi kulawa fiye da tunanin mai karatu,,, kwanaki suka cigaba da tafiya suna zama watanni..

Watanni takwas sukazo alokacin ne bayan sallar asuba,, ciwon nak'uda ya kama Sa'ima tun tana nishi hmhmhmhm hmhmhmhm hmhmhmhm babu wanda yaji,, har tazo ta fara kiran sunan mahaifiyar Suleiman. Inna ta shek'o da gudu ta taimaka mata tana mata addu'a harta santalo santalelen d'anta,, k'yakk'yawa son kowa k'in wanda ya rasa. Bayan Innar Suleiman ta gyarata ta kuma gyara ko'ina sai k'amshi yake tashi ,, can ta shiga cikin gida ta sanarwa kowa da kowa. Zo kuga yadda ake tururuwa zuwa ganin sabon jariri sabon jini,, haka dai mutanen unguwa suka cigaba da zuwa ganin jariri tareda yi mata barka da haihuwa,,, haka dai suka cigaba da zuwa dubiyar Sa'ima...

Sati yana zagayowa ranar suna yaro yaci suna Mubarak,, hak'ik'a 'yan uwa da abokan arzik'i sunyi matuk'ar k'ok'ari wurin ganin sun fitar da Sa'ima kunya,, anyi mata abin arzik'i k'warai da wadata raguna biyu manya -manya aka yanka da tinkiya d'aya. Haka dai akayi bikin cikin rufin asiri da wadatar zuci,, bayan maraice tayi kowa ya kama gabansa ya wuce zuwa gida..

********************

Bayan shekaru biyar da haihuwar Mubarak,, Alhaji Suleiman ya kwaso iyalinsa daga mahaifarsa nijar ya dawo Nigeria zamfara state cikin garin Gumi. Ya cigaba da kasuwancinsa cikeda kwanciyar hankali,, itama matarsa ya bata jari domin ta cigaba da sana'arta da takeyi acan nijar..

Garin Gumi gari ne mai tarihi da d'umbin albarka,, sunayin kasuwanci da kiwo amma ba sosai ba babbar sana'arsu shine noman k'warya. Itace sana'ar da mafi akasari da 'yan garin keyi da kiwo amma ba sosai ba,, garin ba za'a kirashi k'auye sosai ba kuma ba za'a kirashi birni ba yana dai tsaka tsakiya. Mutanen garin mutane ne masu addini da tsoron Allah,, komai nasu zad sha'awa suke gudanar dashi...

**Anan garin ne Mama Sa'ima ta haifi Maryam atsakaninsu da Mubarak akwai tazarar shekaru shida,,, zo kuga murna alokacin da Mubarak yaga ya samu k'anwa fara tass k'yakk'yawar gaske ta bugawa a mujalla,,, hak'ik'a Allah yayi halitta a nan domin kuwa kallo d'aya zakayima jaririya ka gano sai anyi k'yakk'yawar mace abar kwatance da kallo cikin mutane. Haka dai Mama Sa'ima ta cigaba da rainon Maryam itada Mubarak,, shima Alhaji Suleiman Allah ya d'ora masa tsananin k'aunar iyalinsa wato yaranshi,, komai yi musu yakeyi gwargwadon iyawarsa domin samun farin cikinsu da walwalarsu....

Fatima 'ya ce ga Malam Nura da Nusaiba,, kuma yaya ne ga Nazifi mahaifin Fadila da mahaifiyarta Nafisa. Nura da Nazifi sun kasance 'yan uwan juna uwarsu d'aya ubansu d'aya,,, sun kasance 'yan asalin jahar kebbi amma sun dad'e cikin garin Gumi sosai tun kafin su fara tara iyali sosai,,, babbar sana'ar da suka dogara da ita shine noman k'warya da ita suke ci suna rufama junansu asiri. Ahaka suke d'aukar nauyin iyalinsu cikeda zafin nema da wadatar zuci,,, shiyasa ake son mutum mai zuciyar neman na kanshi domin kada mutum ya dogara ga wani. Zuri'arsu zuri'a ce mai had'in kai da zumunta,, tareda da matuk'ar kulawa da kuma soyayya da juna. Kan mazan a had'e yake babu wani munafurci ko gulma,,, hakama matansu sunada had'in kai matuk'a d'aya batayin abu saida shawarwarin junansu. Duk abinda suka yanke shawara shi sukeyi tare shiyasa ko yaransu Fatima,, Fadila,, Nabila da Fadil kansu yake a had'e cikeda matuk'ar tausayin juna da girmamawa..

Familinsu family ne masu matuk'ar k'aunar juna,, da fahimtar juna haka suke tafiyar da rayuwar aurensu cikeda zaman lafiya da soyayya..

***Iya Gwamma 'yar asalin Gumi ce gaba da baya,,, 'ya ce ga Malam Mamman da Ina Talatu tanada k'ane guda mai suna Lawwali ita Iya Gwamma. Inna Talatu mayya ce da taci magani a wurin wani babban boka mai suna LOK'ORO,, boka LOK'ORO shahararren boka ne da ya shahara a cikin garin Gumi da kewayenta. Sunanshi ya bazama ko'ina a jahar zamfara da k'auyukanta ,,,yana bada magani ne ga wad'anda suke son suyi kud'i sosai ko wani cimma burinsu na duniya. Babban matsafi ne dake aiki da bak'ak'en aljannu da dodonni,, ya shahara wurin mugunta da kashe rayuka na mutane harda aljannu. Bayan Inna Talatu ta amshi magani domin ta zamo mai arzik'i to kwatsam! Bata zamo mai kud'i ba ta rikid'a ta zama k'usurgumar MAYYA wadda nan da nan ta fara cin naman mutanen unguwa da na k'etaren gari,,, tun tanayi a b'oye mutane basu sani ba har yazo ya bayyana afili kowa ya gano ita mayya ce. Nan da nan mutanen gari da wad'anda take mu'amala dasu suka fara gudunta domin ceton ransu dana iyalinsu,,,ko'ina ka gani anyi gungu a majalisu babu abinda suke fad'a idan ba Inna Talatu *MAYYA CE* cin naman mutane takeyi da satar kurwa! Harda yaranta su Gwamma ake tarewa a hanya ake ce musu d'iyan mayya kunyi hasara,, Gwamma kuwa kashi takeyima yaran mutane idan ko warinta ne saisu kacame da dambe sosai. Ta samu yaro tayi masa mugun cizo sai jini ya fito tasa halshenta ta lashe jinin ta had'iye mak'wat kamar mayya ,,,tabar yaron nan kwance k'asa yana kukan ciwo wiwiwihhh.

Lawwali yana gefe guda yana kallon yadda take dukan yaron mutane kamar ta samu jaki,,, shi

dai babu ruwanshi saboda yanada matuk'ar natsuwa da sanyin hali. Bayason hayaniya ko tashin hankali ko kad'an idan ka ganshi kana cewa ba Inna Talatu ce ta haifeshi ba,,, saboda natsuwarsa da hankalinsa..

Gwamma ce take kakkab'e jikinta da k'asa bayan ta gama chasa d'an mutane,,, ta juyo ta dubi Lawwali tana harararshi tace "shege raggon namiji kanajin ana zagin mahaifiyarmu amma kayi shiru,, sai dai ka koma gefe kana kallona ina fad'a,,, Allah yayi wadaran naka ya lalace! Wawan banza mai zuciyar kare ".

"yaya Gwamma kiyi hak'uri ni banyi shiru ba ne domin in b'ata miki rai ba,, nayi shiru ne saboda aganina fad'a baya kawo maslaha a cikin wannan lamari,,, kuma ai duk abinda suka fad'a ai gaskiya ne saboda Innarmu ta aikata maita! ".Inji Lawwali cikeda rashin son tashin hankali.

Gwamma ta zaburo mai da k'arfi cikeda jin haushin maganarsa,,, tace "Innarmu ce mayya saboda bakada hankali,, lallai Lawwali anyi tsinannen yaro d'an banza! Yanzu nan zanci ubanka ".

"Eh mana na fad'a ai gaskiya d'aci gareta k'arya kuma tanada matuk'ar dad'in d'and'ano mai zak'i yaya Gwamma ".Cewar Lawwali cikin jin haushin maganar Gwamma.

Nan da nan cikeda matuk'ar zafin nama da jin bak'in cikin maganar Lawwali,,, aiko Gwamma bata tsaya b'ata lokaci ba ta kwashe Lawwali da wani mugun mari mai matuk'ar zafi da rad'ad'i tareda gigita rayuwar d'an Adam! Ai saboda k'arfin marin saida Lawwali ya wintsilo k'asa da k'arfi,,, saida bakinshi ya fashe da jini jinshi da ganinshi suka d'auke na wucin gadi..

Yana kwance k'asa Gwamma ta nuna shi da yatsa cikeda zafin rai da tafasar zuciya tace "ina yi maka gargad'i da kada ka kuskura ka k'ara aibata mahaifiyarmu,,, idan ana zaginta kana kallo kana k'yalewa toni bazan k'yale ba,,, duk wanda ya nemi da ya zagi uwata to sai inda k'arfina ya k'are ciki kuwa harda kai da muke ciki d'aya,, wallahi wallahi! Akan mahaifiyata zan iya kashe rai har lahira!!! Kuma duk wanda ya shiga cikin gonata saina afka mishi koda kuwa kaine Lawwali,, yaron banza mara kishin uwarsa ".

Nan taja jikinta tabar Lawwali kwance a k'asa yana kukan rad'ad'in marin da tayi masa mai zafi sosai,,, ta kama hanyar zuwa gidansu babu abinda Lawwali keyi sai zubar da hawayen bak'in ciki da takaicin abinda Gwamma tayi masa,, kuma yasan ya fita gaskiya a cikin wannan lamari yasa hannu ya share jinin dake fita daga cikin bakinsa yana shassheka da ajiyar zuciya.....

_Share&Comments_

*I luv you my fans more more*
[6/21, 9:53 PM] Mugiratmusa66: 🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥
*MAYYA CE*
🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥

*INTELLIGENT WRITER'S ASSOCIATION ®*✍🏻
_[Onward together]_

*Written by Mugirat Musa*

*DEDICATED TO SIS NAJER'ART*

_Bismillahir rahamanir rahim_

*PAGE 5*

Yasa hannu ya share jinin dake fita daga bakinsa yana shassheka da ajiyar zuciya,, idan banda rad'ad'i da ciwo babu abinda zuciyarsa keyi saboda marin ya shigeshi sosai matuk'a. Dak'yar Lawwali ya mik'e tsaye yana shafa kuncinsa da yake yi masa zafi da rad'ad'i,,, ya kakkab'e jikinsa daya b'aci da k'asa ga shatin hannun Gwamma nan ya fito b'aro b'aro a fuskarsa,,, haka dai yaja k'afafunsa yana tafiya dak'yar domin ya nufi gidansu...

Gwamma ce naga harta iso gidansu ta afka cikin gidan ba tare da sallama ba,, Inna Talatu ce da Malam Mamman ta iske ya dawo gida domin yayi wani mantuwa a gidan,,, ya dubi Inna Talatu yace "Talatu baki ga wata bak'ar leda ba dana yi mantuwa da ita ba,, ta mutane ce idan kin gani ki mik'omin sauri nakeyi zan wuce ".Inna Talatu ta harari Malam Mamman sannan ta buga tsoki mtsssss tace "maganar banza kenan Mamman mi zanyi da bak'ar ledarka idan na gani,, ko kuwa ni na sakaka yin mantuwa ne? Da har zaka zo kana damuna da surutunka na banza da yofi! "."Kinga Talatu ba haka ba ne ai tambaya baya zama laifi,, daga tambaya sai masifa wai miyasa rayuwarki yanzu ta chanza ne? Idan wani abu nayi miki ya kamata ki sanar dani in gyara kuskurena mu fahimci juna,, batare da wasu sun jimu ba ".Inji Malam Mamman cikeda lalama,,, yana dibe dibe ko zai gano inda ya ajiye ledarsa da ya manta,,, Inna Talatu ta k'ara hasala sosai tace "babu abinda ka yimin Mamman tambaya ce kawai bana so,, domin ni tambaya b'atamin rai takeyi da ka shigo cikin gidan nan ya kamata ka bani ajiyar ledar,, amma baka bani ba ka ajiye da kanka sai yanzu da baka gani ba kake neman takuramin da tambayar munafurci,, to ka diba inda ka ajiye kada ka dameni da tambayarka "."Allah ubangiji ya huci

zuciyarki Talatu nasan nayi ba dai -dai ba amma kiyi hak'uri kinji ".Cewar Malam Mamman bayan ya shige cikin d'akin yana cigaba da bincikensa..

"da hak'uri ta mutu sadakar nawa ka bani tsohon banza bak'in munafiki! ".Cewar Inna Talatu cikeda bala'i da masifa.

Tun d'azu Gwamma tana tsaye babu abinda tace,, illa kallonsu da takeyi uwarta tana zagin ubanta. Sai alokacin ne Gwamma ta bud'i baki tace "Inna na dawo fa naga tun d'azu baki lura dani ba,, kinata surutunki ".

"To d'iyar k'warai sannu da zuwa ya gajiyar hanya,, ina kika baro k'anenki ne? ".Inna Talatu ta fad'a yayinda take dube dube ko zata hango Lawwali a bayan Gwamma..

Gwamma taja numfashi tace "lafiya k'alau na dawo Inna Lawwali kuwa na baroshi a bayana kan hanya ".Saiga Malam Mamman ya fito daga cikin d'aki rik'e da ledarshi a hannunsa,, alamar kenan yaga ledar ya dubi Gwamma da Inna Talatu yace "aaa Gwamma kin dawo ko ".

"Eh na dawo baba ".Cewar Gwamma.

Malam Mamman yace "to yayi k'yau Allah ubangiji yayi muku albarka ".

Tace "Amin baba ".

Malam Mamman yace "to ni Talatu zan wuce can kasuwa naga ledar da na tambaye ki,, kika yimin bak'ar magana wadda babu dad'in ji balantana saurare kamar ni ba mijinki ba ne ".

"to tunda ka gani ka isa barka kada ka gayamin maganar da batada dad'i,, inko rama wallahi domin ba tsoronka nakeji ba! ".Inji Inna Talatu MAYYA.

Malam Mamman yace "ai nasan bakijin tsoro na Allah ubangiji ya shiryeki Talatu! Rayuwarki tanada matsala sosai wlh,, ni inada aikin yi na barki lafiya masifaffar banza ".Yana fad'in wannan maganar yasa kai yayi tafiyarsa zuwa kasuwa,, batare da ya tsaya ya saurarin irin martanin da zata mayar mishi ba..

"kaine masifaffe ba ni ba ai wannan rainin wayo ne,,, daga kawai kaga ina maka shiru-shiru sai raini da walak'anci ya shigo,, wallahi bazan tab'a barin ka gayamin magana ba dad'i ba amma ba komai zanyi maganinka! ".Cewar Inna Talatu tana d'aga murya k'warai ta yadda wanda yake bakin garka,,, zai iya jiyo muryarta.

Sai asannan ne Gwamma ta iya bud'a baki tace "kiyi hak'uri Inna wannan abin bai kawo kallo ba,,, kuma bai dace ba kina d'aga murya sosai har na waje suna jinki ".

Inna Talatu tace "haka ne d'iyar albarka rayuwata ce ta b'aci sosai wlh,, shiyasa ki kaga inata fad'a amma yanzu tunda kinsa baki na daina fa,, mi ya faru ne naga kamar bakinki yanada

magana ?".

"ke dai bari Inna ayau Lawwali yayi masifar b'ata min rai da bani takaici ".Cewar Gwamma.

Inna Talatu tace "mi yayi miki ne har ya b'ata miki rai ne? ".

Gwamma ta kwashe labarin duk irin fad'an da takeyi da yaran mutane da suke kiran Inna Talatu mayya,,, da kuma marin da tayima Lawwali da kuma maganganun da sukayi,, babu abinda ta b'oyewa Inna Talatu komai ta gaya mata..

Inna Talatu taja dogon numfashi tareda huci mai zafi,, sannan tace "yanzu Lawwali ni yake zagi harda kirana da mayya,, yau ko wa yayi masa tsaye saina halakashi! Nayi masa mugun bugu sosai wlh,,, yadda idan yaji ana zagina ko baiyi fad'a ba bazai saka bakinsa ba waishi mara kuny....

Inna Talatu bata k'arasa maganar da take sonyi ba,, saiga sallamar Lawwali yayi sannan ya shigo cikin gidan da fasasshen bakinsa. Inna Talatu ta jawo hannunsa kamar abin arzik'i tana k'ara shafe masa jikinsa da jinin dake fita daga cikin bakinsa..

Sannan ta tambayeshi kamar batasan komai ba tace "Lawwali uban waye ya fasa maka baki harda jini,, wa ye ya mareka harda shatin yatsu? Ka gayamin yau ko ni ko maishi mutuwa kad'ai ke rabamu wlh ".

Lawwali yace yana zubar da hawayen takaici "Inna Yaya Gwamma ce ta mareni saida na fad'i k'asa,, sannan ta dinga zagina babu iyaka ".

"ita Gwamman to naji mi kayi mata ne data mareka? ".Inji Inna Talatu.

"haka kawai ne  banyi mata komai ba ".Cewar Lawwali.

Inna Talatu ta harzuk'a da hasala sosai,,, batayi wata wata ba ta kwashe Lawwali da matsiyacin mari biyu masu k'yau,,, ta ka mashi tana ta kashi kamar ta samu jaki. Babu abinda Lawwali keyi sai kuwwa yana kuka domin ya samu agaji cikin gaggawa,,, saboda ba k'aramin duka Inna Talatu takeyi masa cikeda matuk'ar takaicinsa da zafin rai tana cewa "da kai za'a had'a baki ana zagina ko ana cemin mayya baka damu ba,, saboda bakasan zafina ba amma 'yar uwarka da tasan zafina shi ne za kace mata ai gaskiya yaran suke fad'a domin na aikata maita! Yanzu saboda munafurci na tambayeka kace bakayi mata komai ba ,,,yau saina kasheka in kashe banza! ".Haka dai  Inna Talatu ta kama dukan Lawwali sosai tana zaginsa..

Babu abinda Lawwali keyi sai kukan bak'in ciki da zafin duka,, yana cewa "na tuba na tuba Inna,, Inna bazan sake ba wallahi sharrin shed'an ne ki ya femin zan mutu zan mutu! ".Nan ya fad'i k'asa ya some duk da haka bata daina dukansa ba,,, sai da tayi masa lilis da duka sannan daga baya ta gano cewa ya suma,, taje ta d'ebo ruwa a randa masu sanyi ta watsa mishi a jikinsa. Gwamma dai tana zaune tana kallon duk abinda ke faruwa hankalinta kwance,, can yaja dogon numfashi ya tashi zaune yana kuka duk gaba d'aya jikinsa yayi rud'u rud'u akan duka,,, Inna Talatu tace "gobe ma ka k'ara da sai naci namanka d'anye wlh! Kuma yau duk ubanda ya d'aure maka gindi ba za kaci abincin dare ba,, mu zuba mu gani ni da kai shege ya fasa! ".Tana gama fad'in maganganunta taja hannun Gwamma sukayi shigewarsu d'aki.

Lawwali yaja jikinsa sannu ya shige cikin d'akin da babu komai sai tarkacen kayayyakin aikin gida,, ya samu wata tsohuwar tabarma data yakuce akan tsufa ya kwanta. To haka abin ya kasance kuwa domin Inna Talatu hanama Lawwali tayi abincin dare da yunwa ya kwana,, mahaifinsa kuma baisan abinda yake faruwa ba a cikin gidan ba..

********************

Da misalin k'arfe 12:00am na dare ne Inna Talatu ta tashi sannu a hankali,, tana dubawa ko Malam Mamman da Gwamma sunyi nisa cikin barcinsu. Ai kuwa taci sa'a babu abinda sukeyi sai minshari da gurnani na barci,, ta lab'ab'a sannu a hankali ta fito waje tareda zare sakatar gidan..

Tana fitowa waje ne duk unguwar tsit ta ke kowa yayi barci babu abinda kakeji sai kukan tsuntsaye dana wasu halittu,, ga wata irin sansanyar iska da ta ke busowa mai dad'in gaske. Sai da Inna Talatu ta dubi yamma gabas,,, kudu da arewa sannan ta duba kowace hanya babu kowa,,, sannan naga ta kama wata hanya siririya wadda ta nufi cikin daji,, tana ta tafiya har ta kawo wurin wata bishiya nan da nan naga ta cire tufafinta ta koma zindir haihuwar uwarta. Tana cire tufafinta ta isa wani wuri inda babu abinda ke tashi sai wuta wal wal wal,, wai ashe wurin 'yan uwanta mayyu ta zo domin suyi bugun wuta..

Wasar bugun wuta shi ne abinda mayyu keyi da daddare musamman alokacin zafi,, zindir haihuwar uwarsu sukeyi tareda canza kamanninsu ,, suna taruwa a cikin daji suna wasar bugun wuta shi ne su kama zagayar dajin gari bakinsu da hammatarsu sai fitar da wuta sukeyi wal wal wal zad tsoro!,, zasu jima sosai sunayi sannan daga baya kowa ya kama gabansa.

Suna gamawa ne Inna Talatu taje wurin bushiyar da ta aje kayanta ta d'auka ta sanya ta nufi gidan mijinta,, tana cikin tafiya kawai gani nayi ta girgiza da k'arfi! Ta rikid'a ta koma karya mai k'wala k'walan ido da halshenta ya kai tsawon igiyar shanya,, bakinta sai feso wuta yakeyi jawur tana kukan karnuka ohww ohww ohww babu dad'in saurare da ji hayak'i bak'i kawai ke fita daga cikin jikin karyar.

Ta kusa kawowa gida ta had'u da Lado zaiyi fitsari,,, komai na kayan cikinsa tana gani kamar irinsu hanji,, hanta ,, zuciya da duk wani abu da ku ka san d'an Adam ya keda haka suke ganin komai na mu kamar yadda ku ka ga skeleton,,, ai kuwa babu b'ata lokaci tasa halshenta mai kamar igiya ta jawoshi sai da tayi sama da shi ta koma tayi k'asa dashi,, sannan ta bugashi a k'asa cikeda maita. Lado babu abinda yakeyi sai kuwwar neman agaji amma ina dare ne kuwwarka banza.

Babu wanda zai jishi balantana ya kawo masa agajin gaggawa,, haka kawai yaji kamar an tsinke mishi jijiyoyin jikinsa saida Inna Talatu tayi masa azaba da mugunta iri iri daban daban sannan tayi wani mugun sihiri,,, wata irin mahaukaciyar guguwa ta ga me wurin tana zagayesu na wani lokaci,, saiga wani farin abu mai surkin ja ya bayyana a tafin hannun Inna Talatu,,, yana bayyana ta karanta wasu d'alamisai na tsafi da sihiri abin ya zama fa ra ta tura cikin jakarta ashe kurwar Lado ce ta mayar fa ra ta nufi gida da saurinta.

Tana shiga cikin gidan ta girgiza ta sake rikid'a ta koma mutum,,, sannan ta lallab'a sannu a hankali ta kwanta domin kada wani daga cikin d'iyanta ko mijinta su ganta.....

_Share&Comments_
[6/21, 9:53 PM] Mugiratmusa66: 🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥
*MAYYA CE*
🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥

🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥

*INTELLIGENT WRITER'S ASSOCIATION ®*✍🏻
_[Onward together]_

*Written by Mugirat Musa*

*DEDICATED TO SIS NAJER'ART*

_Bismillahir rahamanir rahim_

*PAGE 6*

Tana shiga cikin gidan ta girgiza sannan ta rikid'a ta koma mutum wato ainahin siffarta,,sannan ta lallab'a sannu a hankali ta kwanta domin kada wani daga cikin d'iyanta ko mijinta ya ganta..

Washe gari tunda safe Inna Talatu ta tashi ta share gidan tsab,,, sannan ta aza tukunya saman murhu ta zuba ruwa ta barta nan wuta na ci bal bal bal harta dad'e saman wuta,, bayan ruwan sun tafasa ta d'auko gunba ta dama kunu,,, sannan ta d'auko kaskon suyar k'osai ta aza saman wuta tareda sanya mangyad'a a cikin kaskon. Nan da nan ta shiga cikin d'akin ta d'auko k'ullun k'osai ta fara suyar k'osai cikin natsuwa da kwanciyar hankali,, k'amshi sai tashi yakeyi yana game gidan baki d'aya,, haka dai Inna Talatu ta cigaba da aikinta tana wak'e wak'enta irin na mutanen da,, daga ganin yadda takeyin aikin tana cikin nishad'i da farin ciki sosai,, ta jima sosai tana suyar sannan ta kammala ta fissuwa kaskon saman wuta ta aje gefe,, tareda kashe wutar murhu..

Tana gamawa ta d'ebo ruwa a famfo ta shige toilet domin tayi wanka,, bata jima da shiga wanka ba saiga Malam Mamman ya fito daga cikin d'aki yana gugar bakinsa da asuwaki,, shi ma yaje famfo ya d'ebi ruwa a bokiti domin yayi wanka ya tsaya yana jiran fitowar Inna Talatu..

Ta jima sosai tana yin wanka sannan ta fito daga cikin toilet,, Malam Mamman ya dubeta yace "har kin fito daga wanka Talatu? ".

"Eh mana na fito har na gama had'a karin safe ".Inji Inna Talatu MAYYA.

Malam Mamman yace "to yayi k'yau gaskiya kinyi sauri sosai,, dan Allah kafin in fito ki tabbata kin had'amin komai nawa karin kumallo ".

Inna Talatu tace "to Mamman karka damu yanzu nan zan had'a maka komai ".

"na ko gode miki sosai ".Cewar Malam Mamman tareda shigewa cikin toilet,, domin ya tsabtace jikinsa yaje wurin sana'arsa..

Inna Talatu kuwa wucewa tayi cikin d'akinta tana shafa man shafi,, bayan ta gama komi ne ta sanya tufafinta masu dama dama ,,,sai alokacin ne Inna Talatu ta lura da bata tayar da Gwamma ba daga barci,, ta je ta tasheta daga barci sannan ta juya ta nufi hanyar d'akin da Lawwali yake kwance,, ta tayar dashi daga barci tana zaginsa saboda haushinshi da takeji

sosai ,,Lawwali ya tashi yana wuru wuru da idanu ya duk'ar da kanshi k'asa yana sauraren irin zagin da Inna Talatu ke masa akan rashin so..

Bayan ta gama zaginsa ta fito daga cikin d'akin tayi  cikin d'akinta,, ta iske har Gwamma ta gama karin kumallo,, shi ma Malam Mamman har yasha kunun da k'osai ya shirya yayi wurin neman na kansa,, Inna Talatu ta samu wuri ta zauna saman kujera ta fara cin k'osai tana shan kunu cikin natsuwa da nishad'i,, bayan ta kamalla cin abinci ne ta dubi Gwamma cikeda matuk'ar k'aunar d'iyarta tace "Gwamma babanku ya fita ne,,, ina fatar kin k'oshi sosai babu abinda kikeso? ".

Gwamma tace "Eh ya fita Inna kuma ni a k'oshe na ke,, babu abinda nake buk'ata ".

"babu damuwa d'iyar Inna ".Inji Inna Talatu.

Lawwali ne naga ya shiga cikin kitchen ya d'ebo kunu da k'osai cikeda fargaba da matuk'ar tsoron Innarsa,, zullumi da fargaba ne suka bayyana k'arara a saman fuskarsa,, duk abinda yakeyi Inna Talatu tana lura dashi sai dai bata ce dashi ci kanka ba yaja k'afafunsa ya yi cikin d'akin da ya kwanta barci..

Su kuma Inna Talatu da Gwamma suka cigaba da firarsu cike da tsananin k'aunar juna da wasa da dariya,, babu abinda suke yi sai shewarsu da kuma yin muguwar dariya ta yadda ko wanda yake waje zai iya jiyo dariyarsu da surutunsu..

Shi dai Lawwali yana nan lab'e cikin d'aki bayan ya gama cin abinci,, ya kwanta yayi shiru yana tunani can naga yana zubar da hawayen bak'in ciki da k'uncin rayuwa kamar marayan da bayada uwa ko uba,, ayadda na fahimta Inna Talatu ta tsaneshi bata sonshi hmmm wai kamar ba ita ta haifeshi da cikinta ba,, ko da yake ba abin mamaki ba ne sau da yawa iyaye su kan tsani 'ya'yansu akan *SON ZUCIYA* da hujjar banza..

*********************

Ab'angaren Lado kuwa kafin gari ya waye sosai ya farfad'o daga dogon suman da yayi,,,, ya tashi tsaye yana kakkab'e jikinsa Sannan ya nufi cikin gidansa,, ya shiga da sallama matarsa Hassi ta amsa mashi tareda yi masa sannu da zuwa,, domin ita azatonta daga masallaci ya fito tana surfen hatsi ta ga Lado ya nufi randar ruwa ya d'iba a cikin buta yana arwala,, bayan ya gama ne ya shiga cikin d'aki ya shimfid'a sallaya yana sallah..

Hassi ta daina surfen da takeyi tayi tsaye sakatoto kamar wawuya,, tana ta mamaki da al'ajabi akan mijinta,, tana ta addu'ar Allah yasa ba wani abu na cutarwa ba ya gigita mata miji ba ya fita cikin hayyacinsa..

Bayan Lado ya gama sallah ne ya fito waje wurin matarsa,, Hassi ta kalleshi cikeda matuk'ar tsoro da gigicewa tace "Lado lafiya naga ka sakeyin wata sallar asuba bayan wadda kayi a masallaci? ".

Lado ya d'ago jajayen idanunsa yaja wani dogon numfashi,, sannan yace mata "aike yau na auna arzik'i da tuni sai dai a kawo miki gawa ta na mutu,, sai dai kiyi takaba ki sake sabon aure Hassi ".

"Subahanillah!!! Ta ya hakan ya faru? Inji abin da sauk'i Lado ".Tace cikeda matuk'ar tashin hankali da zullumi..

Lado ya kwashe labarin komai gameda karyar daya had'u da ita,, da irin azabobin da aka gana masa da kuma sihirin da tsafin da ya gani karyar ta aikata,, babu abinda ya b'oye mata na dangance abinda ya faru.

Hassi ta buga k'irjinta da k'arfi! Tace "karya fa kace daga zuwa wurin yin fitsari ".

Yace "Eh mana karya ce na gani ".

Tace "Ina lillahi wa inna ilaihirraji'un!!! In dai har karya ka gani to babu shakka *MAYYA CE* ka had'u da ita Lado,, wayyo Allah Allah yasa kada ta cutar da kai na shiga uku na lalace ni Hassi! ".

Lado yace "mayya kuma ni ina ni ina mayya Hassi,, ki rabani da shirmenku na mata kunfi kowa shegen tsoro da koke koke ".

Hassi ta fashe da kuka mai cin rai tace "ba wani koke koke sai gaskiya,, mijina ka yarda da maganata wallahi *MAYYA CE* ta tare ka kan hanya ".Tana k'ara gunjin kuka sosai..

"ni kinga tafiyata idan kika daina kuka zuwa anjima zan dawo,, kinzo kinata cika ni da surutun banza mtsssss! ".Inji Lado yaja k'afafunsa yayi wucewarsa yana ji nini..

Ya bar Hassi zaune tana ta kukan damuwa da fargab akan yadda abin zai iya kasancewa,, saboda har cikin zuciyarta da jikinta ya bata abinda ya had'u dashi ba alkhairi ba ne.....

_Share &Comments_
[6/21, 9:53 PM] Mugiratmusa66: 🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥
*MAYYA CE*
🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥

*INTELLIGENT WRITER'S ASSOCIATION ®*✍🏻
_[Onward together]_

*Written by Mugirat Musa*

*DEDICATED TO SIS NAJER'ART*

_Bismillahir rahamanir rahim_

*PAGE 7*

***Saboda har cikin zuciyarta da jikinta ya bata abinda Lado ya had'u da shi ba alkhairi ba ne,, kuka kawai takeyi mai ban tausayi da tsuma zuciyar mai sauraro,, ta jima tana hawaye harta gaji da yin kuka sannan ta shige cikin d'akinta domin har kanta ya fara ciwo akan damuwa..

Lado kuwa yana fita bai zarce ko'ina ba sai cikin kasuwa rumfar da abokinsa yake zama,, yana zuwa yayi sallama Idi ya amsa masa sannan sukayi musabaha da juna,, Lado ya zauna saman benchi kusa ga Idi sannan yace "Abokina ya kasuwar? Ina fatar dai komai yana tafiya dai-dai ".

Idi yaja dogon numfashi yayi ajiyar zuciya yace "Alhmdlilah Lado komai dai-dai,, ina ka fito ne yanzu? ".

"gida na fito kai dai na baro Hassi can tanata koke koken banza,, ganin nayi ta dameni da kukan banza shiyasa na fito nabar mata gidan ".Inji Lado.

Idi yace "kai kuwa abokina baka k'yauta ba taya zaka baro iyalinka cikin damuwa,, baka tsaya ka saurari abinda ya sanyata kuka ba,, kai wa ne irin mutum ne kai Lado ".

Lado yace "ba haka ba ne Idi akan wata 'yar magana ce dana gaya mata,, maganar bata taka ka ra ta karya ba shi ne ta ke kuka ".

"to wannan wa ce irin magana ce da ta sanyata kuka nan da nan? ".Cewar Idi yana jimamin maganar..

Lado yace "yanzu kuwa zan baka labarin abinda ya faru dani jiya abokina ".Ya kwashe labarin komai abinda ya faru da shi,, da kuma irin abubuwan da karyar tayi masa na mugunta iri iri daban daban ya gaya  masa ..

Bayan ya gama gaya masa labarin sai Idi ya dubeshi cikin jimami da tausayawa,,, yace "Abokina hak'ik'a ka ga tashin hankali da bala'i a daren jiya,, ina rok'on Allah ubangiji ya tsayar nan yasa abin ba mai cutarwa ne ba,,, amma fa Hassi tana da gaskiyarta saboda mayyu suna iya komawa kowace irin halitta na dabbobi irinsu karya,, ma ge,, rago,, jaki da dai sauransu,,, saboda haka ka daina ganin laifinta ".

Lado yace "haka ne gaskiya amma duk abinda Allah ya tsara zai samu bawa ,,babu mahani sai ya same shi ni na yarda da k'addarata duk abinda ya sameni daga Allah ne ba daga wani ba ".

"tabbas maganarka haka ta ke Lado,,, Allah ubangiji ya tsare mu daga shairin mugayen mutane da aljannu,,, yasa kuma mu dace baki d'ayanmu ".Inji Idi cikin sanyin jiki da damuwa.

Lado yace "Amin abokina ".

Suka bar firar nan suka fad'a firar kasuwanci da kuma abubuwan da ke faruwa a cikin duniyarmu,,,, babu abinda ke tashi sai muryarsu da dariyarsu cikeda matuk'ar k'aunar juna da amintaka da junansu..

***** ***** ***** ***

***Washe gari da safe misalin k'arfe 11:00am na safe,, bayan Malam Mamman ya fita zuwa kasuwa wurin sana'arsa,,,, Inna Talatu ce ta aiki su Gwamma da Lawwali su sayo mata kayan miya kasuwa,,, daga nan zuwa kasuwa da k'afa akwai nisa sosai,,, bayan sun wuce ne Inna Talatu ta fissuwa fa rar da ta saka cikin jakarta jiya da dare,, tana cirowa ta je ta aje fa ra wurin tulun ruwa masu sanyi da ya ke gefen filin gidan,, tana aje fa ra (grasshopper) sai naga fa ru (grasshoppers )masu yawa sosai. Ta aje su kusan wuri guda ashe dai duk kurwar mutanen da Inna Talatu ta kama ne domin ta cinyesu,, ta samu wuri ta zauna tana ta sambatun sihiri da tsafi idanunta sunyi matuk'ar ja kamar garwashi,, gashin jikinta ya fito yayi zago zago kamar dodanniya,,, gashin kanta ya koma fari fat kamar tsohuwa..

Hak'oranta suka yi zago zago kamar gatari,, nan da nan naga ta d'aga hannunta sama tana ta tsafi ta jima tana yi sai naga anyi wata irin mahaukaciyar tsawa! Ta bayyana ratsatsatsa ratsatsatsa fasss fasss fasss !!!Gidan ya kama girgiza komai na gidan ya kama rawa da girgiza da sauri da sauri,,, wani bak'in hayak'i ne yazo wurin Inna Talatu yana ta zagayarta har tsawon minti talati,, sannan ya daina Inna Talatu tasa hannunta fartuna zagal zagal,,, ta yi amfani da wutar da ke fitowa daga cikin bakinta ta d'auko fa ru(grasshoppers) guda biyar tana gasa su da wutar bakinta ..

Kuwwa da kururuwa kawai kurwar sukeyi da k'arfi! Har ma kana jin kukan mutane sosai kawai ke tashi ya cika gidan gaba d'aya,,, hayak'i duk ya gauraye gidan!. Inna Talatu tana gamawa ta sa fa run cikin bakinta ta lak'umesu ba tare da b'ata lokaci ba,, har wani gurnani da nishi takeyi cikeda matuk'ar jin dad'in naman da ta keci na mutane,, tana gama ci ta nufi wurin murhun wuta sai naga wasu fa ru masu yawa ta ajesu nan..

Wai ashe mayyu idan suka kama kurwar mutune,, zasu mayar da ita fa ra ko kaza ko k'aton rago da dai sauran dabbobi iri iri daban daban da suke mayar da mutane..

Idan mayyu suka kama mutum suka mayarda kurwarshi fa ra ko kaza,, za suyi ma fa rar tsafi domin kada ta tashi ta je ko'ina ma'ana ta tsaya a inda anka ajiyeta,, sai mayyar ta ajeta wurin tulun ruwa masu sanyi sai kaga jikin wanda aka kama yanada matuk'ar sanyi sosai,, idan kuma aka aje fa rar wurin murhun wuta zaka samu jikin wanda mayya ta kama yayi zafi sosai kamar garwashin wuta. Wasu kuma suna aje kurwar saman gidan tururuwa,, shi kuma zai ji kamar ana sukar jikinsa da allura.

Wasu kuma kaza suke mayar da kurwar mutum su je su saisuwa,,, su samu kud'i to fa ana yanka kazar nan shikenan mutum zai mutu har lahira,, wasu kuma rago suke mayar da kurwar mutum su je can kasuwa su sai suwa musamman ga sallar layya,, xa'a ga mutane suna ta

mutuwa to akwai mutuwar Allah akwai wadda sanadiyyar mayya ta maida shi rago ta sai suwa idan aka yanka ragon sai mutum ya mutu,, batare da ansan *MAYYA CE* ta kamashi ta cinye ba..

Akwai abubuwa da dama da mayyu sukeyi fiye da wad'anda na ambata,, addu'a ce kawai mafita agaremu 'yan uwana musulmai,, amma maganar gaskiya mayyu sunyi yawa a k'asarmu ta hausa ba yaran ba,,,ba manya ba tsofaffi,, budare,, samari maza da mata kowa a cikin wannan zamanin zaka iya samunshi maye _(Allah ubangiji yayi mana mafita da kuma maganin abinda bamu iya yima kanmu )_..

Bayan Inna Talatu ta gama cin naman mutanen da ta kama,,, ta samu ruwa masu sanyi ta sha ta yi gatsa..

Sannan ta samu kujera k'arama ta zauna tana dama fura cikin roba,, sai wani gyad'a kai takeyi kamar ba ita ba ce ta gama cin naman mutane ba!.

Babu jimawa sai ga su Gwamma sun dawo daga inda ta aikesu,, suna isowa suka d'auko tabarma suka zauna tare da aje kayan miyan gefe cikin bak'ar leda.

Alokacin ne Gwamma ta dubi Inna Talatu MAYYA tace "Inna mun dawo ga aiken da ki kayi mana fa ".

Inna Talatu tace "na ga ne ku d'iyar albarka,, Allah dai yayi muku albarka Gwamma ".Tana cigaba da dama furarta cikeda matuk'ar kwanciyar hankali da jin dad'i.

"Amin Inna ".Inji Lawwali.

"ku tashi ku shiga cikin d'aki ku ci abinci idan na gama dama furar zan sha,, in rage muku sauran amma kuyi wanka kafin ku ci abincin ".Cewar Inna Talatu.

Suka ce atare "to Inna ".Suka tashi tsaye suka shige cikin d'aki suna ta dariyar murna da farin ciki..

**** *** **** ****  ***

Acan cikin kasuwa kuwa Malam Mamman ne zaune da Mande suna fira cikin farin ciki da nishad'i sosai ..

Malam Mamman ya dubi Aliyu Mande yace masa "kasan wani abu kuwa Mande ?".

"sai ka fad'a Mamman ina jinka ".Inji Mande mai shago..

Malam Mamman yayi doguwar ajiyar zuciya sannan yace "kwata kwata al'amarin Talatu yana bani mamaki da tsoro,, duk ta chanza kwanakin nan ta zama kamar ba itace mu ka shafe tsawon shekaru muna soyayya ba,, sannan kuma bayan munyi aure muna zaune zaman lafiya babu mai jin kanmu,,, amma yanzu ta tsiro da wani hali mara k'yawo bata ganin girmana ko mutuncina,, zagina tareda rashin kunya kawai takeyi min,, ni yanzu na rasa yadda zanyi da ita wlh sai na ke ganin kamar maganar mutane ta fara tabbata Talatu ta zama abin k'yama wato mayya ce ".

Mande yace "Subahanillah!! Zato zunubi ne koda ya zamo gaskiya ne kada ka zamo mai d'aukar gulma da jita jitar mutane,, kuma ka ga duk k'azantar da ba ka gani da idonka ba tsabta ce,,, ni dai shawarar da zan ba ka amatsayina na amininka kuma abokinka kayi hak'uri kayi hak'uri domin Allah yana tare da masu hak'uri,, komai da kake gani a rayuwa sai mutum yayi hak'uri sannan ya ke zamowa wani abu a rayuwa,, Annabinmu Muhammad (S. A. W) wanda yafi kowa daraja a duniya an zagesa an dukesa an jefeshi da duwatsu wanda sanadiyyar haka nan saida kanshi ya fashe da jini amma yayi hak'uri,, balantana mu da bamu kowa fa ce bayin Allah,, kaje ka cigaba da hak'uri da ita komai na duniya yana da farko yana da k'arshe zaizo ya wuce kamar ba'a yi sa ba ".

Malam Mamman yace "nagode sosai da shawararka abokina hak'ik'a kai mutum ne na gari,, wanda ya san abinda ya kamata insha Allahu zanyi amfani da shawararka".

"yauwa Mamman ka k'ara hak'uri akan hak'uri duniyar yanzu guda nawa ta ke,, lamarin duniya d'an hak'uri ne wata rana sai labari,, Allah ubangiji yasa mufi k'arfin zuciyarmu ".

Malam Mamman yace "tabbas haka ne gaskiya,, amin amin ubangiji Allah ya amshi bakinka ".

"amin amin ".Inji Mande.

Haka dai suka cigaba da firarsu cike da tsananin yarda da juna da shak'uwa,,, abotakarsu zad sha'awa da burgewa ta yadda suke ba ma juna shawarar k'warai batare da wani munafurci ba ko hassada ba.. ....

_Share &Comments_
[6/21, 9:55 PM] Mugiratmusa66: 🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥
*MAYYA CE*
🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥

*INTELLIGENT WRITER'S ASSOCIATION ®*✍🏻
_[Onward together]_

*Written by Mugirat Musa*

*DEDICATED TO SIS NAJER'ART*

_Bismillahir rahamanir rahim_

*PAGE 8*

***Bayan Malam Mamman da Mande sun gama firarsu ne,, sai kowa ya maida hankali kan sana'arshi suka cigaba da lura da jama'ar da ke zuwa wurinsu da kuma masu kai kawo,, domin gudun sata ko afkuwar wani abu mara k'yawon gani..

****   ****   **** ****

***Ab'angarensu Lado da Idi abokinsa kuwa bayan Lado ya jima sosai a wurinsa suna fira,,, to zuwa wani lokaci mai tsawo yayi masa sallama zai wuce gidansa,,, Idi yaji dad'i sosai na ziyarar da abokinsa ya kawo masa ya d'auko sabulun wanka da na wanki yace akaima Hassi,,,,Lado yak'i amsa sai da Idi ya nuna matuk'ar b'acin ranshi sannan ya amsa da k'yar yana yi masa godiya sosai,, Idi ya nuna masa babu komai ai yi ma kaine kuma maida k'yauta baya ne ka tsinceshi acan gaba ne,, Lado yayi masa sallama sannan ya juya zuwa hanyar gidansa cikeda matuk'ar sanyin jiki..

Hassi ce zaune saman kujera k'arama tana cin abinci,, bayan ta gama kukanta tun d'azu babu abinda takeyi sai tunani da zullumin maganar Lado,,, ta ga Lado bai yarda da maganarta ba balantana ayima abun tufkar hanci shiyasa ta bar abin cikin ranta,,,, da niyar gobe zata tambayi Lado iznin zuwa gidansu ta sanar da iyayenta duk abinda ake ciki..

Haka dai ta cigaba da sak'a da warwara a cikin zuciyarta,,, tana cin abincinta sosai can naji takun tafiyar Lado ya shigo da sallama a bakinsa,, hannunsa rik'e da ledar sabulun da Idi ya bashi,,, Hassi ta amsa masa sallamar tareda juyar da kanta gefe saboda a d'azu taji matuk'ar haushin akan yadda yak'i yarda da maganarta,,, tareda da nuna mata halin ko in kula da tana kuka akan abinda ya faru..

Lado ya d'auko tabarma ya shimfid'a kusa gareta,, sannan ya zauna yana fuskantarta yace "Innar Na'ima dan Allah kiyi hak'uri ki daina fushi dani,,, in dai akan abinda ya faru ne wlh na yarda da maganarki na amince muje gidanku anemi mafita ".

Hassi ta juyo tana kallonsa tace "hmm naji komai ya wuce amma ni bance dole sai ka yarda da maganata ba ".

"ki dai yi hak'uri Allah yana tare da masu hak'uri Hassi,, alal hak'ik'a nasan akwai mayyu a cikin garin nan addu'a kawai ce mafita akan kowane lamari,, ina Na'ima take ne? Na ji banji muryarta ba ".Inji Lado cikeda lalama.

Hassi tace "haka ne gaskiya,, Na'ima an aiko daga gidanmu an d'auketa ".

Lado ya bata ledar da ke hannunsa sannan yace "to ya yi k'yau kice yau zasu sha rashin ji da b'arna,, wannan ledar da nazo da ita Idi yace a baki ".

Hassi ta bud'e ledar ta ga sabulun wanka da wanki,, murmushi kawai takeyi can ta nisa tace"ai kuwa mun gode sosai Allah ubangiji yabar k'auna da zumunci,,, sannan da kake cewa Na'ima rashin ji gareta ai acan gidanmu ustaziya ta ke zama,, idan ba haka idan tayi musu b'arna Mariya kashi take bata saboda ita babu ruwanta da yaro "..

"Amin ya rabbi matata,, ai kuwa idan ta bugar min Na'imata zamu had'u gobe ni da ita".Cewar Lado.

Hassi ta yi dariya tace "ina zaka ga Mariya kuma? Balantana ka had'u da ita ".

Lado yace "gidan zamuje gobe da ni da ke idan Allah ya yarda ".

Hassi tace "Allah ya kaimu gobe lafiya ".

"Amin amin ".Cewar Lado..

Hassi ta mik'e tsaye ta shiga cikin d'akinta,, ta kawo masa abincinsa da ruwa masu sanyi cikin jug ta aje gabansa,,, Lado ya wanke hannunsa da ruwa sannan yayi bismillah ya fara cin abincinsa cike da natsuwa da walwala,,, Hassi tana gefensa sai murmushi takeyi masa cike so da k'auna..

********************

Malam Mamman ne zaune yana wankin kayansa ga Inna Talatu xaune gefe tana kallonsa,,, sai hararsa takeyi tana yatsina fuskarta cikin gadara da nuna isa,,, can Malam Mamman ya dubeta duba na fahimta da natsuwa yace "Talatu wai mi ye dalilin abubuwan da kike yimin,,, mi nayi miki ne? Na ga kina yimin wasu abubuwa wad'anda bana jin dad'insu ".

Inna Talatu tace "hmmmm kai dai Mamman kanada matsala,,, ka sha tambayata nace baka yimin komai ba kawai rayuwa ce ta canza ,,amma kazo kana son matsa min da surutu ".

Malam Mamman yace "ba damuwarki nake sonyi ba,,, ina son zamanmu ne ya koma kamar da babu tashin hankali ko hayaniya a cikinsa,, kuma bansan abinda nayi miki ba Talatu duk kin tsane ni kamar auren dole akayi miki tun farko bada son ranki ba akayi auren ba kina sona ina sonki ".

"hmmmmmmm Mamman ka gama tatsuniyar taka to bari kaji! Ni fa yanzu ba da ba ne babu shegen da ya isa ya takura min,,, saboda ayanzu bana tsoron kowa ciki kuwa har da kai domin na yi wuya na isa yanka! ".Inji Inna Talatu.

Malam Mamman ya cigaba da wankinsa yana shanyawa ga igiyar wanki,, bayan ya gama shanya kayansa ya dubi Inna Talatu cikin tsananin b'acin rai da takaicin maganarta,,, yace "Talatu ina son ki san wani abu guda d'aya naji ke baki tsoron kowa,, karki manta ni fa mijinki ne aljannarki tana k'ark'ashin tafin k'afata idan na d'aga ki shiga ciki,,, idan na ta ke ba zaki shiga aljanna ba,,, ya kamata ki san irin maganganun da za ki gaya min ba wai ki dinga yimin magana tsauri tsauri ba kamar ke ce mijin ni ne matar,,, mace ta iya magana da tausasa kalamanta zuwa ga mijinta ba wai ta dinga sako magana duk yadda ta gadama ba,, ni fa bari in gaya maki kin isheni gaskiya! Ina raga miki ne saboda darajar 'ya'yan dake tsakaninmu ba wai domin ina jin tsoronki ba ".

"ahayyeh ahayyeh nanayeh yau naji maganar banza da yofi! Ai ban san kana jin haushina ba Mamman sai kayi min mugun bugu ka sakeni,,, sannan da kake cewa sai ka d'aga k'afarka sannan in shiga aljanna to bana so ka take!!! Yanzu idan na mutu kazo ka kaini cikin wuta to wlh rashin kwanciyar hankali da rashin zaman lafiya yanzu aka fara a cikin gidan nan ".Cewar Inna Talatu cikeda matuk'ar masifa da son tashin hankali.

Malam Mamman yace "ba ni zan kaiki wuta ba mugun halinki ne zai kaiki cikin wuta,,,, saboda haka to tunda abin naki bana arzik'i ba ne,,, ba zai yiyu in ta zama cikin rashin kwanciyar hankali da tashin hankali ba saboda haka ki saurareni da k'yau Talatu aure zan k'ara yi! ".

Dummmm gaban Inna Talatu ya buga da k'arfi!,, zuciyarta ta girgiza hankalinta yayi k'ololuwar tashi sosai,,,babu abinda zuciyarta keyi sai bugawa da k'arfi da k'arfi amma dolenta ta tattaro natsuwarta da dauriya ta sanyama zuciyarta,, saboda kada Malam Mamman yayi saurin gano ta firgita ko tsorata..

Cikin dauriya da nuna rashin tsoro Inna Talatu tace "Mamman kenan k'aryarka ta sha k'arya tunda dad'ewa sosai baka tashi cewa zaka yimin kishiya ba sai yanzu! To wlh daga yau ka k'ulla aure da masifa da tashin hankali,,, kuma wannan auren ba zai tab'a yiyuwa ba! Amma dan Allah ka gwada ka gani idan ka na shakkar maganata ba zata iya yiyuwa ba,,, zan nuna maka ni kishina yafi *KISHIN JAHILCI*".

Malam Mamman yace "mi zaki iya yi ne Talatu ai ko haukacewa zakiyi kibi duniya,,, sai na k'ara aure Insha Allahu idan kika ga banyi ba to mutuwa na yi mahaukaciya wadda batasan ciwon kanta ba ".

"mahaukata dai ga fili ga mai doki nan sauran sukuwa,,, kayi auren in gani ba sai kana raye zakayi auren ba ko? Zan nuna maka ni na haifu ga iyayena ".Inji Inna Talatu cikeda matuk'ar masifa..

"duk abinda zakiyi Allah ya fiki Talatu aure ne dai sai nayi,,, ina raye zaki gani da idanunki! ".Cewar Malam Mamman yaja takalminsa ya barma Inna Talatu gidan tana ta fad'a da tsinema Malam Mamman..

Inna Talatu ta kama yin fad'a da zage zage kamar ta ari bakin kura,,, bakinta har kumfa yake fitarwa akan bala'i idanunta suka rikid'a sukayi jajir saboda tsabar tashin hankali da bala'in da suka bayyana k'arara akan fuskarta..

Ta sha alwashin babu ita babu zama da kishiya har abada,,, ta yanke shawarar irin matakin da zata d'auka a cikin zuciyarta!!!.

*********************

***Washe gari da da rana misalin k'arfe hud'u 4:30pm na yamma,,, Lado da Hassi suka shirya suka je can gidansu Hassi ziyara,,, bayan sun je gidansu Hassi lafiya k'alau suka iske Baba Abubakar da Inna Lami sun gaishesu cikin girmamawa,,, suka amsa musu fuskarsu a sake cikin fara'a da murna sosai. Mariya da take gefe tareda Na'ima ta gaisar da su Hassi,,, suka amsa mata cikin sakin fuska da walwala,,, Mariya ce ta d'auko tabarma ta shimfid'a musu suka zauna tare..

Hassi ce ta duk'ar da kanta k'asa tace "baba mun same ku Lafiya ".

"lafiya k'alau kuka same mu Hafsa ".Cewar Baba Abubakar.

Inna Lami tace "ina fatar kina zaune da mijinki lafiya Hafsa? ".

Lado yayi saurin yin magana yace "ai Hassi 'yar aljanna ce Inna tana yimin ladabi da biyayya gwargwadon iyawarta,,, bata son b'acin raina ko fushina ko kad'an ban tab'a ganin mace mai k'yawon hali ba irin Hassi ba,,, duk abinda nake so shi ta keyi min koda ace ita bata so Baba ai ni banida abinda zan biya ku dashi na aura min Hafsa da kukayi,, sai dai inyi muku addu'a akan Allah ubangiji ya saka muku da mafificin Alkhairi ".

Mariya tace "Amin ya rabbi ".Cike da tsananin jin dad'i akan yadda aka yabi halayyar 'yar uwarta.

Baba Abubakar da Inna Lami babu abinda sukeyi sai murmushi tsantsar farin ciki ne da jin dad'i yake bayyana a fuskarsu,,, can dai Baba Abubakar yace "na ji dad'i matuk'a akan irin yabon da mijinki yayi miki Hafsa,,, hak'ik'a na k'ara tabbatarwa yau ba ki yassuwa tarbiyar da nayi miki ba,,, kai ma Lado nayi matuk'ar farin ciki akan yadda ka rik'eta amana,,, Allah ubangiji yayi muku albarka ".

Hassi tace "Amin Baba amma akwai maganar da nake son in gaya maka ".

"wa ce irin magana ce Hafsa? fad'i ina saurarenki".Cewar Baban.

Hassi zata bud'i baki ta yi magana kenan! Kawai sai naga Lado ya fad'i k'asa kwance yana birgima kamar mahaukaci,,, babu abinda ke fita cikin bakinsa sai jini mai kamar tsokar nama

gunduwa gunduwa,,, yana shure -shure da kakarin mutuwa!

Baba Abubakar da Inna Lami babu abinda suke fad'a illa ina lillahi wa inna ilaihirraji'un!!! Cikeda matuk'ar tashin hankali da rikicewa,,, Hassi kuma kuwwa ta yi da k'arfi tana kuka tana cewa "wayyo Allah wayyo kaina! Shikenan ta kashe min mijina,, rayuwata tazo k'arshe ni Hassi ".Wa ce ce ta kashe miki mijinki ".Inji Inna Lami cikeda matuk'ar tashin hankali!.

Hassi ta sakewa cewa "ta kashe min mijina! ".Ta fasa wata gigitacciyar k'ara da kuwwa da k'arfi! Ta fad'i k'asa ta sume,,,ai kuwa Inna Lami da Mariya suka sake rikicewa Na'ima banda mahaukacin kuka babu abinda takeyi,, Baba Abubakar da ya ke kusa ga gawar Lado shi ma duk ya rikice ya ya mutse kamar ba babban mutum ba.

Ina lillahi wa inna ilaihirraji'un!!! Kawai yake ambato cike da tsananin rud'ewa da d'imaucewa.....

_Share&Comments_
[6/21, 9:56 PM] Mugiratmusa66: 🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥
*MAYYA CE*
🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥

*INTELLIGENT WRITER'S ASSOCIATION ®*✍🏻
_[Onward together]_

*Written by Mugirat Musa*

*DEDICATED TO SIS NAJER'ART*

_Bismillahir rahamanir rahim_

*PAGE 9*

Ina lillahi wa inna ilaihirraji'un!!! Kawai yake ambato cike da tsananin rud'ewa da d'imaucewa..

Hankalinshi ya yi k'ololuwar tashi duk ya gigice da rikicewa,,, Inna Lami ce yayi mata alama da hannu ta d'ebo ruwa a cikin buta ko kofi ,,, ta nufi randar ruwa da saurinta cikin matuk'ar tashin hankali tana ta kukan k'unci da bak'in cikin rayuwa,,,Mariya kuma sai jijigar jikin Hassi takeyi tana zubar da hawayen tausayin kansu da bak'in ciki.

Na'ima tana gefenta tana kuka sai cewa take yi "Inna,, Inna ci ta ci dan anya (Inna ki tashi dan Allah) ".

Inna Lami ta kawo ruwan da saurinta Malam Abubakar ya amshi ruwan ya yi addu'a mai tsawo,,, sannan ya watsa ma Hassi rabin ruwan ya juyo wurin Lado ya watsa mishi ruwan shima,, sannan yayi umurni da Mariya ta shige da Na'ima cikin d'aki ,,dole ne yasa Mariya taja hannun Na'ima ta shige da ita cikin d'aki ba domin ranta yaso ba saboda ita taso ayi komai gaba

gare ta,,, ba sai ta tashi ba amma yata iya dole ta bi umurnin mahaifinta..

Bayan shigerwarsu Mariya cikin d'aki ba,,,, Malam Abubakar ya dubi Inna Lami yaga tana zubar da hawaye yayi mata nuni da ta matso kusa gareshi,,, Inna Lami ta matso kusa gareshi jikinta yanata rawar tsoro da fargabar abinda ke iya faruwa! Malam ya juyo da fuskar Lado ta yadda zasu b'ullo ma lamarin cikin sauk'i,,, yana juyo da fuskarshi yaga duk idanun Lado sun k'ak'k'afe ga kuma jinin da ya b'ata gaban rigarsa babu k'yawon gani ko kallo,,, yasa kunnenshi ya tara a hancin Lado yaji ya ko zaiji yana numfashi..

Ya kai tsawon minti goma yana saurare ko zaiji fitar numfashin Lado amma shiru,,, kamar an shukka dussa ganin haka ne Malam ya d'ago idanunsa wad'anda ruwa sun taru ciki sosai ya dubi Inna Lami cikin matuk'ar sanyin jiki da damuwa,,, yace "Ina lillahi wa inna ilaihirraji'un!!! Kulli nafsin za'ikatul mautt hak'ik'a Allah ubangiji yayi ma Lado rasuwa Lami! ".Gaban Inna Lami ya buga da k'arfi rassssss! Fuskarta na bayyanar da tsoro da tsananin tashin hankali,,, dak'yar ta bud'i baki tace "Subahanillah! Allah ubangiji ya jik'anshi da rahama yasa ya huta,,, mu kuma idan tamu tazo yasa mu cika da imani Malam ".

"Amin Lami ".Cewar alokacin ne yasa hannunsa ya shafe idanun Lado..

Inna Lami tana shesshekar kuka tace "Malam fa ya kamata kaje ka sanar da iyayensa da mutane,,, domin ayi masa wanka akaishi makwancinsa ".

"tabbas haka ne yanzu nan kuwa zan je in sanar da iyayensa da kuma mutane ".Inji Malam

Abubakar ya fad'a tare da mik'ewa tsaye,,, ya kama hanya ya wucewarsa zuwa waje..

Inna Lami na zaune ta zuba uban tagumi tana kuka mai ban tausayi da tarin damuwa,,, can Hassi taja numfashi tari ne ya sark'eta ta falko daga suman da ta yi,,, Inna Lami tayi hamdala cikin zuciyarta ta k'walama Mariya kira,,, Mariya ta shek'o da saurinta Inna Lami tace ta d'ebo ruwa aba Hassi ta sha taje da saurinta ta d'ebo ruwa a randa masu sanyi aka bama Hassi tasha,,, sai sannu kawai sukeyi mata cike da matuk'ar tausayawa. Bayan ta sha ruwan ne Hassi ta kwanta babu jimawa barci ya kwasheta,,, Inna Lami ta dubi Mariya tace "tashi ki shiga cikin d'aki kada Na'ima ta biyoki waje,,, saboda ta yi k'arama da ganin wannan tashin hankali ".

"ai Inna Na'ima tun d'azu ta yi barci fa,,, shiyasa ma kika daina jiyo kukanta ".Cewar Mariya..

Inna Lami tace "to Allah ya k'yauta ".

Mariya tace"amin".Tana rufe bakinta sai ga sallamar mutane su hud'u,,, sun shigo cikin gidan Inna Lami ce ta amsa musu sallama, Malam Abubakar yayi musu jagora har cikin gidan suka d'auki gawar Lado suka fita da ita waje,,, domin aje gidan mahaifinsa ayi masa wanka akaishi gidan gaskiya..

Suna tafiya da gawar Inna Lami da Mariya suka rungume juna suna kuka mai ban tausayi da

tsuma zuciyar mai sauraro,,, tausayin Hassi da Na'ima ya k'ara d'arsuwa a cikin zuk'atansu,,, Hassi ta zama k'aramar bazawara yayinda Na'ima ta zama marainiya abar tausayi...

*** *** *** *** *** **

***Anje an yima Lado wanka da sanyashi cikin likkafani,,, anyi masa sallah sannan aka kaishi makwancinsa.. *(Allahu Akbar duniya kenan rai bak'on duniya ,,,mutum ba'a bakin komai yake ba a cikin wannan duniyar mai cike da k'unci da bak'in cikin rayuwa 😭😭)*...

Kwatsam! Bayan mutuwar Lado sai da mutum kusan hud'u suka rasu a rana guda,,, mace uku maza biyu gami da Lado hak'ik'a a wannan ranar mutanen sun shiga tashin hankali da rikicewa! Akan mutuwarsu Lado ko'ina ka diba mutane ne zaune suna bak'in ciki da jimamin rasa 'yan uwansu,,, mata da yara k'anana kuka kawai sukeyi cike da tsananin damuwa da bak'in cikin rayuwa,,, to ya zasuyi wanda yafi sonsu ya k'arbi ran abinsa dama ita duniya haka ta gada hak'uri shi ne kan gaba da komai,,,, shi ne kuma jigon rayuwa ko munk'i ko munso dole wata rana za'a wayi gari babu mu cikin wannan duniya mai cike da k'alubalen rayuwa ".(Allah ubangiji yasa mu cika da imani muna musulmai)...

_Kunga kenan babu abinda ya gagari mayyu,,, sai dai ikon Allah_..

*BAYAN KWANA HU'DU*

***Bayan kwana hud'u da faruwar wannan mummunan al'amari,,, mutane kowa ya cigaba da harakokinshi...

Inna Talatu ta cigaba da musgunawa rayuwar Malam Mamman tareda ci masa mutunci da tozarci,,, kullum kullum da irin kalar walak'ancin da zata masa kowace safiya idan garin Allah ya waye,,, bayada natsuwa da kwanciyar hankali masifar safe daban ta rana daban ta dare da daban,,, bata ganin mutuncinshi da girmanshi ko kad'an. Har takai ta kawo Malam idan zai dawo gidansa har fargaba da tsoronta yake ji,, ta zame mishi ciwon ajali ya rasa yadda zaiyi da ita bayada natsuwa da kwanciyar hankali ko kad'an,,, a cikin kwanakin nan idan kaga yadda Malam Mamman ya rame sai kun tausaya mishi,,, har ta kai ta kawo ko abincin gidan nan bata aje mishi sai dai yaci acan kasuwa gurin masu sayarwa,, amma haka bawan Allah nan yake hak'uri matuk'a da ita,,, ganin yayi tana shirin kashe shi tunda sauran ranshi yasa dole ya fara neman wata bazawara mai suna Laweeza a cikin unguwarsu da aure..

Inna Talatu MAYYA ta ji labarin neman auren Laweeza da yakeyi amma da yake k'usurgumar *MAYYA CE*,,,sannan kuma ta san muguntar da zata k'ulla yasa ko a fuska bata damu ba bale a cikin zuciyarta..

***Wata rana Malam Mamman ne yayi wankansa sannan ya d'auko shaddarsa sabuwa a cikin kayansa yasa,,,, ya feshe jikinsa da turare sannan ya dubi kanshi a madubi yaga ba laifi ya jawo k'ofar d'akinsa ya kulle da padlock,,, ya fito filin gida Inna Talatu tana zaune tana gyaran shinkafar da zata yi tuwo da ita gasu Gwamma da Lawwali zaune gefe suna wasarsu cikin kwanciyar hankali..

Inna Talatu tana ganin irin wankan da Malam Mamman ya d'auka ga k'amshi sai tashi yakeyi na turarensa,,, ta yi masa walak'antaccen kallo mai cike da raini ta ja mugun tsoki mtsssss! Sannan tace "Mamman mai budurwar zuciya ina zaka je? ".Tayi masa tambayar rainin wayo..

Ya juyo ya kalleta da yake yasan tambayar raini ne ta yi masa,,, yayi murmushin mugunta yace "wurin masoyiyata matata mai son farin cikina,,, tana gudun b'acin raina ta iya kalamai masu sanyaya zuciyar masoyi gata da tarbiya da biyayya,,, ga ta d'iyar mutanen k'warai alal hak'ik'a nayi matuk'ar dace da samun mace ta gari Talatu,,, idan kina zuwa zan kaiki gobe ku gaisa da ita saboda tun yanzu ku saba da juna ".

Hali zanen dutse! Hak'ik'a maganganun Malam Mamman sun matuk'ar k'ona zuciyar Inna Talatu,,, babu abinda zuciyarta keyi sai suya rayuwarta idan har tayi dubu to ta b'aci sosai..

Ta bud'i baki tace "Mamman kenan mi kake ci na baka na zuba? Wato bazawarar da kake nema itace mai kirki ni ce mara kirkin ko,,, itace d'iyar mutanen k'warai ni ce d'iyar mutanen banza ko itace wadda ta iya kalamai ni ban iya ba? To ka rubuta a takarda ka ajiye wlh wannan auren muddin ina raye ba zai tab'a yiyuwa ba! Na fika iya shege na rashin mutunci da hatsibibanci ".

"tabbas ta fiki duk abinda na lissafa harda wanda ban fad'a ba ta fiki,,, sannan baki isa ki hanamin k'ara aure ba Talatu ba zaki hana inji dad'i ba kamar yadda kowane magidanci mai mata biyu keji ,,,idan naga kina son b'atamin gida sai in sakeki ki koma gidanku! ".Cewar Malam Mamman cikeda matuk'ar zafin rai da haushi..

Inna Talatu tace "to sai mi idan ka sakeni nifa ba irin wad'annan matan bane wad'anda ake

tsoratarwa da kalmar saki,,, so kake ka kawo wata a cikin gidan nan kazo kana iskanci da ita agaban 'ya'yanka kana tab'a mata nono ko,,, bazai tab'a yiyuwa ba nadai gaya maka gaskiya ".

Malam Mamman yace "sai nayi abin nan da bakiso ko na sadu da ita idan har na aureta ai halat na aikata ba haramun ba,,, ke kinyi kad'an ki haramta min abinda Allah ya halat min ba kuma ko mutuwa zakiyi saina k'ara aure! ".

"hmmm haka kace? To mu zuba mu gani ni da kai shege ya fasa,,, wanda yaji tsoro ya janye d'an wuta ne a tsakaninmu".Cewar Inna Talatu cikeda son tashin hankali..

Mal. Mamman yace "mahaukaciya wawuyar jahila! Ai kece 'yar wuta kuma shegiya dama ai mace idan bata biyayya ga mijinta sunanta 'yar wuta,,, kinyi 'k'arama wlh da ki hana min rawa gaban hantsi,, banda lokacin karya irinki! ".Yasa kai yayi tafiyarsa zuwa inda zaije..

"kaine k'aton kare kuma jahili! Wallahi zaka gane bakada wayo ko dabara,, zan nuna muku ni murucin kan dutse ce ni ban fito ba saida na shirya,,, ni ce ajalinku da kai da ita! Hmmmm yaro baisan wuta ba sai ya taka andaiji kunya ana son ayi aure adinga yi mata iskanci da tambad'a yara suna kallo,,, ni ba zan bari a lalata min yarana ba ".Inji Inna Talatu cikin jin haushinsa..

*********************

Malam Mamman naga yazo baki k'ofar gidansu Laweeza ya samu yaro ya aika domin ayi masa sallama da ita,,, can yaro ya fito daga cikin gidan yace masa tana zuwa Malam Mamman ya bashi naira ishirin yaron ya amsa yayi godiya ya wucewarsa yana jin dad'i sosai.
Bayan mintuna kad'an saiga Laweeza ta fito daga cikin gidan tana tafiya cike da yanga da natsuwa,,, tana isowa wurin Malam Mamman ta gaidashi ya amsa cikin fara'a da murmushi..

Nayi duba zuwaga fuskar Laweeza ashe k'yakkyawa ce bak'a ba tilin ba,,, tanada doguwar fuska tareda da dogon hanci ga madaidaicin bakinta,, wanda ya k'ara mata k'yawo sosai..

Malam Mamman ya nisa yace "Lawiza ".

Tace"Na'am ".Tana wasa da yatsun hannunta.

Yace mata "ina son ki bani dama in turo magabatana asa mana rana,,, saboda kinga ni da ke ba wannan ne karo na farko da zamuyi aure ba ke kin tab'a aure harda yaro ni inada mata harda yara biyu,, saboda haka mu ba yara bane da zamu tsaya b'atawa kanmu lokaci ,,,shin miye ra'ayinki game dani kina sona kin aminta naturo magabatana? ".

Lawiza tace masa "na amince amma ina tsoron abinda zaije ya dawo,,, saboda naji ana fad'a agari cewa matarka masifafffar mace ce mafad'aciya sannan kuma ance ana zarginta da maita!.....

_Share &Comments_
[6/21, 9:56 PM] Mugiratmusa66: 🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥
*MAYYA CE*
🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥

*INTELLIGENT WRITER'S ASSOCIATION ®*✍🏻
_[Onward together]_

*Written by Mugirat Musa*

*DEDICATED TO SIS NAJER'ART*

_Bismillahir rahamanir rahim_

*PAGE 10*

Lawiza tace "na amince amma ina tsoron abinda zaije ya dawo,,, saboda na ji ance matarka masifaffiyar mace ce mafad'aciya sannan kuma ance ana zarginta da maita a cikin garin nan,,, kaga kuwa dole hankalina ya tashi sosai in dai domin fad'a ne to abin da sauk'i saboda saina

kulata ne zamuyi sa'insa ni kuma ba zan kulata ba idan Allah ya yarda ".

"hmmmm wannan maganar ta maita da akecewa matata tana yi ba gaskiya ba ne,,, wannan zance ne na mak'iya da mahassada wad'anda basu son mutum a rayuwa ko cigaban mutum,,,,lafiyar matata k'alau kawai dai mafad'aciya ce shi ne gaskiyar magana ".Cewar Malam Mamman cikin taushin murya da lallashi..

Lawiza tace "to shikenan na yarda ka turo a sanya mana rana ".

Malam Mamman yace "yanzu naji maganar k'warai Lawizata amma ko gobe ina baki shawarar ki daina yarda da maganar mutane,,, domin su mutane iyawa dasu sai ubangiji duk abinda kakeyi saika samu wanda ya kusheka yakejin haushinka,,,, saboda hassada da bak'in ciki a cikin jinin d'an Adam yake".

Lawiza tace "ai kuwa karka damu komai ya wuce na daina yarda da maganganun mutane,,, ni ke aure ba mutum duk wadda ta kawo tseguminta ko anyi ance zanyi kunne uwar shaggu da ita harta gaji ta k'ara gaba ".

"dako kin k'yauta mana wlh,, sannan karki damu jibi zan turo manyana wurin babanki saboda haka ki sanar da su da wuri,,, ga wani 'yan chanji inbaki farin cikin rayuwata ".Fad'ar Mlam Mamman yana washe mata hak'oransa da suka gogu da aswaki zad sha'awa,,, ya mik'a mata kud'i da kuma bak'ar leda..

Lawiza tasa hannu ta karb'a cikeda matuk'ar kunya da k'aunarsa,,,sannan tace "nagode sosai Allah ya saka da alkhairi ".

Mal. Malam Mamman yace "Amin amin rabin jikina,,, to ni zan wuce gida yanzu ki gaida mutanen gidanku ".(🤣🤣Ka ji su Malam an iya lobaiya da kashe murya).

"zasu ji mijina Allah ya kiyaye hanya ya tsare min kai ".Cewar Lawiza cikeda nuna kulawa da soyayya.

Ai kuwa wannan addu'a da ta yima Mal. Mamman ba k'aramin masifar dad'i yaji ba,, wani irin sanyi ne yabi jinin jikinsa yace "Amin babina ".Sannan ya kama hanyar zuwa gidansa,, ita kuma ta shige cikin gidansu ..

********** ******* ****

***Ab'angaren gidansu Hassi bayan anje ankaisu Lado gidansu na gaskiya shi da sauran mutum hud'u,, da suka rasu rana d'aya..

To bayan Hassi tayi barci mai tsawo daga baya saita falka daga barcin,,, tana tashi da hamma ta tashi daga barci Mariya ce ta d'ebo abinci da ruwa masu sanyi ta kawo mata,, Hassi ta yi bismilla ta fara cin abincinta sai da taji tayi nak sannan ta wanke hannunta ta sha ruwa sosai,,, Inna Lami ce ta had'a mata ruwan wanka ta taimaka mata ta yi wanka sannan aka d'auko kala d'aya tsofaffi daga cikin kayan Mariya aka bata ta saka...

Zuwa anjima da daddare da Malam Abubakar ya dawo gida,, bayan sun kammala cin abincin dare ne Malam Abubakar yayi gyaran murya yace "Hafsa ".

"Na'am baba ".Cewar Hassi cikin mutuwar jiki da fargaba..

Mal. Abubakar ya dubeta cikin tausayinta da tsantsar k'aunar 'yarsa yace "ina so ki saurari abinda zan gaya miki da k'yau,,, ki fahimci maganata cikin natsuwa da kaifin tunani kinsan da cewa komai ya faru da bawa muk'addari ne daga Allah kuma babu wani mahaluk'i a cikin wannan duniya,,, da ya isa kaucewa k'addararsa Allah ya riga ya rubuta a cikin littafinmu duk irin abubuwan da zai samu mutum tun daga farkon haihuwarsa har zuwa mutuwarsa,,,, ana son musulmi na k'warai yayi imani da k'addara mai k'yau ko mara k'yau,,, sannan duk abinda Allah ya baka a matsayin aro na wani lokaci daga baya ya amshi abinsa zakiji ciwo Hassi? ".

Hassi ta gyad'a kai cikin matuk'ar sanyin zuciya da zullumi! Ta bud'e baki tace "a'a baba ".

Malam Abubakar yace "kiyi hak'uri da duk abinda zakiji Hafsa domin Allah yana tare da masu hak'uri,,, ubangijin da ya baki Lado a matsayin miji ya k'addari aurenku ya kuma k'addari samuwar Na'ima a tsakaninku batare da sisinku ba,,, ya amshi ran Lado domin ya fiki sonshi aronsa dama ya baki ".

Hassi tana jin wannan maganar ta fashe da wani rikitaccen kuka mai ban tausayi,,, hankalinta yayi k'ololuwar tashi zuciyarta sai k'una da rad'ad'in zafi sosai takeyi mata ..

Inna Lami ce ta rungumeta tana lallashinta da fad'a mata kalamai masu sanyi a cikin zuciya,, tana cewa "kiyi hak'uri hafsa kiyi ta fad'ar wannan kalma ina lillahi wa inna ilaihirraji'un!!! Alhumma ajirni fi musibati wa'akhalufni min khari minha,,, da yarda Allah zakiji sauk'i cikin zuciyarki Allah ubangiji ya jik'an Lado ya gafarta masa zunubbansa ".

"kiyi hak'uri yaya Hassi ki daina kuka addu'a kawai ce yaya Lado ke buk'ata a gareki,,, ba kuka ba saboda kukan mai rai akan mamaci azaba ne kuma masifa ne,,, ki tausayawa mana ki daina kuka 'yar uwata saboda nima zaki iya sakani kuka ".Cewar Mariya idanunta sun cicciko da ruwan hawaye..

Inna Lami tace "ki daina kuka ki saurari maganarmu kuma ki fahimcemu Hafsa,,, duk abinda kika gani daga Allah ne sannan ina son ki sanar dani waye kike cewa ta kashe Lado d'azu alokacin da ya fad'i k'asa yana aman jini? ".

Mal. Abubakar yace "tabbas muna son muji wani bayani a cikin bakinki,,, sannan d'azu wa ce irin magana ce kikaso gaya min da baki samu dama ba? ".

Hassi ta d'ago jajayen idanunta wad'anda suka kumbura akan zubar hawaye,, ta bud'i baki dak'yar tace "tabbas ba mutuwa akeyiwa kuka ba sabo ne akeyiwa kuka ,,,baba,, Inna,, Mariya hak'ik'a na yarda komai ya faru da bawa muk'addari ne daga Allah kuma mutum bai isa ya gujewa k'addararsa ba,, Lado ya riga ya zamo ginshink'in rayuwata kuma jigona ni da 'yata mantashi alokaci d'aya yanada matuk'ar wuya agareni sai dai a sannu sannu cikin wani lokaci,,, ku dai tayani da addu'a Allah ubangiji ya k'ara sanyaya zuciyata tareda hak'uri da juriyar rashinsa,,, yanzu kuwa zan baku labarin abinda ya faru da marigayi kafin ya rasu....... ".Nan da nan ta basu labarin da Lado ya bata kafin ya rasu,,, na gamuwarshi da karya alokacin da ya fito waje domin yayi fitsari...

Babu abinda bata gaya musu ba kamar yadda dai ya sanar da ita..

Tana gama bada labarin suka saka salati atare,,, da kuma fad'ar kalmar ina lillahi wa inna ilaihirraji'un!!! Duniya ina zaki damu wannan ai rashin imani ne,, anya wasu mutane suna tuna mutuwa kuwa,, anya mutane suna tuna kwanciyar kabari da hisabi kuwa,,, anya wasu mutane suna tuna cewa komai daren dad'ewa zasu koma ga Allah ubangijin talikkai? ".Cewar Inna Lami cikeda matuk'ar tashin hankali da jimami..

Mal. Abubakar yayi huci mai zafi da ajiyar zuciya yace ".wannan magana taki akwai alamun k'amshin gaskiya a cikinta na cewa *MAYYA CE* ta kama Lado,,,, amma kuma sanin gaibu sai

Allah idan ma itace mun barta ga ubangijin sammai da k'assai wanda baya kwana baya angaje shi zai miki *SAKAYYA* tun anan duniya Hassi,, saboda haka ki share hawayenki ki tashi kuje da Mariya gidanki kiyi takaba acan domin haka ne yafi dacewa ".

"wannan gaskiya ne maganarka ".Inji Inna Lami cikeda matuk'ar tausayin Hassi..

"ya zamo dolena in kiyaye dokokin ubangijina yi muku biyayya ya zamo wajibi agareni iyayena,,, zan tashi in koma gidan Lado inyi takabata acan kamar yadda kuka umurceni amma dan Allah ku tausayamin ku sakani a cikin addu'arku ku rok'armin akan Allah ya sanyamin hak'uri da dangana na rashin Lado ".Cewar Hassi yayinda take zubar da hawayen bak'in ciki da k'uncin rayuwa..

Mal. Abubakar yace "karki damu akodayaushe muna yi muku addu'a Hassi,, ki sani albarkarmu da aminci yana tare daku a duk inda kuka shiga a cikin fad'in duniyar nan,, Allah ubangiji ya tsaremin ku yayi muku albarka ".

Mariya tace "Amin ya rabbi baba ".Tana share hawayen da ke fitowa daga idaniyarta.

Inna Lami tace "Allah ya sanya miki hak'uri da dangana akan wannan k'addarartaki,,, ki sani ku

masu albarka ne akodayaushe akowane lokaci,,, kuma kuna tareda aminci da yarda Allah saboda haka ku tashi ku tafi gida kafin dare yayi k'warai,, Mariya jeki d'auko Na'ima tana cikin d'aki ku wuce ".

Mariya tace "to Inna ".Ta tashi tsaye ta shiga cikin d'akin ta d'auko Na'ima,,, tasa zanen Inna Lami tsoho ta goyata a bayanta.

Itama Hassi dole tasa ta mik'e tsaye suka yima iyayensu sai da safe,,, iyayen suka k'ara sanya musu albarka tareda yi musu fatar alkhairi a rayuwa,,, sannan su Hassi suka nufi gidan marigayi Lado..

*********************

***Ab'angaren Malam Mamman kuwa bayan ya dawo daga wurin Lawiza yarinyar da yake son ya aura,,, to aranar sai da sukayi fad'a har na tashin hankali da Inna Talatu,, saboda har kwalar rigarsa ta rik'e tareda sa hannunta ta shak'e mishi wuya sosai cike da son kasheshi.
Yayi amfani da k'arfinshi na zama namiji ya b'anb'are hannunta dak'yar ga wuyansa,,, bai b'ata lokaci ba ya kashe ta da wasu mahaukatan maruka hud'u masu rai da lafiya,,, wanda sai da jinta ganinta suka d'auke na wucin gadi ga wani mahaukacin zafi da rad'ad'i da yake fitowa daga kuncinta..

Haka dai rikici da tashin hankali ya cigaba da gudana a cikin gidan Malam Mamman,, wata rana har dambe take cewa tayi dashi cikeda matuk'ar masifa da bala'i shi dai saidai ya ceci kansa domin har makami ko takobi take d'auka tace saita kasheshi,,, haka dai zaiyi dabarar amshe makamin sannan yayi mata matsiyacin duka wanda sai tayi fitsari da tutu cikin wando saboda bak'ar wahala,, amma ba zai hana gobe tayi mishi rashin kunya ba ko tace zatayi dambe dashi..

**Malam Mamman ya aika magabatansa a gidansu Lawiza aka saka ranar aurensa da Lawiza nan da sati biyu masu zuwa.
A wannan ranar Malam Mamman ji yayi kamar anyi masa bushara da gidan aljanna akan tsananin farin ciki da murna sosai,, akan murna ya siyo kwalin minti da chewgam yana rabawa 'yan uwa da abokan arzik'i tare da sanar musu da lokacin aurensa..

Hak'ik'a 'yan uwa da abokan arzik'i sun tayashi murna matuk'a tareda yi masa addu'ar fatan alkhairi a cikin auren da zaiyi,,, haka ya nufo gidansa cikin farin ciki da walwalarsa,, bayan ya shigo cikin gidan tareda sallama a bakinsa ya samu wuri ya zauna yace "Talatu albishirinki ".

Inna Talatu ta hararesa sannan tace "dallah rufamin bakinka tsohon munafiki! Azzalumi maciyi amana,, wato kazo ne kayimin albishir da ka kusa zama ango ko to ai kana bari har a d'aura auren bawai kazo kana yimin cika bakin banza!! Zaka gani idan zakayi auren ayi dai mu gani idan tusa zata hura wuta ".

Yace mata "haukarki ko kishinki na jahilci baya tayar mini da hankali aure ne kamar an d'aura

kina gani da idonki,,, saboda haka ki iya tsabtace kalamanki zuwa gareni Talatu ".

Inna Talatu ta juyo ta dubeshi da jajayen idanunta b'acin rai k'arara akan fuskarta ta bayyana,,,tace masa cike da jin haushin maganarsa "bakasan wa ce ce ainahin Talatu ba ganina kawai kakeyi Mamman,,amma zan nuna maka banbanci a tsakanin suga da gishiri zakasan ni ba sakaryar mace ba ce da zata zauna da kishiya,,, wannan auren ba komai ba ne a wurina da ya wuce rusasshe ".

"ba zaki iya ba Talatu aurena kumada Lawiza kamar an d'aura ne ".Cewar Mal. Mamman.

Inna Talatu ta bushe  da mahaukaciyar dariya sannan tace "zaka ko gani lokaci ne kawai zai tabbatar da zan iya ko bazan iya ba amma zaka gani da idanunka idan wannan munafikin auren naku zai yiyu! "......

_Share &Comments_
[6/21, 9:56 PM] Mugiratmusa66: 🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥

🍥🍥
🍥
*MAYYA CE*
🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥

*INTELLIGENT WRITER'S ASSOCIATION ®*✍🏻
_[Onward together]_

*Written by Mugirat Musa*

*DEDICATED TO SIS NAJER'ART*

_Bismillahir rahamanir rahim_

*PAGE 11*

Inna Talatu ta bushe da mahaukaciyar dariya sosai sannan tace "zaka ko gani lokaci ne kawai zai iya tabbatar da zan iya ko bazan iya ba,, amma zaka gani da idanunka idan wannan munafikin auren naku zai yiyu! Kuma yanzu ka cigaba da fuskantar barazana da tashin hankali kenan har abada a cikin rayuwarka Mamman,,, saina nuna maka ainahin mummunan halayyarta sai ka gwammace ma kid'i da karatu saina wargaza duk wani farin ciki naka! ".

Mal.Mamman yace "ni surutunki ko haukarki baya tayarmin da hankali,,, sannan farin ciki yanzu na fara kasancewa a cikinsa gida dai nawa ne inada ikon in auri mace d'ai d'ai har guda uku bayan ke Talatu,, domin ba gidanki ba ne nawa ne ko kare na jawoshi na kawoshi cikin gidan nan baki isa ki koreshi ba bale mace matata uwar yarana masu zuwa ".

"hmm tun yanzu kaje ka d'aukota ku kwana idan har ka cika namiji bak'in jarababbe,,, nifa bana magana biyu magana d'aya nakeyi tak saboda haka kasha kuruminka angon Lawiza aure dai ko to kaje kayi! ".Inji Inna Talatu cikin bak'ar magana..

Malam Mamman yace "aiko baki ce ba sainayi aure saboda haka ki daina b'ata miyan bakinki a banza ".

"naji mijin mace hud'u ".Fad'ar Inna Talatu ta tashi sannu a hankali ta shige cikin kitchen,, tana cigaba da aikace aikacenta batare da ta k'ara sauraren maganar Mal. Mamman ba..

Shi kuma Malam ganin Inna Talatu ta fita batunsa,, tana aikace aikacenta dole yasa ya mik'e tsaye yayi shigewarsa cikin d'aki,,, domin yayi barci dama ya gaji sosai...

*********************

Lawwali ne zaune bakin k'ofar gidansu da leda cikeda nama yana ci,,, ga pure water masu sanyi guda biyu yana sha..

Yana tsakar cin naman saiga Gwamma ta fito daga cikin gidan,,, tana fitowa idanunta ya kai ga ledar naman da Lawwali keci akan kwad'ayi irin na Gwamma ta fitar da halshe tana lasar baki,,, sai naga ta matso kusa ga Lawwali tana kallonsa shi kuma ya k'ara juyar da kansa kamar bai ganta ba tare da tamk'e fuska.
Gwamma ta dafa kafad'arsa tace "Lawwali juyo da fuskarka mana nice fa kawai domin ka samu nama,, zaka juyamin baya ko mi nayi maka ne?".

"aini banma lura da ke ba yaya Gwamma,, to yanzu mi kikeson inyi miki ne? ".Inji Lawwali yana cigaba da cin naman..

Gwamma tace "ban gane mi nake so kayimin ba ai kasan abinda nake so,, to naman da kakeci zaka sammini nima in had'iye kwad'ayina ".

"hmm yaya Gwamma kenan har kin manta ko to bari in tuna miki,, ranar nan ba kece kikasa Innarmu ta dokeni ba harda gaya mata nace mata ita mayya ce,, ta bani mugun kashi har na suma ke kuma sai dad'i kawai kikeji abinki saboda haka bazan sammiki namana ba ".Cewar Lawwali..

Gwamma tace "dama inada niyar baka hak'uri k'anena dan Allah kayi hak'uri ka yafemin,,, abinda ya faru ya riga ya faru wlh bazan sake yi maka munafurci a wurin Inna ba,, muddin ka bani nama naci kuma ai nasan abinda ake fad'a gaskiya ne Innarmu k'usurgumar *MAYYA CE*,, kuma babanmu kishiya zaiyi mata saboda mugun halinta da bayada k'yawo kullum kullum ci masa mutunci takeyi akodayaushe akowane lokaci ".

Lawwali yace "ya isa abar maganar domin ke bakinki bayada linzami,, saura kuma gobe ki k'ullamin munafurci ko gulma da ko idan kikaga abu a wajena mutuwa zakiyi bazan baki ba,, saboda haka kiyaye ".

"bazan ma k'ara ba wallahi aini banda kamarka a cikin wannan duniya,,, daga yanzu ko wani naga zai tab'a min kai sai inda k'arfina ya k'are ".Cewar Gwamma.

Lawwali yace "Allah yasa da gaske kikeyi har cikin zuciyarki ".Sannan ya bata sauran naman da ya rage da pure water guda,, da sauri Gwamma ta fisge ledar saboda kwad'ayi har miyau ya fara dalala daga cikin bakinta,,, ta fara d'aukar tsoka biyu tasa cikin bakinta tana ci tana gyad'a kanta cikeda matuk'ar jin dad'i ..

Sannan tace "da gaske k'anena nagode sosai,, amma fa kada ka fad'ama kowa ka bani nama naci ".Tana cin naman tana lasar yatsun hannunta..

Lawwali yace"to aini ba irinki ba ne mai tonon asiri,, ni kinga tafiyata nayi wurin wasa kuma naman da kikaga inaci babane ya sayamin domin kada kiyimin wata fassarar ta daban ".Bai saurari abinda zata ceba ya k'ara gaba yayi tafiyarsa.

Gwamma tace "ni dai ko satowa kayi ina ruwana muradina shine ni dai inci nama mai dad'i,,, saboda haka ko naman mutane ne ka samo saina cishi babu abinda ya dameni ".Ta cigaba da cin naman bayan ta cinye tas tareda lashe takarda da hannunta,, sannan ta sha ruwan pure water ta kuma wanke hannayenta,,, sannan ta juya tayi cikin gida..

********************

***Inna Talatu ta cigaba da kamun kurwar mutane tana mayarda su fa ra ko kaza,, daga baya ta gasa naman mutane ko ta cishi hakanan d'anye kullum kullum saita fita kamun kurwa a kowane lokaci,,, idan ta hango mutum daga nesa ta kama tsura mishi idanu kenan domin tana hango kayan cikin mutane,,, idan kai ma'aboci yawan addu'a ne da iznin Allah ba zata iya kamaka ba,, idan mutum ya zama lusari mara son addu'a kallo d'aya ne ta chafke kurwar mutum tayi gaba da ita.
Haka zataje ta aje kurwar wurin murhu ko wurin randar ruwa masu sanyi,,, idan abin yayi kwana biyu mutum ya kama tsananin rashin lafiya sosai wani za'a samu jikinsa da sanyi wani ko yayi mugun zafi kamar garwashi,, to wanda jikinsa yakeda sanyi kurwarsa tana aje ne a wurin randar ruwa wanda jikinsa yakeda zafi kuma ta aje kurwarsa kusa ga garwashi,, haka mutum zaiji kamar ana sukar jikinsa allura saboda zafi da rad'ad'in ciwo..

Wani ma idan ya gagari mayyu aljannu suke ba kurwar mutum,, domin a halaka mutum kowa ya huta.

_Allah ubangiji ya karemu daga muyagun k'addarori da kuma fad'awa tarkon wahala_.

**Kwanakin auren Malam Mamman da Lawiza sai k'ara gabatowa yakeyi,, Inna Talatu kuwa sai k'ara cin mutunci da tozarci takeyi masa kala kala daban daban,,, ta k'untaceshi ta hana mishi zama cikin gidan sosai saboda tsabar masifa da fitina irin tata,,, bayada halin ya dad'e k'warai cikin gidansa batare da sun kachame da rikitaccen fad'a ba. Komai ta d'auko jefarsa takeyi dashi ba adda ba  na wuk'a ba,, harda duwatsu jifarsa takeyi dasu sai ya kauce domin kada tayi masa illa  ko ta halakashi..

Ganin haka ne yasa dole ya rage yawan zama cikin gidansa,, sai dai idan ya dawo daga kasuwa yayi wanka ya fita can wurin majalisarsu ya zauna,,, idan yaga abokansa sunyi gidansu su dawo shi sai dai kuma ya k'ara gaba wata majalisar ya zauna,, acan waje zaici abinci yayi komai sai tsakar ya daidaici tayi barci ya dawo gida,, amma duk da hakan bai tsira ba ashe tana nan tana jiranshi yana dawowa ta aza mishi ruwan bala'i da masifa tana zage zage,, da yake yaga dare ne yayi kunnen uwar shaggu da ita yayi kwanciyarshi cikin d'akinsa..

Tayi fad'anta na rashin dalili ta gaji,,, sannan daga baya ta kwanta tana jin haushin rashin kulata da baiyi ba..

Ana saura kwana uku auren Malam Mamman da Lawiza Kwatsam!! Inna Talatu ta tashi da tsakar dare,,, misalin k'arfe 12:15am na dare ta girgiza sannan ta karanta wasu d'alamisai na tsafi da sihiri,, nan da nan wurin ya gameda da bak'ar guguwa da tururin hayak'i,,, guguwar ta daina yawo ta tsaya cak hayak'in ya shige cikin jikin Inna Talatu ta rikid'a ta koma mage......

Managed it please munada matsalar wutar nefa shiyasa.

_Share&Comments_
[6/21, 9:56 PM] Mugiratmusa66: 🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥
*MAYYA CE*
🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥

*INTELLIGENT WRITER'S ASSOCIATION ®*✍🏻
_[Onward together]_

*Written by Mugirat Musa*

*DEDICATED TO SIS NAJER'ART*

_Bismillahir rahamanir rahim_

*PAGE 12*

Inna Talatu ta rikid'a ta zama mage mai fari da bak'i,,,,,sai naga ta fice da sauri daga cikin dak'in kamar k'iftawa da bismillah,,tana kawowa wurin sakatar ta kalli k'ofar da idanunta wani farin haske ne ya fito daga cikin idanunta ya shafi sakata,,, sai kawai naga k'ofar ta bud'e kanta,,, magen ta wuce da saurinta tana wani masifaffen gudu mai cike da al'ajabi da matuk'ar ban tsoro!..

Abin ya matuk'ar bani mamaki kuma ya d'auremin kai ni Mugirat ,,,nabi magen da sauri saboda kada ta b'acewa ganina tana sauri ina biye da ita har muka kawo k'ofar gidansu Lawiza,,, sai naga magen ta tsaya tana duban k'ofar gidansu Lawiza na d'an lokaci ,,,,ta bud'e bakinta kenan saiga jar iska ta bayyana suu suu suu ta nufi k'ofar gidan ya bud'e da sauri,,, magen bata tsaya b'ata lokaci ba ta afka cikin gidan da gudu..
Tana shiga sai na ga ta nufi d'akin dake gefen dama ta afka cikin da sauri,,, tana shiga ta iske Lawiza kwance kamar matatta tana barci,,, magen ta girgiza sannan ta rikid'a ta koma mutum wato ainahin siffarta Inna Talatu,, saboda k'arfin hali da kuma rashin imani saida tayi wani sihirin da ya tayar da Lawiza daga barcinta mai dad'i sosai,, Lawiza ta falka a firgice! Cikeda matuk'ar tsoro da gigicewa ta daure dak'yar tace "wa ye yake tayar dani a cikin wannan tsakar dare? ".

Inna Talatu ta bushe da wata irin mahaukaciyar dariya sosai,,, wanda akan haka saida d'akin ya kama girgiza tanbal tanbal,, abubuwan dake cikin d'akin suka kama fad'uwa k'asa suna halakewa,,,idanun Inna Talatu suka k'ara ja hannunta ya k'ara tsawo zago zago farcenta yayi tsini kamar allura,,,ta dubi Lawiza cikin takaici da haushi tace "nice Talatu matar Mamman wanda kike shirin aura saboda bakida hankali! ".Lawiza taji gabanta ya buga da k'arfi rasssss tsoro da tashin hankali ya bayyana akan fuskarta ,,,tace "baiwar Allah mike tafe da ke,, shin mi ne ne dalilinki na zuwa wurina a cikin tsakar dare ,,,a ina kika shigo saboda nasan rufe gidanmu akeyi idan dare yayi sosai? ".

Inna Talatu ta banka mata harara da idanunta jawur kamar kan maciji,,, sannan tace "yanzu kuwa zan baki amsar tambayoyinki yarinya! Ni da kike ganina ayanzu gaba gareki *MAYYA CE NI TALATU*,,, ta sihiri na shigo cikin gidanku dalili kuma shine nazo ne in kasheki har lahira! Saboda mijina da kikeson ki aura ni talatu nafi k'arfin inyi kishi da kowace irin jakar mace a duniya,,, saboda kishi dani masifa ne son mijina bala'i ne kallona ma jafa'i ne,,, saboda haka ba gargad'i nazo yi miki ba d'aukar ranki nazo yi in kasheki in kashe banza shegiyar bazawara! ".

Hankalin Lawiza yayi matuk'ar k'ololuwar tashi zuciyarta duk ta karaya,,, ko'ina a jikinta zufa ne ke tsattsafo mata saboda tsananin tashin hankalin da take cikinsa..

Ta fara zubar da hawayen bak'in ciki da afkawa cikin tarkon wahala,,, tace "dama ashe maganar da mutanen gari ke fad'a akanki gaskiya ne ke mayya ce! Na rok'eki dan girman Allah kiyimin rai kada ki kasheni,, idan har domin mijinki ne wlh na hak'ura dashi har abada dama saida nace

masa bazan auresa ba amma ya nacemin,, ashe da rabon zan fuskanci abinda yafi k'arfin tunani nabar miki mijinki wlh nabar miki mijinki! ".Ta sake fashewa da wani irin gigitaccen kuka mai tsuma zuciyar mai sauraro!.

"k'arya kike munafuka azurakar mace! Bazan tab'a yarda da maganarki ba domin ku 'yan Adam kunada sab'a alk'awari,,, kuma na riga nasha alwashin duk wadda ta kusanci mijina ko ta nuna tana son uban 'ya'yana hukuncin mace shine mutuwa! Mutuwa! Saboda haka wallahi bazan tab'a barinki a raye ba,,, kwanciyar kabari shi yafi dacewa dake daga yau zuwa kwana biyu ".Inji Talatu cikeda matuk'ar hasala sosai..

Lawiza tayi kuwwa da k'arfi ta sake fashewa da kukan bak'in ciki da k'uncin rayuwa,,,, jikinta babu abinda yakeyi sai makarkatar tsoro! Tashin hankali da rikicewa ne ya bayyana a fuskarta dak'yar cikin rud'ewa tace "na shiga uku ni Lawiza! Na kawo kaina gidan mutuwa ka cuceni Malam Mamman ka cuceni Malam Mamman,,,saboda saida nace bazan aureka domin matarka mayya ce amma kace sharrin mutane ne ba haka ba,,, gashi yanxu na jawowa kaina masifar da zata kashe batare da na cika burina ba,, iyayena ku yafemin 'yan uwana ku yafemin! ".Tana ta kukan bak'in ciki da takaicin rayuwa..

Inna Talatu tace "maganar banza da yofi lokaci yana tafiya,, saboda haka yanzu zanyi miki abinda ya kawoni in wuce gidan mijina wanda ni kad'ai ce matarsa a duniya! ".Hhhhhhhh ta fashe da dariya sosai sannan tayi amfani da hannunta,, tana ta surutai na sihiri wani bak'in abu ne ya bayyana a cikin hannun Inna Talatu MAYYA,, Lawiza babu abinda takeyi sai kukan bak'in ciki tana ja da baya da baya cikin firgici da tsananin tsoro! Ganin haka ne yasa ta fasa wani irin

uban kuwwa da k'arfi domin neman wanda zai iya kawo mata agajin gaggawa! Tace "kiyi hak'uri Talatu na tuba na biki ki yafemin wlh bazan sake ko kallon mijinki ba ".

Inna Talatu tace "kije kiyita kuwwa Lawiza babu wanda zai jiyo kuwwarki bale yazo ya ceceki,,, kafin nazo saida nayi wani mugun sihirin da ko kinyi kuwwa babu wanda zai jiki balantana yazo ya ceceki,, hmmmm gashi kuwa harna kwad'aitu da namanki!Saboda ina hango komai na kayan cikinki da k'asusuwanki kin tara mai sosai fa ".Kiyi hak'uri ko nawa kikeso zan  baki koda zan rasa duk abinda mahaifina ya mallaka zan baki,, nidai burina da fatana kada ki kasheni da duk abinda kike buk'ata zan b.... ".
Inna Talatu bata bari ta isuwa maganar da take sonyi ba,,, tayi amfani da hannunta ta kame mata kurwa ta sanya kurwar Lawiza cikin jakarta da sauri..

Tana kama kurwar Lawiza ta some tare da ruwan hawaye saman fuskarta,,, Inna Talatu ta ganin haka ta girgiza ta sake rikida ta koma mage,, tana komawa ta fice da sauri daga cikin gidan zuwa gidan mijinta..

*********************

***Washe gari da safe koda Lawiza ta tashi daga barci lafiya k'alau ta tashi kamar babu abinda ya faru da ita jiya,,, ci kin gidan kuwa har mutane sun fara taruwa 'yan uwa da abokan arzik'i sai ayyuka kawai sukeyi na 'yar garar da za'a kai gidan miji,,, babu abinda ke tashi sai surutu da ya yar mutane cikin gidan kowace ka kalli fuskarta farin ciki da murna kawai zaka hangowa,,,Inna Lawiza kamar ta zuba ruwa ak'asa tasha akan murna da matuk'ar farin ciki saboda mijin da Lawiza ta fara aure rasuwa yayi ya barta yaro guda mai suna Audu,,, haka dai suka cigaba da gudanar da komai cikin natsuwa da nishad'i sosai..

**Abangaren Malam Mamman shima sai shirye shiryen aurenshi kawai yakeyi cikeda matuk'ar farin ciki da nishad'i sosai,,,, ya gyara d'akin da zai saka Lawiza cikinsa harda saka sabon panting,,, yayi mata kayan lefe kala shida,, takalmi biyu,, hijabi biyu,, sark'a biyu da dai sauransu duk abinda kukasan ake sakawa a cikin lefe ya sanya mata bibbiyu,,, sannan ya aje a cikin d'akin dazai sakata Malam Mamman ya d'auki turmi biyu na daban yaba Inna Talatu ,,, tak'i amsa masa tareda wurga masa kayansa a saman fuska cikeda matuk'ar son tashin hankali! Tace "amshi tsiyarka Mamman! Saboda niba matsiyace ba inada suturata,,, kuma ba gidan matsiyata ka d'aukoni ba da suturata kaje ka aureni alokacin kuma kana fak'irinka! ".

Malam Mamman yace "sannu mai arzik'i har abada Talatu ba zaki tab'a yin hankali ba da karatun ta natsu ba,,, kibi duniya a sannu domin zata koya miki hankali wata rana kuma nasan zakiyi nadama anan gaba alokacin da nadamar da batada amfani,,, aure dai babu fashi sai nayi duk abinda zakiyi kiyi  mahaukaciya! ".

Inna Talatu tace "hmmm kaidai akeji Mamman wannan maganartaka baya tayar mini da hankali,, aurenka auren banza bai shafeni ba kana bari dai har a d'aura auren tukun kafin ka cikani da kurin banza ".

"aure ne kamar anyi an d'aura kina ji kina gani,, babu abinda zaki iya yi na maji dad'i sosai da kika k'i amsa saina k'ara ma Lawiza amaryarta matata farin cikin rayuwata ".Cewar Malam Mamman cikeda lalama..

Inna Talatu taja mugun tsoki mtsssss sannan tace "kodai bak'in cikin rayuwarka ce babu abinda ya dameni,,, da ran mai toka da mutuwarsa duk d'aya ne ga hankaka! Saboda haka kaga tafiyata inada aikin yi ".Inna Talatu tayi shigewarta cikin d'akinta batare data tsaya sakejin abinda zai fito daga cikin bakinsa.

"gara da kikayi wucewarki cikin d'akinki,, jahila wanda batasan muhimmancin miji ba da darajarsa ko kad'an ba ".Inji Mal. Mamman..

Allah ubangiji yaba mata mazaje nagari,, mazan kuma yabasu mataye nagari masu tsoron Allah da iya d'aukar dukkan lalurorinmu..

Ana saura kwana biyu a d'aura auren Lawiza da Malam Mamman,,, sai Lawiza ta tashi da wani mugun ciwon ciki sosai kuka kawai takeyi da murje murjen ciwo,, babu abinda takeyi sai danna cikinta tana kukan ciwo da nadamar rayuwa.
Lawiza ta kamayin shure shure da k'afarta sai birgima takeyi,, idanunta har wani k'ak'k'afewa da juyewa sukeyi akan rad'ad'i da zafin ciwo can naga ta fasa ihu da wani gigitaccen k'ara tayi kuwwa da k'arfi! Wani irin jini ne ke fita a cikin bakinta da hancinta gunduwa -gunduwa.

Innar Lawiza ce ta shek'o da gudu da saurinta,, tana shigowa cikin d'akin gabanta ya fad'i rasssss! Da taga abinda d'iyarta ke fissuwa hmmmm,,
tace "Lawiza mi ya sameki? Ina lillillahi wa inna ilaihirraji'un!.....

_Share&Comments_
[6/25, 6:20 PM] Mugiratmusa66: 🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥

🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥
*MAYYA CE*
🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥

*INTELLIGENT WRITER'S ASSOCIATION ®*✍🏻
_[Onward together]_

*Written by Mugirat Musa*

*DEDICATED TO SIS NAJER'ART*

_Bismillahir rahamanir rahim_

*PAGE 13*

Innar Lawiza tace" Lawiza mi ya sameki ?Ina lillillahi wa inna ilaihirraji'un!!! Na shiga uku na lalace ".Cikin kid'emewa da matuk'ar tashin hankali,, tana kuka mai cikeda bak'in ciki da k'uncin rayuwa..

Dak'yar Lawiza ta bud'i baki tace cikin matuk'ar zafi da rad'ad'in ciwo,, idanunta suna rufewa suna bud'ewa "kuyafemin Innata hak'ik'a nasan bayan mutuwata zaku kasance cikin bak'in ciki da k'uncin rayuwa,,, kuyi hak'uri wannan itace k'addarata kuma haka Allah yaso sannan na baki amanar Audu ki kulamin dashi ko bayan raina,,, ina son kisan cewa ashe matar Malam Mamman Talatu k'usurgumar mayya ce itace sanadin ciwona saboda haka ku kiyaye kanku Inn..... ".Ai bata k'arasa maganar ba idanunta suka k'ak'k'afe nan ta rasu ga jini duk ya b'ata jikinta,,, Innar Lawiza ta fasa gigitacciyar k'ara tayi kuwwa da k'arfi! Ta fashe da kukan tausayin kansu tana jijjigar gawar Lawiza tana cewa "dan Allah Lawiza ki tashi karki tafi ki barmu! Wallahi na yafe miki duniya da lahira,,,,babanki nasan shima zai yafe miki yau naga ta kaina wannan wa ce irin k'addara ce,, wannan wa ne irin rashin imani ne? 'yar tawa guda da nake kallo inyi farin ciki an kashemin ita,, Allah ya isa Talatu Allah ya isa Talatu!Bamu yafe miki ba duniya da lahira sai kinyi mummunan k'arshe a rayuwarki! Baban Lawiza baban Lawiza ".Ta sake fashewa da wani rikitaccen kuka tana ihu tana ifface iffacen kamar mahaukaciya sabon kamu,,, baban Lawiza da yanzu ya shigo cikin gidan ya shek'o da gudunsa,,, domin yaji kuka da kuwwa yana shiga cikin d'akin yaga Lawiza kwance cikin jini bata motsi,,, hankalinsa yayi matuk'ar tashi sosai gabansa sai fad'uwa yakeyi dummmmm! Yana ganin yadda duk Innar Lawiza ta yatsume da gigicewa yasan kila mai faruwa ta faru,,, yazo kusaga gawar Lawiza yana kallonta na wani lokaci can ya d'aga hannun Lawiza yana saki hannun ya fad'i alamar babu rai kenan,,, yasa hannunsa ya shafe mata idanu tareda furta "Ina lillahi wa inna ilaihirraji'un Allahumma ajirni fi musibati wa'akhalufni khari minha! Allah ubangiji ya jik'anki Lawiza da rahama ".

Yasa hannunsa ya jawota a jikinsa ya rungume Innar Lawiza yana lallashinta,,,, yana shafar mata baya alamar lallashi cikeda matuk'ar tausayin kansu,, sannan ya dubeta cikin raunin zuciya yace "kiyi hak'uri Innar Lawiza ubangijin da ya bamu Lawiza ya amshi abarsa,,, saboda haka muyi hak'uri Allah ubangiji ya jik'anta da rahama yasa ta huta ".

Innar Lawiza ta d'ago rinannu idanunta da suka rikid'e sukayi ja,,, ta saki wani sabon kuka tace "ya zamuyi baban Lawiza,,,shikenan ta tafi ta barmu ba zata dawo ba,,, shikenan bazan sake ganinta ba har abada,,, shikenan Audu ya zama bayada uwa,,, wannan wa ce irin rayuwa ce mai cikeda bak'in ciki da k'uncin rayuwa? ".

"kiyi hak'uri domin Allah mad'aukakin sarki da ya bamu Lawiza a matsayin d'iya yafimu sonta,, kuma komai na duniya sai mutum yayi hak'uri mutuwa dole ce dukkan mai rai saiya d'and'ani zafin mutuwa,,, to ya zamuyi idan ba hak'uri ba muma lokaci ne kawai muke jira Allah ubangiji yasa muyi k'yakk'yawan k'arshe,,, bari inje in sanarda mutane abinda yake faruwa ".Cewar baban Lawiza cikeda sanyin jiki da tsananin damuwa.

Ita dai Innar Lawiza babu abinda takeyi sai kukan bak'in ciki da mutuwar Lawiza,,, fuskarta tayi jawur majina da hawaye sun b'ata mata fuska yab'e yab'e zad tausayi,, baban Lawiza ya fita daga cikin gidan saboda ya sanar da mutane da 'yan uwa..

*********************

***Agidan Malam Mamman kuwa shi ne ya shiga cikin d'akin dazai saka Lawiza ya share tasss,,,,sannan ya gyara ko'ina cikin d'akin ya k'ulle d'akin ya fito ya zauna.

Yana zaune ne ya kira Gwamma ya aiketa domin ta siyo masa fura da nono,,,,tazo ya bata d'ari biyar ta siyo masa furar d'ari nonon d'ari,, ta amsa mashi ta wuce domin ta siyo masa furar.
Bayan wucewar Gwamma ne Inna Talatu ta fito daga cikin d'akinta itada Lawwali,,, ta dubi Malam Mamman tana wani yi masa rikitaccen murmushi cikin zuciyarta wani nishad'i ne da farin ciki ke wanzuwa a cikin zuciyarta,,, saboda tasan ta riga ta kashe Lawiza har abada! Sai dai

Mamman ya nemi wata matar badai Lawiza ba kuma muddin tana raye babushi babu k'ara aure,,, sannan tayi masa walak'antaccen kallo tace "Mamman angon Lawiza saura kwana biyu ka angwance ko? Ya kamata ka k'ara kawo kayayyakin miya wad'annan da ka kawo baya isa fa ".

Malam Mamman yace "hmmm lallai duniya akwai makirar mace,,, har kin sauko Talatu ko kuwa wani sabon salon munafurci ne kika b'ullo min dashi? ".

Inna Talatu ta banka mishi uwar harara tace "ban gane ba Mamman daga magana sai kace wani sabon salon munafurci na b'ullo dashi,,, ada fa aurenka ya dameni ayanzu ko matan duka garin nan zaka aure babu abinda ya dameni,, saboda haka kaje kayita harakarka ".

"aiko bakice babu ruwanki ba bashi zai hana in fasa abinda nayi niya ba,, saboda haka naji zan k'aro kayan miyan ko banason abin tashin hankali kada ki b'atamin ranar farin cikina ".Fad'ar Malam Mamman fuskarsa tana bayyanar da farin ciki sosai..

Inna Talatu tace "kaidai akeji anyima akuya wanka wannan kuma ba damuwata bace ".

Malam Mamman yace "ai naga alama Talatu kishiyar Lawiza,,, Lawiza amarya a gidan Malam Mamman kwana biyu kawai ya rage in zama ango,, mijin Talatu da Lawiza ".

Da yake Inna Talatu tasan abinda ta aikatawa Lawiza,, ta kasheta har abada bazai ganta ba tace "tabbas haka ne mijin mace biyu Talatu da Lawiza takawarka lafiya ango mijin amarya gaba haske baya k'amshi ".

Malam Mamman har cikin zuciyarsa yayi matuk'ar mamakin yadda Inna Talatu bata wani nuna damuwa ba ko tashin hankali ba,,, a fuskarta wani annuri ne ke bayyana a cikin fuskar Talatu babu abinda takeyi sai murmushi da dariya sosai..

Malam Mamman yayi murmushi yace "tabbas haka ne gaskiya zan baki goron kirarin da kikayimin nida amarya ".Yana rufe bakinsa saiga sallamar wani yaro tareda Gwamma domin kunsan ita batayin sallama,,, suna shigowa Mlam. Mamman ya amsa masa suka iso kusaga Malam Mamman,,,, Gwamma ta bashi sak'on ya amsa tayi tafiyarta wurin mahaifiyarta,,,, sannan yaro ya dubi Mal. Mamman yace "ana kiransa can gidansu Lawiza ".

Malam Mamman yace "lafiya dai mi yake faruwa ne yaro? "..

"lafiya k'alau baban Lawiza ke nemanka ".Cewar Yaron..

Malam Mamman yace "to yaro ".Sannan ya tashi tsaye ya bud'e d'akin daya gyara domin amaryarsa,,, ya aje furarsa da nonon aciki ya jawo d'akin ya kulle d'akin sannan ya juyo ya dubesa yace "muje zuwa ko to Talatu na fita zuwa can gidansu Lawiza ".

"lafiya dai Mamman mike faruwa? ".Cewar Inna Talatu MAYYA..

Malam Mamman yace "nima ban sani ba Talatu zanje can injiyo ko mike faruwa ".

Inna Talatu tace "saika dawo Mamman Allah yasa muji alkhairin Allah ".(Kamar da gaske har cikin zuciyarta alhali kuwa ran nan nata da zuciyarta fari fas akan murna da farin ciki sosai,,, saboda tasan mugun labari na mutuwar Lawiza za'a sanardashi).

Yace "Amin ya rabbi ".Suka sa kai sukayi wucewarsu ayayinda gaban Malam Mamman sai bugawa yakeyi da k'arfi! Rassssss,,, yaji duk jikinsa yayi matuk'ar sanyi wani k'ololon bak'in ciki ya tokare masa zuciya,,, shi kansa jikinsa ya bashi akwai mummunan al'amarin da yake faruwa...

Yana wucewa ne Inna Talatu ta bushe da mahaukaciyar dariya sosai! Sannan tace "Hhhhhhhhhhh haukar banza da yofi ni za'a kawowa iskanci da rainin wayo! Harda cemin shine mijin Talatu da Lawiza _(ta karkace baki tana kwaikwayon maganarsa cikeda matuk'ar raini)_ to yanzu zaka samu mummunan labarin da zai gigita rayuwarka da tunaninka,,, nasan saika kusa haukacewa da d'imaucewa kuma wlh ko ya nemi wata mata itama kasheta zanyi,,,saboda ni bazan tab'a zaunawa da kishiya ba niba wawuyar mace bace kamar sauran mata,,, ko waye yace zaija dani rabonsa wahala!".

Lawwali da Gwamma wasarsu kawai sukeyi,,, suna kuwwace-kuwwace suna dariya sosai..

¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤

¤¤¤Koda su Malam Mamman suka isa gidansu Lawiza har anyima gawar Lawiza wanka da sallah,,,,suna isa aka fito da gawar Lawiza za'a kaita makwancinta .
Suna zuwa Malam Mamman yaji gabansa ya k'ara bugawa da k'arfi dummmmm!Ya dubi baban Lawiza yace masa "Sani wa ye ya rasu? Ina lillahi wa inna ilaihirraji'un ".Gabansa yana fad'uwa da sauri da sauri zuciyarsa tana bugawa!.

Sani yace "saidai muyi hak'uri Allah ya amshi ran Lawiza ayau da rana Malam Mamman ".

Gaban Mamman ya bada dummmmm zuciyarsa ta girgiza hankalinsa yayi k'ololuwar tashi sosai! Har wani duhu duhu ya fara gani akan tashin hankali da rikicewa,,, ai kuwa nan da nan ya fad'i k'asa ya some mutanen dake wurin suka saka salati atare! Mutane hud'u suka kamashi suka shigardashi cikin gidan Malam Sani mahaifin Lawiza.

Sauran mutanen dake rik'e da gawar Lawiza cikin makara suka wuce da gawarta zuwa gidanta na gaskiya..

*Allahu Akbar! Duniya kenan wata rana za'a wayi gari duk babu mu a cikinta...*

¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤

***Suna dawowa daga wurin kai Lawiza gidanta na gaskiya mutane suka taru suna zaman makoki,,, 'yan uwan Sani dana matarsa suke karb'ar gaisuwa kowa ka gani ya zauna jugum yayi shiru yana jimami da damuwa.

Acan cikin gidan Mal. Sani kuma bayan an watsawa Malam Mamman ruwa ya farfad'o daga suman da yayi,, cikin mutuwar jiki da damuwa Malam Sani yace "kayi hak'uri Mamman Allah ya k'addara Lawiza ba matarka bace tun farko,,, sannan ubangijin da ya bamu Lawiza ya amshi abarsa alokacin da yaso ya kuma gadama saidai muyi hak'uri mu bita da addu'a,,, shi kad'ai take buk'ata ".

Innar Lawiza tace "tabbas haka ne gaskiya babu yadda zamuyi haka Allah ya k'addara,,, lokacinta ne yayi kuma bawa bai isa ya gujewa mutuwa ba,,, saboda haka hak'uri zamuyi muma ba zamu wuce lokacinmu ba ".

Malam Mamman ya juyo ya kallesu idanunsa sunyi jawur,,, jijiyoyin kansa sun tashi rud'u rud'u sannan yace "haka ne Sani nagode sosai da kulawarku akaina,, Allah ubangiji ya jik'anta yasa ta huta mu kuma idn tamu tazo yasa mu cika da imani ".

Suka ce "Amin ".Atare da juna.

Malam Mamman ya tashi tsaye yana musu kallon tausayi da jimami sosai,, yace musu shi zai wuce gida,, Malam Sani ya tashi domin yayi masa rakiya zuwa waje tare da bashi hak'uri da maganganu masu sanyi,,, shidai Mamman jijjiga kansa kawai yakeyi yana saurarensa.......

_Share&Comments_
[6/25, 7:51 PM] Mugiratmusa66: 🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥
*MAYYA CE*
🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥

*INTELLIGENT WRITER'S ASSOCIATION ®*✍🏻
_[Onward together]_

*Written by Mugirat Musa*

*DEDICATED TO SIS NAJER'ART*

_Bismillahir rahamanir rahim_

*PAGE 14*

Shidai Malam Mamman jijjiga kansa kawai yakeyi yana saurarensa cikeda matuk'ar sanyin jiki,,, can dai bayan Malam Sani ya gama yi masa nasiha mai ratsa jiki,,,, bayan ya gama ne sukayi sallama da juna cikeda rashin jin dad'i da  jimamin mutuwar Lawiza....

¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤

Malam Mamman ya shigo cikin gidan da sallama cikin sanyin jiki,,, Inna Talatu tana cikin d'akinta amma tanajin muryar Malam Mamman ne ta fito da saurinta tana kallonsa..
Malam Mamman ya zauna ak'ofar d'akinsa yayi tagumi cikeda sanyin jiki,,, yanayinsa ya nuna yana cikin damuwa da bak'in ciki Inna Talatu ta matso kusa gareshi cikin munafurci da k'ulle-k'ullen makirci,,, ta canza yanayin fuskarta daga farin ciki xuwa zullumi kamar ta damu da damuwarsa,,, tagumi yayi yayi shiru kamar ba Malam Mamman ba sarkin kiza-kiza,,, Inna Talatu tasa hannunta ta jaye hannun Malam Mamman domin son taji gulma kuma ta tabbatar ta kashe Lawiza ko kuwa da sauran aiki agabanta,, kunsan mace duk munin halinta ta iya munafurci da makirci idan tanason taji tsegumi ko gulma.
Ta dubi Malam Mamman zuciyar nan tata fara fass amma afuskarta kamar tana tausayinsa,,, tace "haba Mamman ka daina tagumi babu k'yawo,,,, sannan naga yanayin fuskarka ya canza mi yake damunka,,, mi yake faruwa? ".

Malam Mamman ya d'ago idanunsa wad'anda suka fara canzawa daga launin fari zuwa ja,,,, ya bud'i baki muryarsa tana rawa yace "Talatu dole in shiga cikin bak'in ciki da k'uncin rayuwa saboda mummunan k'addarar da ta sameni,,, ya zanyi da rayuwata,,, wannan wa ce irin k'addara ce mai cikeda bak'in ciki da takaici? ".

"ban gane ba Mamman abinda yake faruwa,,, ya kamata ka sanardani mi ke faruwa? Kayimin bayani dallah dallah yadda zan gane bawai kazo kayi tagumi ba ".Inji Talatu MAYYA cikeda matuk'ar makirci da munafurcinta..

Malam Mamman ya daure yace "Talatu Allah yayima Lawiza rasuwa a yau da rana,,,, kiran da kikaga akayimin d'azu alokacin ne koda na isa za'a kaita makwancinta na gaskiya,,,, ina cikin matuk'ar damuwa Talatu ina son Lawiza domin ta nunamin k'auna amma ubangijin da ya fimu sonta ya karb'i abarsa,,, ya zanyi ne yanzu? ".

Hak'ik'a maganar Malam Mamman ta k'ona ran Inna Talatu,,, amma da yake ta iya kissa da kisisina da munafurci bata nuna masa ba,,, kuma tasan burinta ya cika saboda ta k'ara tabbatarwa Lawiza ta mutu tabar duniya har abada!.

Ta dubeshi cikin munafurci tace "Ayyah Allah sarki duniya kenan! Allah ubangiji ya jik'anta da rahama yasa ta huta mu kuma yasa muyi k'yakk'yawan k'arshe,,,, amma agaskiya Mamman banji dad'in faruwar wannan mummunan al'amarin ba,,, amma ya muka iya lokacinta ne yayi,,,, kayi hak'uri Mamman Allah yana tareda masu hak'uri sannan zaka samu wata matar ka aura insha Allahu ".

Malam Mamman ya dubeta yana mamakin kalamanta sosai,,, shi kansa yasan Talatu batada tausayi ko imani amma ji yadda take masa nasiha kamar ta k'warai,,,,,,, amma da yake bayason ya fara zarginta yasa yayi saurin kauda wannan magana gaskiya.

¤¤¤Malam Mamman yace "tabbas haka ne amma ina cikin damuwa,,, sannan mantawa da Lawiza alokaci guda abu ne mai matuk'ar wahala sosai,,, amma bazan tab'a mantawa da Lawiza ba acikin rayuwata ba har abada ".

"haka ne baidace kayi saurin mantawa da ita ba,,,, idan Allah ya bani ciki muka samu d'iya mace sunan Lawiza za'a saka mata saboda k'aunar da kakeyi mata,,,, amma ka daure ka rage yawan damuwa saboda kada kamu da wata cutar hak'urin dai shi ne yafi dacewa ".Cewar Inna Talatu.

Malam Mamman yace "eh mana maganarki haka take nagode sosai da kulawarki gareni,,,

kuma idan Allah ya yarda zan rage sa damuwa acikin raina ".

Inna Talatu tace"da kam yafi Mamman karka damu ai dole in tausaya maka,,, saboda anzama d'aya tuntuni "...

Inna Talatu ta cigaba da bashi maganganu masu dad'i,,, da nasihohi masu ratsa zuciya da jini..

*** **** *** *****

*BAYAN WATA SHIDA*

••••Bayan watanni shida abubuwa da dama sun faru,,, ciki kuwa harda kamun kurwar da Inna Talatu keyi tana cinyewa ko ta mayarda kurwar kaza,, rago,, tunkiya,, bunsuru da dai sauran dabbobin dake cikin duniya to mayyu suna iya komawa kowace irin halittar dabbar da suka gadama.
Inna Talatu ta addabi mutanen gari itada sauran mayyu,,, babu abinda sukeyi sai kashe rayuka da cin naman mutane,,, mutanen gari duk sun tsorata da kid'emewa akan mayyu idan suka hangosu daga nesa,,, kowane mutum ko mace zai iya cikawa wandonsa ko bujensa iska k'afa mi naci ban baki ba! Mutane kowa sai kaffa kaffa yake da d'iyansa saboda gudun kada su had'u da mayyu su lamshe musu kurwar d'iya ko mata.
Idan matar aure ce tana kaffa kaffa da mijinta domin kada mai afkuwa ta afka musu,,, amma duk da hakan basu tsira ba domin har gida ake zuwa a lamshe musu kurwa ,,,saidai kaga mutum ya fad'i k'asa rikcham! Idan yana tsaye idan kuma zaune yake sai aga mutum ya fara aman jini yana murk'usu,, can ya fara shure shuren mutuwa yana kakarin mutuwa nan da nan ya rasu! Akwashi gawar mutum ankaishi mak'abarta! Haka abubuwan suke faruwa cikeda matuk'ar tashin hankali da rikicewa .

Rayuwar garin ta zamo cikin rashin kwanciyar hankali da rashin natsuwa,,, saboda akodayaushe akowane lokaci mutum za'a iya kame masa kurwa a cinye ya mutu! Shiyasa mutane basuda natsuwa ko walwala.

***Ab'angarensu Hassi kuwa bayan rasuwar mijinta Lado,,, sukaje itada Mariya ta tayata zaman idda domin ta d'ebe mata kewar Lado da mutanen gida.

Alokacin ne Hassi duk ta rame tayi bak'i akan tunanin mijinta,,, wata rana har kuka takeyi saboda tunani da zullumi,,,alokacin idan kaga Hassi saita baka matuk'ar tausayi haka Mariya zata kama ta tana kuka ,,,tayi mata nasihohi masu sanyi tareda da bata hak'uri akan lamarin rayuwa,,, haka al'amarin nasu ya cigaba da tafiya hartayi watanni hud'u da kwana goma kenan,,, sannan ta fita daga takaba tayi wanka fes tayi kamar ba ita ba tareda sanya sabuwar sutura.

Bayan wani lokacin ne akayi rabon gado sannan Hassi itada Mariya suka koma gidansu da zama,,,, al'amarin nasu dai komai cikin tausayawa Na'ima da Hassi suke yinsa daga Innarta har babanta babu maison b'acin ranta,,, duk abinda take so shi sukeyi mata babu shakka,,, shiyasa Na'ima takeyin sagarci da shagwab'arta babu mai takura mata ko hantararta.

Anan ne wata rana Hassi Allah ya kawo mata miji nagari mai tsananin k'aunarta tsakani da Allah ya aureta,, sunansa Iliya ba saurayi bane yanada matarsa Dije da yara uku mace biyu namiji d'aya,,, haka dai akayi auren cikin wadatar zuci da rufin asiri sosai,,, aka kaita gidan mijinta sukayi zamansu lafiya da Dije.

Da yake Dije mace ce mai halin dattako da karamci,,, kirki da sanin ya kamata shiyasa zamansu ya zamo abin sha'awa da burgewa,, babu gulma ko tsegumi balantana haukan kishin da bayada k'yau ko misali..

*****    ******** ******

Macijiya ce naga ta fito daga cikin gidan Malam Mamman cikeda da saurinta kamar iska,,, ta kama tafiya ta nufi wata hanya mai yawan hakukuwa da itatuwa.
Abin mamaki macijiyar tana tafiya tana waige waige kamar mutum,,, can naga ta nufi cikin sark'ak'k'iya da duhun ciyawa ga k'oramai agefen daji,,, ga itatuwa dogaye manya -manya  a ko'ina cikin k'usurgumin dajin baka iya hango tsawon dajin da girmansa saboda yawansa.

Macijiyar tayi ta tafiya tana ratsa hakukuwa da kuma k'oramai tana wucewa,,, tana kawowa wurin wani rami mai matuk'ar zurfi da ban tsoro wata irin guguwa ce da bak'in hayak'i ne suka game wurin nan da nan fass fasss fasss! Tass tass tass saboda tsananin tashin hankali da bala'i! Abin yakai tsawon minti ashirin sannan ya tsaya cak ya daina,,, saiga wata irin mahaukaciyar dariya ta bayyana b'ut akayi fitar burgu acikin ramin kamar walk'iya,,, nan da nan wata irin guguwa mai k'arfi ta zagaye wurin cikeda sihiri da tsafi! Babu abinda ke tashi cikin guguwar sai kukan namun daji da muryar mutane,,, can dai guguwar ta daina yawo a doron k'asa.

Wani irin murgujejen k'aton mutum ya bayyana tsulut kamar aljani,,, kallo d'aya nayi masa amma kamar inyi amai saboda halittarsa babu k'yawon gani,, domin ido d'aya garesa atsakiyar kai ga kuma k'aho biyu agefen dama da hagu duk jikinsa gashi ne zago zago kamar rago,,

halshensa yakai tsawon k'afar mutum mai tsawo hak'oransa sunada tsini kamar wuk'a,,, fatarsa bak'ik'irin kamar gawayi. Ya dubi macijiyar da babban murya mara dad'in saurare yace "yake Talatu ki koma zuwa ainahin siffarki ".

Ai bai rufe baki ba Inna Talatu ta girgiza sannan ta rikid'e zuwa ainahin siffarta ta mutum,,,, ta dubi boka LOK'ORO tace "ya kai wannan k'urgumin boka mai babban matsayi a cikin duniya,,, ina mik'o gaisuwata da girmamawa agareka,,, tsawon rai da shahara sun tabbata agareka ".

Boka LOK'ORO ya bushe da mahaukaciyar dariya,, dariyarsa da muryarsa bibbiyu take fitowa dajin ya gauraye gaba d'aya yana tanbal tanbal kamar  zai kife a cikin k'asa !Yace "godiya nake da gaisuwar ban girma amma inason ki sani Mamman mijinki yana nan yana neman wata budurwa fara ce tass mai suna Salima da aure,,, yana yawan zuwa wurinta fira yau zai sanardake yana neman aurenta ance ya turo magabatansa,,, saboda haka ki iya takonki domin gujewa afkawa cikin wahala da nadama! 'Yarki Gwamma zata gajeki a wurin maita zata shahara cikin maita da mugunta iri iri daban daban,,, Lawwali bazai gajeki ba saboda halinsu yasha banbanci dana Gwamma ".

Inna Talatu ta bushe da dariya sosai tace "nagode sosai babban boka LOK'ORO aikinka yana k'yawo sosai,,, nayi farin ciki sosai 'yata zata gajeni amma ko Lawwali bai gajeni ba babu komai boka,, sannan ni auren Mamman bai dameni ba domin cinye namanta zanyi ta mutu har lahira alokaci guda! ".

Boka LOK'ORO yace "aikinki yana k'yau shiyasa nake k'ara sonki saboda bakida imani bale tausayi,,, saboda ni banason haraka da mai tausayi da sanyin hali sannan idan zaki dawo kizo da Gwamma domin ta saba da aljannunmu tun yanzu,,, kafin ta zamo shahararriyar MAYYA gagararriya! ".

"zanzo da ita yah mai girma boka LOK'ORO, ".Cewar Inna Talatu cikeda matuk'ar farin ciki .

Boka LOK'ORO yace "to Talatuwa Innar Gwamma ki tafi zuwa gidanki cikin farin ciki da nishad'i sosai,, duk abinda kika sama gaba kece zakiyi nasara ki kashe kowa kici naman kowa! ".Yana gama fad'ar wannan magana ya b'ace b'at kamar k'iftawa da bismillah,, kamar kuma  wata halitta bata tab'a zama a wurin ba.

Inna Talatu tana ganin boka ya b'ace itama ta girgiza sannan ta rikid'a ta koma tsuntsuwa,,, ta tashi sama ta lulluk'a a cikin  sararin samaniya,,, tana ta gudun bala'i da masifaffen saurinta.......

_Share&Comments_
[6/25, 8:12 PM] Mugiratmusa66: 🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥
*MAYYA CE*
🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥

*INTELLIGENT WRITER'S ASSOCIATION ®*✍🏻
_[Onward together]_

*Written by Mugirat Musa*

*DEDICATED TO SIS NAJER'ART*

_Bismillahir rahamanir rahim_

*PAGE 15*

Tana ta gudun bala'i da masifaffen saurinta kamar walk'iya ce ta gifto ta wuce da sauri,,,,,abin akwai ban mamaki da matuk'ar al'ajabi  akan tsuntsuwar wato Inna Talatu MAYYA...

Haka dai ta cigaba da tafiya har ta iso bayan gidan Malam Mamman,,, abayan gidan akwai hakukuwa da yawa tana sauka ta k'ara girgiza da k'arfi,,, sannan ta rikid'a zuwa ainahin siffarta ta dawo mutum sannu a hankali,,,, tana dawowa siffarta ta fito daga cikin hakin ta nufi cikin gidan Malam Mamman,,, tana shiga cikin gidan ta isko Lawwali wasa kawai yakeyi ita kuma Gwamma tana cikin d'akin Innarta tana kwana..

Lawwali ya dubi Innarsa yace "Inna sannu da zuwa ".

Inna Talatu tace "yauwa Lawwali ina Gwamma take ne? ".

"tana d'aki tana kwana Inna,,,, sannan da kika fita da safe Gwamma tayi tafiyarta yawon banza da neman magana ".Inji Lawwali cikeda dad'in baki.

Inna Talatu tace "ya isa bashi na tambayeka ba,,, babu ruwanka da sha'anin Gwamma saboda haka ka rabani da surutunka na banza ".

Lawwali yace "to Innarmu na daina fa ".

Suna surutu saiga sallamar Malam Mamman ya shigo cikin gidan,,, Lawwali ne ya amsa masa sallamarsa yana yi masa sannu da zuwa,,,, Mamman ya amsa tareda sa mishi albarka Inna Talatu tayi masa sannu da zuwa,,, ya dubi Talatu sannan ya amsa gaisuwar da tayi masa...

Malam Mamman yayi gyaran murya,, tareda ajiyar zuciya yace "ina son magana dake Talatu ".

"ina saurarenka Mamman ".Inji Inna Talatu cikeda natsuwa,,, ta mayarda hankalinta kacokam wurinsa tana kallonsa.

Malam Mamman yace "da farko dai kinsan dai aure nufin Allah ne shine ke k'addara abu tun ranar gini ranar zane,,, saboda haka na nemi auren wata yarinya mai suna Salima har gidansu sun yarjemin in turo magabatana asaka rana,,, shi ne nace bari in sanardake abinda ke faruwa,,, saboda kada kiji abin daga sama zan tura iyayena gobe asaka sati biyu ad'aura auren,,,, shine nace bari in sanardake ko akwai shawarar da zaki bani ?".

Inna Talatu ta dubesa duba na munafurci da k'ulle-k'ullen makirci,,, tace "Alhmdlilah agaskiya na tayaka murna da farin ciki sosai,,, Allah ubangiji ya gwada mana lokacin biki lafiya musha bidiri mu dargwaji kaji,,,, ai shiyasa akeson mutum komai ya samesa yayi hak'uri da juriya domin babu abinda yakeda tabbas a rayuwa,,,, komai kaga ya samu bawa to muk'addari ne daga Allah ".

"tabbas haka ne maganarki gaskiya Talatu komai na duniya yanada farko yanada k'arshe,,,, saboda haka ki gayamin abinda ya kamata asiyo kafin biki na dangane da abinci da sauran abubuwan buk'ata ".Inji Malam Mamman cikeda matuk'ar farin ciki da nishad'i sosai,,, saboda shi azatonsa Inna Talatu yanzu ta sauko kuma ta gyara halayyarta,,, daga mugun hali zuwa k'yakk'yawar d'abi'a,,, baisan wannan yana daga cikin tarkon makircinta ba da munafurci irin na Inna Talatu MAYYA ba ".

Inna Talatu tayi murmushin da iyakarsa a leb'en bakinta baikai zuci ba,,, sannan tayi wata wawuyar ajiyar zuciya tace "mi kakeci na baka na zuba ka bari har lokacin biki ya k'ara k'arasowa mana,,, bakada matsala indai nice matarka Mamman aure ne kamar kayishi ".

"tooo.. Too bakomi uwargidana sarautar mata kece Innar Gwamma da Lawwali,,,, kece haske gidan Malam Mamman ".Cewar Malam Mamman cikeda zolaya da jin dad'i..

Inna Talatu tace "a'aaa wannan kirarin duk ni kad'ai naji dad'i matuk'a,,, mijin Talatu angon Salima babansu Gwamma da Lawwali ".

Hak'ik'a Malam Mamman yaji dad'i sosai da kirarin da Inna Talatu tayi masa,,, akan farin ciki ya ciro d'ari biyar daga cikin aljihunsa ya bata k'yauta,,, ta amshe kud'in tana zaginsa tareda da tsine masa a cikin zuciyarta.
Wata irin tsanarsa ce ta k'ara ninkuwa da kishinsa a cikin zuciyarta,,, ta fad'a cikin zuciyarta

"lallai Mamman zaka tafka babban kuskure a rayuwarka,,, zakasan ni babu mai tabani ya kwana lafiya in kashe mutum ya mutu har lahira ba'a bakin komai yake gareni ba! Amma da sannu zakasan ko wa ce ce ni Talatu idan ma ka gano ni *MAYYA CE* naga kanason ka kawomin tangard'a sai in kasheka! ".Da yaga tayi shiru na wani lokaci,, Malam Mamman ya tab'a Inna Talatu .

Yace "lafiya dai Talatu ya naga kinyi shiru kina tunani? ".

"lafiya k'alau wlh farin ciki ne yayimin yawa sosai,, shiyasa kaga nayi shiru ina tunani nagode sosai da wannan k'yautar daka bani mijina Allah ubangiji ya k'ara bud'i na alkhairi ".Cewar Inna Talatu tana dariyar yak'e da baikai zuci ba..

Malam Mamman yaji dad'in addu'arta matuk'a yayi murmushi yace "amin amin Talatu Allah ubangiji yabarmu tare har abada ".

Inna Talatu tace "amin amin Mamman ".

**Suka cigaba da firarsu cike da tsananin jin dad'i da nishad'i,, saboda shi Malam Mamman agaskiya yaji dad'in sauyawar Inna Talatu har cikin zuciyarsa,, bai kawo zarginta ba ko wani mugun zato akan taba ya yarda da ita ne da zuciya d'aya,,,amma baisan ita munafukar Allah ba haka bane a cikin zuciyarta ba,,, tana nan tana binsa da mugun nufi da k'ulle k'ullen makirci da sharri..

¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤

***Awashe gari da misalin k'arfe hud'u da rabi 4:30pm na yamma magabatan Malam Mamman ya tura can gidansu Salima.
Anyi musu tarba ta musamman da nuna karamci da dattako,,, hak'ik'a iyayen Salima mutanen k'warai ne da sukasan mutunci da sanin ya kamata,,, komai cikin sauk'i da wadatar zuci akayisa ansa sati biyu aranar juma'a za'a d'aura auren Malam Mamman da Salima,,, sun baro gidan suna masu farin ciki da murna sosai akan yadda aka tarbesu hannu bibbiyu cikin sakin fuska da fara'a.

Haka dai abubuwan suke tafiya cikeda zalunci da cin amana,, Inna Talatu taje da Gwamma wurin boka LOK'ORO har ya bama Gwamma maganin maita! Itama ta zama k'usurgumar mayya,,, uwarta Talatu ta kama kurwar mutane ta cinye ita Gwamma ta kama ta cinye.

Saboda tsabar shahara da gunguma a wurin Gwamma ita idan ta kama kurwar mutane ko gasawa batayi,,, sai dai taci naman d'anye hakanan batare da ta gasa ba,,, yaro komai k'ank'antarsa Gwamma tana kameshi mishi inwa (Shadow) ta cinye batare da b'ata lokaci ba.

Ana nan kwatsam!Ana saura kwana d'aya auren? Malam Mamman da Salima,, aka wayi gari itama ta mutu irin mutuwar Lawiza alal hak'ik'a awannan rana iyayenta da 'yan uwanta sun shiga cikin matuk'ar tashin hankali da rikicewa! Kowa awannan rana idan ka ganesu sai sun baka tausayi saboda mahaifiyar Salima har yassuwa zane tayi ta ruga da gudu ta haukace! Saboda tsananin bak'in ciki da b'acin rai sannan kuma ita kad'aice ke gareta amatsayi 'ya a duniya.

Mutanen gari 'yan uwa da abokan arzik'i suka bita da gudu,,, domin su kamota suka babbazu cikin daji suna nemanta,,, sunbi lungu da sak'o na daji har suka gaji amma ko ma kamada ita basu gani ba ganin mutane da yawa daga cikinsu sun galabaita yasa dole suka juyo sukayo cikin gari gidajensu .

Haka dai aka cigaba da cigiyarta da nemanta amma shiru babu wani labari,, asanadiyar haka ne shima baban Salima ya kamu da ciwon zuciya mai tsanani sai dai atayardashi a kwantar dashi,,, abubuwan dai babu dad'in ji balantana saurare sun faru mutane sun k'ara tsoracewa

akan al'amarin mayyu,,, saboda kamasu kawai sukeyi suna canyewa jariri ma ko jaririya tun suna cikin cikin mahaifiya ake kamasu acinye,,,wannan lamarin da gaske yana faruwa ni Mugirat na gani da idanuna azahirin gaskiya bawai labari kawai aka bani ba.

*Azahirin gaskiya ta'adancin mayyu ya wuce duk wani tunaninku mutane.*.

Malam Mamman da yaji labarin mutuwar Salima saida ya fad'i ya suma,, sannan daga baya ya farfad'o saboda matuk'ar damuwa da bak'in ciki saida ya kwanta matsananciyar rashin lafiya sosai,,, duk yayi bak'i ya rame sosai Inna Talatu ke jinyarsa cikeda matuk'ar munafurci tana lallashinsa tareda basa hak'uri,,,idan kaga yadda take kula dashi da tarairayar miji saika rantse da Allah batada masaniya akan komai,,, amma awurin nan muguwa ce azzaluma batada tausayi da tauhidi ko kad'an,,, ita fa arayuwarta bata yarda da k'addara ba indai akan kishiya ce da cikar burinta.

_Agurguje please._

Bayan wasu kwanaki Malam Mamman ya warke garau ya cigaba da harakokinsa,,, tafiya tayi tafiya Malam ya nemi wata mai suna Jummai da aure itama dai ana sauran kwana d'aya da

auren ta rasu!.
Sai da Malam Mamman ya nemi mata d'aid'aya har guda bakwai suna mutuwa,, sauran matan sune Karima, Labiba,, Nuratu,, Ummu,,, Lantana,, Falmata,,, Laraba,, Zainabu,,, duk garin gaba d'aya ya d'auka Inna Talatu *MAYYA CE* saboda alokacin basusan Gwamma ta fara maita ba .

Suka zama abin gudu da tsoro a cikin garin gaba d'aya,, babu mai zuwa inda take daga 'yan uwan Malam Mamman har nata kowa gudun ceton ransa yakeyi,,, ko ahanya ne aka tsinkayo Inna Talatu daga nesa sai kaga kowa ya watse domin ceton ransa,,, tun Malam Mamman bai fara yarda da maganar mutane fa har yazo ya fara yarda da maganarsu,,,aiko arana nan ne yayi mata mugun bugu sosai yana zaginta.

Ya dawo kamar ba Mamman ba yana yi mata walak'anci da rainin wayo iri iri daban daban,, shi kanshi alokacin wani tsanar Inna Talatu ne ya dirar masa a zuciya,, yanason ya saketa amma yana ganin idan yayi haka bai dace ba .

Ganin irin abubuwan da Malam Mamman keyi mata na walak'anci da duka sosai,, tabbas taga alamar idan batayiwa abin tufkar hanci da wuri ba zai iya tona mata asiri cikin mutane.

Nan da nan batare da b'ata lokaci ba Inna Talatu ta kama kurwar Malam Mamman,, ta mayarda ita zakara ta cinye d'anye bata tsaya gasawa ba to aranar saida taci kusan fara goma zama guda bayan ta Malam Mamman cikon na goma .

Ina lillillahi wa inna ilaihirraji'un!!! Washe gari da safe mutanen gari suka shiga cikin matsananciyar tashin hankali da bala'i babu abinda sukeyi sai kuka da ifface ifface ,,saboda bayan Mamman mutum tara ne suka rasu alokaci guda idan kayi duba zuwa ga jama'a zakaga mutane idanunsu jawur,,, fuska duk ta kumbura sosai bak'in ciki duk ya bayyana a fuskokinsu k'arara,, haka dai akayi jimami da bak'in cikin rasuwarsu Malam Mamman kowa ya watse.

Ganin da Lawwali yayi mahaifiyarsa ta kashe masa mahaifi! Yasa ya tashi tun kafin ayi sallar asuba ya gudu ya koma wurin k'annen mahaifinsa Labbo,, aka wayi gari Inna Talatu ta nemi Lawwali sama da k'asa ta rasa........

_Share&Comments_
[6/28, 1:56 PM] Mugiratmusa66: 🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥
*MAYYA CE*
🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥

*INTELLIGENT WRITER'S ASSOCIATION ®*✍🏻
_[Onward together]_

*Written by Mugirat Musa*

*DEDICATED TO SIS NAJER'ART*

_Bismillahir rahamanir rahim_

*PAGE 16*

Inna Talatu ta nemi Lawwali sama da k'asa ta rasa a cikin gidan,,, nan da nan hankalinta yayi k'ololuwar tashi cikin kid'ima da fargaba,, haka dai ta daure ta cigaba da harakokinta na cin

naman mutane,, Gwamma itama ba baya wurin kamun inwar kurwar mutane tana cinyewa d'anye ba babu tausayi ko rahama acikin zuciyarta ko kad'an,,,mutane sai k'ara tsoracewa da katsewa akan lamarin mayyu sukeyi...

**Inna Talatu ce da Gwamma zaune suna tattaunawa akan yau,,, wa ne gari zasuje kamun inwar kurwar mutane suje can batare da b'ata lokaci ba,, Inna Talatu ce ta dubi Gwamma tace "Gwamma har yanzu bakijin labarin ina Lawwali yaje ya b'oye ba,, acikin garin nan wai?".Gwamma ta karkace baki tace "Inna ayau da dare da naje kamun inwar kurwar mutane,,, na ganshi acan gidan baba Labbo yana b'oya saboda  kada ki ganshi wai ".Inna Talatu ta bushe da dariya sosai tace "hmm to ai ko ya gudu ya b'oye can bai tsira ba,, saboda idan inason inci naman jikinsa abu ne mafi sauk'i a wajena ".

Gwamma tace "nima naga wautarshi Inna ai kamun inwar Lawwali shan ruwa ma yafisa wuya sosai,, abinda ya aikata rashin wayo ne babba ".

Inna Talatu tace "yaje yayi tayi fa sannan ina son inja miki kunne ki rik'e wannan haraka ta maita hannu bibbiyu,,, saboda muddin kinayinta babu mai rainaki cikin mutane kowa shakkunki zai dinga yi,,, domin inason ki shahara da gunguma fiyedani inason duniya tasan da zamanki ".

Gwamma tace "zanyi iya bakin k'ok'arina kuma zan kasance mai biyayya ga boka LOK'ORO ,,har sai burinmu ya cika Inna bana wasa a cikin wannan sana'ar gado wato maita !"

"zaki ko shahara sosai da zama gagararriya acikin mutane da aljannu,,, babu wanda ya isa ya tab'aki ".Cewar Inna Talatu cikeda matuk'ar farin ciki da murna sosai..

Gwamma tace "naji dad'i sosai Inna dazan shahara a duniya ".

Inna Talatu tace "ba zakiji dad'i sosai ba sai nan gaba kad'an,, idan shahararki ta bayyana a cikin wannan gari ".

Gwamma tace "to Innata ta kaina".

Haka dai suka cigaba da shawarwari ta yadda zasu b'ullowa al'amarin kamun inwar kurwar mutane,, da kuma yadda zasu gudanar da komai cikin sauk'i....

¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤

*BAYAN SHEKARA BIYAR*

**Abubuwa da dama sun faru acikin wad'annan shekarun da suka wuce,, ciki kuwa harda kamun kurwar mutane dasu Inna Talatu keyi suna cinyewa,, domin abin nasu yayi tsamari sosai sun hana shak'at da jin dad'i a cikin gari,, mutum bayada halin ya fito daga cikin gidansa ya dad'e yana a cikin kasuwa face sun kamesa,, ganin sun addabi rayuwar mutane yasa kowa yake addu'ar Allah ubangiji ya kawo k'arshen Inna Talatu MAYYA.
Saboda har yanzu basusan Gwamma ta zama k'usurgumar *MAYYA CE* shahararra a wurin mugunta da cin naman mutane,, domin ayanzu tanada shekara goma sha takwas Lawwali kuwa sha shida,, tamafi Inna Talatu mugunta saboda ita har naman aljannu ci takeyi saboda ta shahara da gunguma akan maita! Tana alak'a da dodanni wurin abokanka,,, batada tsoro ko shakku uban kowa duk abinda takeso shi takeyi.

Ganin da mutane sukayi kashe rayukan da akeyi agarin nan yayi yawa,, yasa dole suka fara takon sak'a da Inna Talatu sukayita d'ana mata tarko tana tsalkewa,,, domin duk abinda sukeyi

tana ganinsu cikin tsafinta,,, ganin abinda suke mata yayi yawa sosai.

Yasa dole wata rana da misalin k'arfe 10:00am na safe,,, bayan sunyi karin safe itada Gwamma tace mata zataje can wurin boka LOK'ORO,, ta tsaya ta fake gida yanzu zataje ta dawo,,, Gwamma ta nuna mata babu matsala saita dawo.
Inna Talatu ta shirya sannan ta saka kai tayi wucewarta zuwa wurin boka LOK'ORO..

********************

Inna Talatu ta girgiza ta rikid'a ta koma kaza sannan ta kama hanyar zuwa cikin k'usurgumin daji mai duwatsu,, dajin da boka LOK'ORO ke rayuwa acikinsa na tsawon shekaru,,, tana isa inda yake ta girgiza sannan ta rikid'a zuwa siffarta ta ainahi,,, wata irin mahaukaciyar guguwa ce ta ratso kusa gareta tana girgizawa da zagayarta na wani lokaci kad'an,, can dai komai ya tsaya cak guguwar ta daina yawo ta girgiza sannan ta rikid'a ta koma boka LOK'ORO,, idanunsa sunyi jawur kamar barkono jijiyoyin kansa sun tashi rud'u rud'u halittar yanayin jikinsa duk ya chanza,, ya bud'i baki yace mata "nasan mi yake tafe dake Talatu,, amma ki sake gayamin da bakinki saboda wak'a abakin mai ita yafi dad'i ".

"ya maigirma boka LOK'ORO abubuwa da dama sun faru acikin wannan lokacin,,, mutane yanzu so suke su kasheni har abada,, sunyi d'anamin tarkuna har sun gaji ina tsallakewa,, ka sanardani ta yadda zan k'ara kare kaina".Inji Inna Talatu cikeda matuk'ar sanyin jiki.

Tana gama fad'in wannan maganar boka LOK'ORO ya bushe da mahaukaciyar dariya sosai,, wanda sanadiyyar hakan saida k'asa ta kama rawa yace"Talatu babu wani taimakon dazanyi miki domin alk'alami ya riga ya bushe,, mutuwarki ta kusantoki! Ajalinki yana zuwa agareki kwananki ya kusa k'arewa ".

Hankalin Inna Talatu ya d'unguma sosai zuciyarta sai bugawa takeyi da k'arfi da k'arfi,, rayuwarta idan har tayi dubu to ta b'aci sosai,, ta d'ago idanunta jawur tace "boka LOK'ORO wa ye zai kasheni sannan ya zamo ajalina? ".

"Sala mafarauci k'anen baban Lado shine zai kasheki! Amma ba'a cikin sauk'i zai kasheki ba 'yarki Gwamma itama ta kashesa,,, sannan abin yazo ya zamar musu gaba mai tsananin gaske itada Ummaru d'an Sala mafarauci,,kinga kuwa bakida damuwa domin ak'alla ko kinyi k'aranci kinci naman mutane fiyeda dubu 'yarki Gwamma taci d'ari ".Inji boka LOK'ORO yana dariyar mugunta da rashin tausayi!.

Inna Talatu ta bushe da dariya sosai sannan tace "hak'ik'a nayi matuk'ar farin ciki da wannan maganar taka boka LOK'ORO,,, aini burina ya cika koda ya kasheni saboda 'yata ta zamo shahararriyar *MAYYA CE* gagararriya acikin mutane da aljannu,, saboda haka banida fargaba ko shakku akanta ".

Boka LOK'ORO yace mata "tabbas haka ne Talatu ,,,ki tafi zuwa gidanki na barki lafiya ".

Yana gama fad'ar wannan magana ya b'ace b'at kamar bai tab'a wanzuwa a wurin ba,,, Inna Talatu tana ganin boka LOK'ORO ya tafi itama ta rikid'a ta zamo kaza ta k'ara gaba domin zuwa gida...

¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤

Inna Talatu ta koma gidanta ta cigaba da harakokinta itada Gwamma,, amma bata sanarda ita abinda boka LOK'ORO yace ba na gameda da mutuwarta ba,, saboda kada ta tayar mata da hankali.
Haka dai suka cigaba da rayuwarsu ta cin naman mutane da aljannu,,, cikeda matuk'ar kwanciyar hankali.

*BAYAN KWANA BIYU*

Bayan kwana biyu da faruwar magana atsakanin Inna Talatu da boka LOK'ORO,, bayan sun tashi da safe ne sun karya Inna Talatu tace ma Gwamma zataje daji domin ta d'ebo ganyayyakin da zata had'a wani magani,, Gwamma ta nuna mata babu matsala saita dawo,, Inna Talatu ta shirya tayi cikin k'urgumin daji Gwamma tana ganin ta fita itama tayi wurin kamun inwar kurwar mutane da satar kayan jama'a har cikin gida.

Inna Talatu ce ta shigo k'usurgumin daji mai duhu da yawan itatuwa,, yanada manyan duwatsu babu abinda ke tashi cikin dajin sai kukan tsuntsaye dana namun daji daga ganin halittar dajin kasan ba za'a rasa k'wamak'wanmai acikinsa ba.
Inna Talatu ta falfala da wani azababban gudu tana hawa saman wannan icce ta sauka tahau wancan bishiya,, haka dai ta kama yawo acikin dajin cikin tsafi da sihiri harta kallama had'a ganyayyakin da suka kawota,, ta juyo ta kama hanyar zuwa gida tana tafiya tana wak'e wak'enta.

Tayi nisa da tafiya kenan kwatsam! Sai taga Sala mafarauci agabanta kamar an jefosa,, hannunsa rik'eda kwari da bakansa ga kuma kibiyar halbi a d'ayan hannunsa,, jikkarsa ce goye abayansa ya kamo namun daji irinsu,, kura,, damo,, zomo da maciji.

Inna Talatu taja tayi tsaye turus gabanta sai bugawa yakeyi da sauri da sauri,, ta daure ta dubesa da jajayen idanunta b'acin rai k'arara ya bayyana akan fuskarta tace "kai Sala mafarauci lafiya ka taremin hanya,, mi kake nufi ne dani wai? ".

Sala mafarauci yace "kasheki zanyi Talatu saboda na dad'e ina d'ana miki tarko kina tsallakewa,, kin addabi mutanen gari da cin namansu saboda rashin imaninki ko jariri baki bari ba,, yau zan kawo k'arshen rayuwarki da zaluncinki! Ayau komai naki zai zama tarihi ".

"k'aryarka tasha k'arya Sala mafarauci ayau kaine zaka zama gawa bani ba,, sai dai uwarka ta haifi wani d'an idan tana raye amma ba kaiba,, ayau zaka d'and'ani d'acin mutuwa kwanciyar kabari shine yafi dacewa dakai a yanzu babu b'ata lokaci ".Inji Talatu cikeda matuk'ar tashin hankali da bala'i!.

Sala mafarauci yace "lallai kuwa ayau zakiyi nadamar duk abinda kika aikata saina banbance miki tsakanin k'arya da gaskiya! ".

Yana rufe bakinsa suka afkawa juna da azababban fad'a mai cike da rikitarwa da tashin hankali! Sara da suka kawai suke kaima juna cikin matuk'ar juriya da zafin nama.

Sala mafarauci yayita amfani da kwari da bakansa yana kaimata hari tana kaucewa,, sannan ya sareta da takobi ta kauce ya sari iska,,, kibiyarsa ya jefa mata ta kama kallon kibiyar da idanunta,, siririn haske ya bugi kibiyar ta juya domin ta chake Sala mafarauci ya kauce cikin zafin nama da juriya,, haka itama tayita jefo masa abubuwan sihiri irinsu wuta,, mashi,, wukake k'anana yana tsallake tarkonta.

Sun dad'e sosai suna azabtar da juna duk sun yiwa juna rauni sosai,, jini sai zuba yakeyi daga jikinsu akan fad'a,, amma duk da hakan basu daina ba Sala mafarauci ganin yayi Inna Talatu MAYYA tana batun kashesa a banza da yofi! Dole ya k'ara tattaro dauriya da hakurinsa ya sake afka mata cikin zafin nama ya sanya takobinsa yana ya sare mata kai ,,ai kuwa yana sare kan Inna Talatu jini ya kama bulbulowa kamar teku mai ambaliyar ruwa.

Wani irin rugugin tsawa ne ya bayyana dajin ya kama rawa da girgiza komai na cikinsa ya kama da wuta!,, Namun daji da tsuntsaye suka kama gudu domin ceton ransu,, alal hak'ik'a Sala mafarauci yaga abin mamaki da al'ajabi akan mutuwar Inna Talatu,, yasa hannunsa ya d'auki kan Inna Talatu da ya rabuda gangar jikinta yasa acikin jikkarsa ,,,yana sakawa wani k'aramin rami ya bayyana akusa da jinin jikin Inna Talatu,,, abin mamaki jinin ya dinga shiga cikin ramin har ya k'are tsab sannan gangar jikin Inna Talatu ta k'ara matsawa agefen bakin ramin.

Jinin yana k'are shiga ramin,,, ramin ya rufe kansa kamar bai tab'a bayyana a wurin ba,, Sala mafarauci ya juya zuwa hanyar zuwa gida yana tafiya yana tangad'i kamar mashayi,,, ga jinin Inna Talatu duk yayi masa faca faca a jiki ga wani zafi da rad'ad'in ciwon da taji masa sosai, akafarsa ta dama harta zaftari namansa babba yana shillo,,, dak'yar da bala'in dauriya ya kawo gidansa yana kawowa bakin garka ya fad'i k'asa rikcham ya some.

*Ab'angaren Gwamma kuwa bayan ta tafi wurin sace sacenta da kuma kamun inwar kurwar mutane,,, ta jima sosai a wurin kamun kurwar mutane sannan daga baya ta dawo gida tayi wanka tana jiran dawowar Inna Talatu.

Tana, zaune taji gabanta ya buga da k'arfi rassssss! Hankalinta yayi k'ololuwar tashi sosai zuciyarta tana yi mata k'una da tafasa sosai,,, haka kawai taji hawaye sun zubo daga idanunta jijiyoyin kanta sun mik'e tsaye rud'u rud'u halittar jikinta gaba d'aya ta chanza kammani,, safa da marwa kawai takeyi a cikin d'akin ita kanta ta rasa dalilin dayasa hankalinta yayi matuk'ar tashi sosai,, zuciyarta tana yi mata suya da tafasa sosai .......

_Share&Comments_

*Muje zuwa*💗
[6/28, 4:34 PM] Mugiratmusa66: 🍥🍥🍥🍥🍥🍥

🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥
*MAYYA CE*
🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥

*INTELLIGENT WRITER'S ASSOCIATION ®*✍🏻
_[Onward together]_

*Written by Mugirat Musa*

*DEDICATED TO SIS NAJER'ART*

_Bismillahir rahamanir rahim_

*PAGE 17*

Zuciyarta ta kama tafasa da k'una sosai,, hakan ne ya tabbatarwa Gwamma akwai mugun abun da zai faru marasa k'yau ko ya faru ,,,hankalinta ya sake tashi ta dubi agogo bango ganin har Inna Talatu MAYYA ta zarce kusan awa biyar awaje,,, bata dawo gida ba gashi ita kad'ai cikin gidan babu mai shigowa ko lek'owa ganin mahaifiyarta ta jima sosai a waje,,, yasa ta yanke shawarar bari ta bita can inda taje ta nemota ta dawo gida,,, sai da Gwamma tasa tsintsiya ta

k'ara sharen gidan sannan tayi musu girki domin tarbon dawowar mahaifiyarta,,, tana kamalla komai da komai ta sake wanka ta shirya cikin tufafinta masu dama dama,,tana shiryawa ta d'aga hannunta sama tana sambatu na tsafi da sihiri ta jima sosai tanayi,,,, saiga wani bak'in abu ya bayyana yana zagayarta can naga ya shige cikin jikinta ta rikid'a ta koma tsuntsuwa fara tass,,, tana komawa tsuntsuwar ta fito filin gida ta bud'e fikafikkanta ta tashi sama ta lulluk'a a cikin sararin samaniya tana ta matsiyacin gudu kamar aljana..

*********************

**Ab'angaren Sala mafarauci kuma bayan ya fad'i k'asa abakin k'ofar gidansa ya suma,,, duk jikinsa jinin Inna Talatu ne da kuma mugun raunin da taji masa hak'ik'a ya zubar da jini fiyeda kima,, ya dad'e kwance a k'asa babu wanda ya gifto can saiga Ummaru d'ansa da yayansa Labaran baban marigayi Lado sunzo bakin k'ofar gidan zasu shiga ciki,,, suna kawowa suka iske Sala mafarauci cikin jini kwance a k'asa ya suma,, sukaja suka tsaya,, baba Labaran ne yace "Subahanillah Ina lillahi wa inna ilaihirraji'un! Sala ne akwance cikin jini Ummaru,, ko namun daji ne sukayi masa haka amma bamu sani ba ".Ummaru yace "anyah kuwa baba namun daji basu tab'a yima babana ba wannan mugun ta'addanci ba,, akwai dai abinda yake faruwa dashi "."wannan abu ko da yayi masa rauni sosai agaskiya koma miye bayada imani ko kad'an,, Allah ubangiji dai yasa shi farfad'o daga suman da yayi ".Inji baba Labaran,, Ummaru yace "amin baba ai komai yayi zafi maganinsa Allah,,, Allah ubangiji ya bashi lafiya ".Baba Labaran yace "amin yanzu abinda za'a yi shine mu kamashi mu ida shigardashi cikin gida,, kada mutane su fara taruwa suna yad'a maganganun gulma da jita jita ".Ummaru yace "to baba maganarka haka take mutane lamarinsu sai Allah "."ai shine saboda kasan mutanen garin nan akwai shegen munafurci da gulma ce gulma ce ".Cewar baba Labaran.

Ummaru ya kama hannuwa baba Labaran ya kama k'afafuwansa,,, suka ciccib'esa dak'yar suka shigardashi cikin gida suna nishi mai d'aukeda wahala,, suna shigowa baba Labaran ya kira

Innar Ummaru da sauri ta fito daga cikin d'akinta,,, ya umurceta ta kawo tabarma a shimfid'a ma Sala mafarauci akwantar dashi,, jikinta yana rawa zuciyarta tana fad'uwa rasss saboda ganin halin da mijinta yake ciki na ciwo sosai,,, yasa tayi sauri ta d'auko tabarma da filo aka kwantar da Sala mafarauci samanta,, sannan aka aza kansa saman filo.
Inna Ummaru mai suna Yashe ta bud'i baki dak'yar cikin rashin kwanciyar hankali tace "yaya Labaran mi ya sami Sala,, a ina kuka tsintoshi? ".Baba Labaran ya dubeta duba na fahimta yace "kwantar da hankalinki Yashe anan muka tsinceshi bakin k'ofar gidan nan,, kwance a k'asa cikin ciwo ".Ummaru ya dubi mahaifiyarsa ganin irin tashin hankalin da ya bayyana a fuskarta,, dole yasa ya tausasa halshensa yace "eh ba wani babban abu bane Inna,,, rauni ne kawai yakeda ajikinsa kuma Insha Allahu zai warke ".Inna Yashe tace "Allah ya bashi lafiya ".Baba Labaran yace "amin Ummaru tashi ka shigar masa da jikkarsa cikin d'akin,, sannan kafin ka shigarda da ita fito da namun daji daya kamo saboda kada su lalace a banza,, wanda ya kamata asaisuwa sai asaisuwa wanda ya dace aci sai a ci".Inna Yashe tace "haka ne gaskiya ".To baba ".Cewar Ummaru alokacin ne ya mik'e tsaye yana fito da duk naman da Sala mafarauci ya kamo,, bayan ya gama fissuwa hmmmm yaji akwai abinda ya rage mai nauyi dunk'ulalle kamar k'wallo,, yana tab'awa yaji kamar kan wata dabba haka ne yasa ya fitar dakan Inna Talatu batare da yasan ko miye ba,,, yana fitarwa dukkansu idanunsu ya sauka ga kan Inna Talatu MAYYA,, ai saida suka zabura da k'arfi! Hankalinsu ya d'unguma sosai ita Inna Yashe fitsari ta saki a tsaye tareda rik'e bangon d'akinta 😂😂,,,su baba Labaran kuwa jikinsu sai rawa yakeyi da makarkatar tsoro,,, saboda shi yasan har abada bazai tab'a mantawa da Inna Talatu MAYYA ba domin jikinsa da zuciyarsa sun bashi itace sanadiyyar mutuwar Lado da sauran mutanen da ake kashewa! Ummaru ne yayi saurin mayarda kan Inna Talatu acikin jikka sannan yasa acikin d'akin Babansa ya kullesa aciki.
Sannan Ummaru ya dubesu yace "ina ganin kamar wannan abin bana damuwa bane,,, karku damu idan baba ya farfad'o zai sanardamu duk abinda ake ciki ko mike faruwa ".Baba Labaran ya dubesu yace "wannan abin haka yake amma akwai ban mamaki da al'ajabi acikinsa ".Inna Yashe dake wuru wuru da idanu alamar tsoro tace "muyi dai hak'uri har lokacin da Sala ya farfad'o zamuji duk abinda mukeson ji ".

"tabbas haka ne amma indai shi ya kashe Talatu MAYYA da kansa dole ne yaji jiki sosai,,, kuma Sala ya cika babban jarumi ".Inji baba Labaran.

Ummaru yace "babu shakka baba ne ya kashe Talatu mayya,,, shikenan mun rabuda azzaluma macuciya mai cin naman mutane ".

Inna Yashe tace "haka ne gaskiya maganarka Ummaru ".

Baba Labaran ne ya umurci Ummaru daya d'ebo ruwa a cikin randa masu sanyi,,, Ummaru yaje ya d'ebo ruwan ya kawo masa,,, yana kawon ruwan baba Labaran yayi doguwar addu'a acikin ruwan sannan ya watsawa Sala mafarauci ruwan ajikinsa.

Bayan jimawa kad'an sai naga Sala mafarauci yaja numfashi mai tsawo ya farfad'o daga suman da yayi,,, farin ciki da murna ya bayyana a zuk'atansu,,, shima kallonsu kawai yakeyi ya kasa magana akan rad'ad'i da zafin ciwo..

¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤

**Tsuntsuwar da Gwamma ta zama ta kama falfala gudu bata sauka a ko'ina ba sai cikin k'usurgumin dajin da aka kashe Inna Talatu,,, tana sauka ak'asa cikin dajin ta girgiza sannan ta rikid'a ta koma Gwamma,,, tana shiga cikin dajin lungu da sak'o gabas da yamma kudu da arewa tana neman Talatu MAYYA. Ta jima sosai tana nemanta harta galabaita akan yawo cikin dajin gashi hankalinta duk ya k'ara tashi,,, jikinta yayi matuk'ar sanyi da fargaba akan neman mahaifiyarta,, saida ta sake dawowa baya sannan taci karo da gawa kwance ak'asa duk naman jikinta tsutsotsi ne da tsuntsaye da namun daji sun yakuce naman,,, sunyi guntu guntu dashi wani mugun wari da d'oyi kawai ke fita daga cikin naman Inna Talatu.
Gwamma bata gane Innarta bace Talatu ba saida ta tsaya tana nazari da kallon gawar da k'yau,,, cikin natsuwa da yawan kallon gawar can taga guntun zanen Inna Talatu ak'asa yasshe,, ta duk'a har k'asa ta d'auko guntun zanen Inna Talatu sannan ta d'ebi jinin da yake ga naman tana karanta wasu d'alamisai na tsafi da sihiri ,,,,tana tayin wasu surutai marasa dad'in saurare da ji,,, ta jima tanayi saiga rugugin tsawa da hayak'i sun bayyana dajin gaba d'aya ya kama girgiza da tsawace tsawace mai muni! Jijiyoyin kanta sun mik'e tsaye zago zago,,, idanunta sunyi jawur kamar barkono can dai duk abinda ya faru a tsakanin Inna Talatu MAYYA da Sala mafarauci ya bayyana tana ganin komai,,, daga farkon fad'ansu har K'arshensa inda ya kashe mata mahaifiya..

Tana ganin abinda ya samu mahaifiyarta ta fasa gigitacciyar k'ara da kuwwa! Dajin gaba d'aya ya amsa kuwwarta wani irin mahaukacin kuka ne takeyi mai cikeda tashin hankali da bak'in cikin rayuwa,,, jikinta gaba d'aya bak'in hayak'i ne ke fita bakinta da kunnenta kumfa suke fitowa saboda b'acin rai k'arara dake cikin fuskarta,,, kammaninta gaba d'aya ta rikid'e zuwa babbar dodanniya! Ta bud'i baki dak'yar tace "na rantse da rayuwar mahaifiyata na rantse da boka LOK'ORO,, kuma na rantse da gadon maita da tsafi! Sala mafarauci kajama kanka masifa da bala'i,,, kajama kanka mutuwa wlh saina kasheka na kashe duk zuri'arka!Saina d'auki fansar jinin mahaifiyata duk mutane garin Gumi kaja musu bala'i da tashin hankali !Saina kashe duka

mutanen gari baki d'aya ".

Haka dai ta kama kururuwa da kuwwa mai cikeda tashin hankali da k'uncin rayuwa! Sannan daga baya ta dawo tsuntsuwa ta tashi sama cikin sararin samaniya tana masifar gudu harna tashin hankali,,,,, ta kamayin masifaffen gudu mai cikeda matuk'ar tashin hankali da rikicewa!.

**********************

**Ab'angaren Lawwali bayan ya gudu ya koma gidan baba Labbo da kuma matarsa Inna Tani,,, bayan ya koma gidan baba Labbo ya had'ashi da d'iyansa Ila da Sagiru yana koya musu aikin noma da kasuwanci,,, komai na gidan cikin kwanciyar hankali da natsuwa suke yinsa basu nunawa Lawwali banbanci ko kad'an,, hankalin Lawwali ya kwanta sosai har haske da k'iba ya k'ara yi,,, duk abinda suke buk'ata shi sukeci iyaka gwargwado suna cin mai k'yau susha mai k'yau cikin rufin asiri da wadatar zuci ,,,komai tare sukeyi shida su Sagiru suna tsananin k'aunar Lawwali da tausaya masa saboda irin muguwar  uwa da Allah ya bashi mara tsoron Allah da mugunta iri iri daban daban.

**Wata rana ne Inna Tani tana zaune da baba Labbo suna fira cikeda matuk'ar farin ciki da

fahimta sosai ,,,,Inna Tani ce ta dubi baba Labbo tace "agaskiya maigida ina matuk'ar tausayawa rayuwar Lawwali,, yanada halayyar k'warai da sanyin zuciya sannan gashi Allah ya had'asu da muguwar uwa MAYYA ".

"hmm Allah ya dai karemu daga shairin mugayen mutane,, amma lamarin Talatu kam sai a hankali duk ta rikita mutanen gari sai kashesu takeyi,,  harda d'an uwana mijinta ta kashe saboda kada yayi mata kishiya! ".Inji baba Labbo cikeda matuk'ar bak'in ciki da jimamin mutuwar Malam Mamman.

Inna Tani ta nisa sannan tace "ai ganin akan irin abubuwan da Inna Talatu keyi ne yasa Lawwali ya gudu ya barta itada  Gwamma su kad'ai aciki gida,,, Talatu kam tayi nisa bata jin kira saidai kayi hak'uri na kashe yaya Mamman da tayi,,, amma agaskiya ba zata tab'a k'arshe mai k'yau ba saitayi mutuwar walak'anci da tozarci! ".......

_Share&Comments_

*ku cigaba da bina fans*
[6/28, 4:35 PM] Mugiratmusa66: 🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥
*MAYYA CE*
🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥

*INTELLIGENT WRITER'S ASSOCIATION ®*✍🏻
_[Onward together]_

*Written by Mugirat Musa*

*DEDICATED TO SIS NAJER'ART*

_Bismillahir rahamanir rahim_

*PAGE 18*

Malam Labbo ya dubi Inna Tani yace mata "idan banyi hak'uri ba mi zanyi mata Tani,, ni kaina idan nayi mata wata maganar banza tana iya kasheni a banza da yofi! Ni wallahi tsoronta nakeji kamar ciwon ajali,,, saboda nasan wadda rashin imani da rashin tausayi yasa ta kashe mijinta akan *KISHIN JAHILCI* da hauka,,, to babu shakka uban kowa tana iya kashewa batare da wani fargaba ko tsoro ba,,, domin mayyu da kike ganinsu basuda d'igon imani da tausayi ko kad'an a cikin zuciyarsu ".

Inna Tani ta bushe da dariya sosai sannan tace "ashe dai maigida kana tsoron mutuwa wallahi! Nida so nayi ka tareta kace mata miyasa ta kashe maka d'an uwa,,, ka dai gane ka irin tsorata ta d'in nan kace zaka had'ata da hukuma ".😁😁

"wa! Ni idan kikaga an kaini cikin kabari kaini akayi bani nakai kaina ba,,, so kike ina zuwa ta dubeni da shegunan idanunta jawur kamar wuta ta kame mini kurwa ta lak'umeni aini duk abinda tayi alhakin mutane na nan bisan wuyanta,,, saboda haka ki rufamin asiri babu ruwana duk abinda zatayi taje tayi tayi duniya ce wanda baizo bama jiransa take ".Inji Labbo cikeda matuk'ar tsoron al'amarin Inna Talatu MAYYA.

Inna Talatu ta sake fashewa da dariyar k'eta harda rik'e ciki takeyi akan dariya,,, sai ta dubi Labbo sannan ta fashe da wata dariyar mugunta.

Can dai ta daure ta tsayar da dariyar ta karkace baki tace "kaini wasa nakeyi maka taya zance kaje mahalaka da hankalina,, halan so nake in zama bazawara ai nasan ko maza masu tashe da k'arfi da mazantaka tsoron tunkarar mayyu sukeyi,, balantana kaida ka kwana biyu Allah ya sawwak'a in tura uban 'ya'yana wurin annobar gari mai cin naman mutane ".

Labbo yace "aike bakisan wani abu ba,,, idan kikaga yadda maza da mata yara da manya suke gudu in suka hango mayyu yadda zasu cikama buje ko wandonsu iska da gudu,, to sai cikinki yayi ciwo akan dariya wlh ai ni abin na d'aure min kai yadda suke rikid'a su koma kowace irin halittar suka gadama ".

"ina ni ina tsayawa dariya kowa yanata kansa,, to kai maigida miye abin mamaki bayan kowa yasan tsafi da sihiri ne sukeyi suna komawa kowace irin halitta,, inda ma Gwamma kaje ka dawo da ita nan kada uwar ta koya mata mummunan dabi'a da halinta ".Inji Inna Tani tana dariyar mugunta k'asa k'asa kada Labbo ya jiyota.

Labbo ya harareta yace "ina ni ina raba uwa da d'iyarta babu ruwana wlh,, ai tasan da zamana tayi zamanta wurin mahaifiyarta amma ke na baki iznin ki fita kije ki dawo da ita wannan gida ".

Inna Tani tace "hmmmm wai mutuwa kenan! Ni ko uwatace ke maita gudunta zanyi saboda in

tsira da raina da lafiyata,,aini saboda tsorana ko muryar mayya naji saina saki fitsari a cikin wando 😂balantana har nakai kaina mahalaka ".

"to shine saboda kin mayardani wawa kike cewa inje ina ruwanki,, ai d'an uwana ne ta kashe ba naki ba to nabarta ga Allah ubangijin talikkai shi zaiyi mana hisabi a tsakaninmu ".Cewar Labbo ya muzurai da idanu alamar tsoro..

Inna Tani tace "kaini wasa nakeyi maka ai duk abinda zai cutar dakai sai inda k'arfina ya k'are,, bawai ince kaje gidan mutuwa ba ".

Labbo yayi murmushi yace "ai nasan wasa kike yimin matata,, uwar yarana banda tamkarki a cikin zuciyata ".Yana wani kashe mata idanu alamar soyayya. 😂

Inna Tani tayi masa kallon so tace "su Labbo kenan an tunada tsohuwar soyayyar da mukayi tunda dad'ewa sosai ".

"na tuna uwargida ran gida ".Inji Labbo.

Suka fashe da dariya tareda kallon juna suna murmushi,, daga ganin yadda suke gudanar da rayuwar aurensu akwai soyayya da k'auna mai k'arfi a tsakaninsu,,, firarsu kawai sukeyi cikeda matuk'ar farin ciki da kwanciyar hankali.

¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤

**Abangaren Sala mafarauci yana farfa'dowa daga suman da yayi,, Inna Yashe ta kawo masa ruwa da abinci da magani ya fara cin abinci sannu a hankali,, cikin yanayi na ciwo sosai baba Labaran da Ummaru suna zaune gefe suna kallonsa cikeda matuk'ar tausayawa sosai.

Ya cigaba da cin abinci bayan ya d'anci mai dama sannan yasha ruwa tareda maganin,, ya aje kofin gefe yana jan numfashi dak'yar,, su duka sukayi masa sannu ya amsa,, baba Labaran yaje ya d'auko garin magani na gargajiya Inna Yashe ta shafe duka jikin Sala mafarauci dashi maganin,, da maganin ya fara yi masa rad'ad'i da zafi sai naga Sala mafarauci yana runtse idanu tareda cije baki yana nishi sannu sannu.

Zuwa wani lokaci sai naga maganin duk ya game jikinsa gaba d'aya yana ratsa sassan jikinsa,, ga wani irin zufa dake tsiyaya cikin jikinsa can yaja doguwar ajiyar zuciya sannan yace "hmmm yau naga mutuwa ga filin wuri naga tashin hankalin da ban tab'a ganin irinsa a rayuwata ba,, nasha azaba da bak'ar wuyar da ban tab'a shan taba a cikin rayuwata,, lallai mayyu annoba ne kuma guba ne cikin al'ummarmu saboda suna kashemu a banza sannan su cinye namanmu a yofi,,, ban tab'a zaton rashin imani da rashin tausayin mayyu yakai haka ba sai yanzu da naga mutuwa a filin wuri k'iri k'iri ".

Baba Labaran yaja doguwar ajiyar zuciya sannan yace "hak'ik'a yau k'anena kaga tashin hankali,, kuma Allah yasa kanada tsawon rai domin Talatu ko cikin mayyu ba k'aramar mayya bace ba,,, sannan duk ta zamo shahararriyar *MAYYA CE* wadda ta gagari mutane da dama acikin wannan gari namu mai tarin albarka ".

Ummaru yace "abin ba'a cewa komai amma gaskiya sharrin mayyu da muguntarsu ya wuce tunanin duk wani d'an Adam,,, sabodasu sun riga sun fita daga cikin mutane sun zama mayyu haka suke ganin komai na jikin mutane,, kamar dai yadda kukasan k'warangwal (skeleton),, wasu ma idan suka kama mutum idan ya gagaresu aljannu suke mik'awa kurwarsa su kashesa! Saboda haka baba ka auna babban arzik'i da ka dawo da ranka ".

"mun godewa Allah ubangiji da ya bashi ikon kasheta da kuma dawowa da rai,, duk da yake shegiyar annobar duk ta jimasa raunika da yawa ga jini sai zuba yakeyi a d'azu ajikinsa ".Inji Inna Tani cikeda matuk'ar sanyin jiki da farin cikin mutuwar Talatu k'usurgumar mayya.

Baba Labaran yace "haka ne gaskiya maganarki mun gode Allah da farin cikin dawowarsa a raye gida,, amma muna son ka bamu labarin irin gwagwarmayar da kasha wurin kashe wannan mayyar Talatu ".

Sala mafarauci ya gyad'a kansa yace "yanzu kuwa zan baku labarin yadda abin ya kasance "......Ya kawo labarin komai duk abinda ya faru daga farko har k'arshe ya gaya musu,,, bai b'oye musu komai ba na irin abubuwan da suka faru a tsakaninsu da Inna Talatu,,, da kuma irin tsafe tsafen da ta kamayi tana rikid'a ta koma mutum,,, haka dai ya sanardasu komi bai b'oye ba..

Suka had'a baki wurin cewa "ina lillillahi wa inna ilaihirraji'un!!! "...

Haka dai suka cigaba da tattaunawa akan lamarin mayyu,,, da kuma irin cutarwar da sukeyi acikin al'ummar musulmai baki d'aya..

*Allah ubangiji ya kiyayemu*..

¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤

*BAYAN KWANA BIYU*

Bayan faruwar mutuwar Inna Talatu MAYYA duk labarin komai,,, da irin kisan walak'anci da Sala mafarauci yayi mata ya bazu ko'ina a cikin garin Gumi,,, ko'ina lungu da sak'o acikin garin kowa ka gani fuskarsa tana bayyanar da tsananin farin ciki da nishad'i mara misaltuwa.
Majalisar samari da ta dattijawa sai murna sukeyi suna mayarda labarin abinda ya faru ,,, saboda farin ciki da murna ji sukeyi kamar su goya Sala mafarauci abayansu,, sarki da dogaransa da kansu sukaje har gidan Sala mafarauci sukayi masa godiya tareda da bashi babbar k'yauta,, ya amsa yana cikin farin ciki da nishad'i sosai domin yanzu kam yaji sauk'i sosai a jikinsa,, sukayi masa sallama tareda musabaha da junansu cikin girmamawa,,, suka wuce zuwa gida..

Tsuntsuwar  bata sauka a ko'ina ba sai a cikin k'usurgumin dajin da boka LOK'ORO yake zaune,,, tana sauka ak'asa ta koma ainahin siffarta Gwamma,,, ta iske har boka LOK'ORO ya bayyana yana jiranta.

Ta dubesa da idanunta jawur kamar barkono,, b'acin rai da bak'in ciki ne suka bayyana k'arara

akan fuskarta,,, ga hawaye yab'e yab'e a fuskarta tace "boka LOK'ORO ya kashemin mahaifiyata ya zanyi da rayuwata boka?,,, na zamo marainiya banida uwa banida uba wallahi wallahi duk wanda yakeda sa hannu ko yayi farin ciki da mutuwar mahaifiyata,, duk saina kashesu! Gaba d'ayansu in yaso kowa ya d'and'ani zafin mutuwa da rashin uwa,,,gasu can sai walima sukeyi suna murna da farin cikin mutuwar Talatu MAYYA ".

Boka LOK'ORO yace "kiyi hak'uri Gwamma zaki d'auki fansar jinin mahaifiyarki,, yanzu nan zan k'ara miki k'arfin tsafi da sihiri wanda zaki iya yak'ar kowane mahaluki  a cikin duniya! ".

"ina son ka bani k'arfin sihirin da babu wanda zanji tsoronsa a cikin wannan duniyar mai cikeda bak'in ciki ".Inji Gwamma tana zubarda hawayen bak'in ciki da k'uncin mutuwar mahaifiyarta!.

Boka LOK'ORO ya bushe da mahaukaciyar dariya mai cikeda rugugin tsawa da bak'in hayak'i! Yace "yanzu kuwa zan baki sihirin da zaki kashe kowa kici naman kowa yadda kike so,,, sannan idan kika kashe Sala mafarauci ya mutu Ummaru d'ansa zaiyita farautarki kamar yadda sukeyin farautar namun daji! Saboda haka kiyi taka tsan- tsan da Ummaru domin shima hatsabibin yaro ne da zai gaji ubansa a farauta ".Yana gama fad'ar wannan magana ya dinga feso mata wani irin abu mai tsananin haske,,, shi kuma abin ya kama shiga cikin jikinta sosai yana kuma zagayarta da sauri da sauri!.

Hasken saida ya shige cikin jikinta tsab sannan komai ya dawo dai dai,,, "ki tafi gida Gwamma ki kashe duk wanda kike ra'ayi babu wanda ya isa ya hana ki sai Ummaru d'an Sala mafarauci,, saboda haka ki bishi a hankali sannu ki samu ki kawardashi a doron k'asa kafin ya zamo ajalinki! ".Yana kawo k'arshen maganarsa ya b'ace b'at kamar bai tab'a sauka a wurin ba.

"to mai girma boka LOK'ORO zanyi biyayya agareka matuk'ar ina raye,, sannan zanyi taka tsan-tsan da Ummaru d'an babban mak'iyina a duniya,, na rantse da girman tsafina saina kashe duka dangin Sala mafarauci muddin ina raye a cikin duniya! ".Inji Gwamma tana gama fad'ar wannan kalmar ta rikid'a ta koma tsuntsuwa,,, ta tashi sama tana masifaffen gudu a cikin gajimare,, tun ana hango tsuntsuwar har ya zamana ko hangota ba'ayi ta riga ta b'ace a cikin sararin samaniya..........

_Share&Comments_💜
[6/28, 6:03 PM] Mugiratmusa66: 🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥

🍥
*MAYYA CE*
🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥

*INTELLIGENT WRITER'S ASSOCIATION ®*✍🏻
_[Onward together]_

*Written by Mugirat Musa*

*DEDICATED TO SIS NAJER'ART*

_Bismillahir rahamanir rahim_

*PAGE 19*

Ta b'ace a cikin sararin samaniya tana masifaffen gudu harna tashin hankali,,, ta jima sosai tana gudu sannan ta kawo gida ta sauka a saman roofing na gidan,, sannan ta sauko a cikin tsakiyar gidan wanda ya zamo mallakinta ayanzu,,, bada jimawa ba ta rikid'a zuwa ainahin siffarta Gwamma tana mai bak'in ciki da takaicin yadda aka kashe mata mahaifiya zama guda,,, ta nufi randar ta d'ebo ruwa tayi wanka fes.
Sannan ta gama shiryawa taci abincin da ta girka tunda safe,,, sannan ta nufi wurin inda take aje kurwa mutane kusaga randa ta d'auko fa ru (grasshoppers) kusan shidda ta lak'umesu a cikin bakinta,, batareda ta tsaya gasawa ba aiko tana cinyesu duka sai wata irin kuwwa da kururuwar mutane kawai yake tashi! Gwamma ta rufe kunnuwanta domin kada ta kurumce ga wata irin iska da guguwa mai k'arfi dake zagayar gidan sosai,,, hankalinta kwance dayake tasan babu abinda zai iya tunkararta da fad'a ayanzu,,,bayan komai ya lafa ta tashi daga inda take zaune tanata huci da bak'in rai akan yanzu ta rasa kowa nata idan ba Lawwali ba,,, tasha

alwashin koda zatayi yawo tsirara sai taga bayan dangin Sala mafarauci  da zuri'arsu baki d'aya,,,saboda ya sanyata cikin bak'in cikin da har abada ba zata tab'a warkewa ba idan har bata kashesa ba,,, bata huce takaici ba sannan kuma masu murna da farin ciki da kuma masu yin walima akan mutuwar mahaifiyarta saita kashe musu mata ko d'iya,,, domin su d'and'ani irin kwatankwacin zafi da rad'ad'in da ta jiya a cikin zuciyarta,,,,bazata tab'a yafewa duk wanda yakeda sa hannun acikin mutuwar Inna Talatu MAYYA ba,,,,shiyasa yanzu taji zuciyarta tana k'una da tafasa sosai wani irin zugi da rad'ad'i ne zuciyarta,,, ga wani turirin bak'in ciki daya dafe mata kan zuciya wani abu takeji yana tokare mata saman k'irji kamar an aza mata dutse babba.

Can dai ta kwanta saman gadon Ummanta tana zubar da hawayen bak'in ciki da na rashin uwa,, ga wani zogi da zuciyarta keyi saboda damuwa,, haka dai tayi shiru tana tunanin rayuwarsu ta can baya itada mahaifiyarta Inna Talatu da mahaifinta Malam Mamman...

*********************

**Acan cikin gari kuwa bayan mutanen sun gama yin walima da cin abincin walimar ,,,kowa ya watse tareda kama gabansa,, saboda yanzu mutane sun saki jikinsu sai murna sukeyi da mutuwar Talatu MAYYA,, wasu ma har gidan Sala mafarauci suke zuwa suna yi masa gaisuwar ya jiki dana ban girma sannan ya d'auko kan Inna Talatu da ya fille ya nuna musu ,, saboda tsananin jarumtakar daya nuna da kuma k'ok'arin da yayi wurin kashe k'usurgumar mayya gagararriya irin Inna Talatu,,, wadda akan shahararta ba kowa ke iya fad'a mata maganar banza ba..

Ganin maitar tayi sauk'i k'warai bayan mutuwar Inna Talatu MAYYA,, yasa mutane suka saki jikinsu kowa ya cigaba da sha'aninsa da kuma kulada iyalinsa,,, kodayaushe mutum zai iya fitowa acikin tsakar dare batare da fargaba ba ko shakku ba,,, idan kaga yadda mutane suka dawo cikin natsuwarsu da walwalarsu sai kayi mamaki sosai,,, mutane suka cigaba da gudanar da rayuwarsu cikeda matuk'ar kwanciyar hankali da kuma gudanar da kasuwancinsu..

¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤

*BAYAN SATI GUDA*

Bayan sati d'aya da mutuwar Inna Talatu MAYYA,, Gwamma ta wartsake ta share maganar kashe Sala mafarauci saboda batason ayi saurin gano ta zamo shahararriyar mayya,,, domin tasan hakan ne zai iya tona mata asiri da wuri yasa mutane su ganota cewa ita d'in mayya ce,,, saboda haka ne taba zuciyarta hak'uri da dangana tana kula da duk wani motsi na Sala mafarauci,,, duk inda ya shiga akan idanun Gwamma yake tana hankalce dashi da duk wani motsinsa,, idan tari Sala mafarauci yayi akan idon Gwamma idan abinci yakeci akan idonta ne,, in tak'aice muku babu wani motsin da zaiyi ba'a kan idanun Gwamma ba..

**Washe gari da safe misalin k'arfe 9:30am na safe,, Gwamma ta tashi tunda tayi sallar asuba ta share gidan gaba d'aya tsab sannan ta aza ruwan zafi asaman murhu ta d'ibi na wanka,, sauran ta barsu domin ta had'a shayi mai kauri.

Bayan ta shiga wanka ne ta fito ta sanya doguwar rigarta,, sannan tazo kitchen ta juye sauran ruwan zafinta a kofi tana juyewa ta shige cikin d'akinta,, ta d'auko kayan shayi da biredi ta had'a shayinta mai kauri tana sha da biredi,, haka dai ta cigaba da cin abincinta cikin natsuwa harta kammala,, tana gamawa taje wurin murhun wuta ta d'auko fara biyar ta cinyesu zama guda,, saida kuwwar mutane da kururuwarsu ta bayyana na tsawon lokaci,, bayan komai ya lafa ta fito bakin k'ofar d'akinta ta shimfid'a tabarma ta zauna shiru tana nazari da tunanin lamarin duniya da zamantakewar rayuwa gaba d'aya..

Can dai da jimawa saiga sallamar baba Labbo ya shigo har cikin gidan batare da wani shamaki ba,, Gwamma ta tsura mishi jajayen idanunta tun kafin ya k'araso kusa gareta yana k'arasowa ya samu wuri ya zauna kusa ga Gwamma,, yana kallonta yana mai tsananin jin tausayinta saboda gata marainiya kuma d'iya mace ita kad'ai acikin gidan,,, dak'yar ta bud'i baki ta gaidashi ba domin ranta yaso ba ya amsa mata cikin sakin fuska da walwala.

Sannan ya dubeta cikin tausayawa da k'aunarta amatsayinta na d'iyar yayansa yace "Gwamma ya mukaji da hak'uri na rashin da mukayi? ".

Gwamma ta kauda kanta cikeda matuk'ar takaici da jin haushinsa,, tace "mun gode Allah ya zamuyi duk abinda Allah yayi mai k'yau ne ".

"haka ne 'yata inason kiyi hak'uri ki maida komai ba komai ba,,, Allah ubangiji da ya baki su

yaya Mamman da Talatu amatsayin iyayenki shine zai chanza miki da sauyi mafi alkhairi,, sannan ki sani dukkan mai rai mamaci ne kowa lokacinsa ne kawai yake jira,, burinmu dai Allah yasa mu cika da imani muna musulmai ".Inji baba Labbo cikeda matuk'ar tausayi da lallashi.

Nasihar nan da yakeyi mata saida taji an fama mata tsohon ciwon da ya riga yayi mata k'urji acikin ciki,,, ta d'ago rinannun idanunta jawur dasu tace "haka yake baba ".

Baba Labbo yace "saboda haka amatsayina na babanki k'ane ga mahaifinki Mamman,,nake umurtarki da ki dawo gidana da zama saboda bai dace ba kina yarinya budurwa kina zaman kanki ke d'aya acikin gida,,, bak'ya tsoron kada wani abu na cutarwa yazo ya cutardake ko yayi miki wata illa,, sannan akwai matasa masu shiga har cikin gidan mutane suna musu fyad'e da k'arfi da yaji,,, saboda haka ki tashi yanzu ki kwaso kayanki bazan bar gidan nan ba sai k'afata k'afarki ".

"to baba yanzu zan shiga cikin d'akin in had'o kayana saimu wuce zuwa gidanka ".Cewar Gwamma.

Baba Labbo yace "ina jiranki d'iyar albarka shiga ki had'o kayanki ".

Tace "to baba ".Ta tashi sannu kamar abin arzik'i ta shige cikin d'akinta,, tana shiga bada jimawa ba ta rikid'a ta koma macijiya mai kai biyu idanunta jawur kamar wuta bakin nan nata wargajeje gudan k'ato,,, macijiyar tayi zuruf zuruf ta fito wurin baba Labbo,, baba Labbo bai hankalta da macijiyar ba saida yaji ana lasar masa tafin k'afafuwa,,, naji yana cewa "wai wa ne irin k'waro ne ke lasarmin k'afafuwa ",,,yana gama magana yana juyowa idanunsa ya sauka akan macijiya,, ai kuwa ya zabura da k'arfi! Yana kuwwa sosai da kururuwar neman agajin mutane,, itama macijiyar tana ganin zai shek'a da gudu ta bisa da gudu tana fitar da halshenta.
Ai kuwa yana ganin ta biyosa ya k'ara gudu tareda k'ara rikicewa! Yana hawayen ganin mutuwa k'iri k'iri,,, ya kama zagayar filin gida saboda tsananin rikicewa da d'imaucewa! Babu abinda yakeyi sai zubar da hawayen tsoro,, macijiyar ta kama binsa harda hawa takeyi saman jikinsa tana k'ara tsoratardashi,, can naga baba Labbo ya buga wata gigitacciyar k'ara da kuwwa mai ban tsoro!.

Saiga kashi da fitsari tsuluttt tsuluttt tsuluttt sun fito daga cikin wandon baba Labbo,, ashe wai zawo yakeyi amma da yake yana cikin tsoro ne da firgici baisan yayi ba,, ya cigaba da zagayar gidan yana kukan bak'in ciki da takaici can ya bud'i baki yace"na tuba dan Allah kiyi hak'uri bansan Inna Talatu tabar miki mai gadinki bane,, nasha aradu bazan koma dawowa cikin gidan nan ba har abada,,, sai yaga macijiyar ta bushe da mahaukaciyar dariya tace "idan ka sake dawowa acikin gidan nan saboda ka tafi da Gwamma,, saina kasheka har abada! "."bazan ma koma dawowa ba kiyimin rai banason in mutu yanzu inbar iyalina ".Inji baba Labbo sai wari da d'oyin kashi da fitsari yakeyi. "Naji! Naji tsohon munafiki fita ka bani wuri,, kafin in chanza ra'ayina in kasheka a banza ".Cewar macijiyar cikeda matuk'ar hasala sosai,, ai kuwa baba Labbo ya shek'a da gudu saida ya buge kansa abango gidan ya fad'i k'asa d'immm! Sannan ya tashi da sauri ya falfala da gudun bala'i yana fesa zawo da fitsari,, babu abinda ke tashi sai b'urr b'urr b'urr yana gudun ceton ransa.

Tun yana gudun ceton ransa har ya kawo gungu samari ya wucesu da gudu,, suna lafiya lafiya Malam Labbo amma ina yayi nisa bayajin kira ganin haka ne yasa samarin suma kowa ya cikawa wandonsa iska suka shek'a da gudu ,,,suna biyar bayan Labbo.

Suna gudu har suka iso majalisar dattijawa suna firarsu cikin natsuwa ,,su Labbo sukayo cikinsu da gudu harda take cikin wani daga cikinsu sukayi yana kuwwa da k'arfi da kuka ,,,dattijawa

suka runtuma da gudu da babbar rigunansu harda wanda aka takawa ciki shima ya mik'e zumbur ya kama gudu da k'aton cikinsa kamar k'warya.

Haka dai suka kama gudu nan kamar ransu zai fita,, kowane daga cikinsu ka duba bakin rai bakin fama yake gudu!. Nishinsu da sawun takalminsu kawai ne ke tashi ruduuu ruduuu d'iiiiiiiii.

Maigari ne zaune da dogarawansa da sauran mutanen gari suna fira,, ga kwanonin tuwo nan da miya aje agefe rufe sannan ga ruwan yamin da aka kawowa Maigari domin ya kaiwa awakin matarsa,,, suna tsaka da firarsu saiga su Labbo da samari,, dattijawa sun shek'o da gudu sunyo cikinsu aikuwa aka d'unguje Maigari ya fad'a cikin kwanon tuwo shida wani dogarinsa,, ga hula da rawanin maigari agefe sai kuwwar zafin ciwo da neman agaji sukeyi shida dogarinsa,, d'ayan kuma ya fad'a cikin miya duk jikinsa ya b'aci sosai da ruwan miya shima sai kuwwa yakeyi yana murza idanu da laluben hanya saboda duk miyar ya shige masa acikin idanu.
Saura mutum uku suka fad'a cikin ruwan yami suna iyo dayake irin babbar roban nance wadda ke iya d'aukar mutane kusan hud'u,, sunsha ruwan yami sunyi tsamo tsamo suna kuwwar neman ceto da agajin gaggawa,, robar da taji nauyin bala'i ta fashe fasss suka kasa tashi a k'asa sai kuwwa sukeyi,, wad'anda suka tsere ko waiwayo su basayi sunata kansu! Wad'anda suka fad'a cikin ruwan yami suka tashi dak'yar suka kama Maigari duk ya k'one a hannu da fuska sai kuka yakeyi,, suka shigardashi cikin gidansa dayake a k'ofar gidan suke zama,, sauran kuwa daga baya mutanen gari ne suka ciccib'esu suka kai kowa gidansa..

*********************

Macijiyar ta koma mutum wato ainahin siffarta Gwamma sannan ta sake rikid'a ta koma kaza,,, ta fito daga cikin gidanta ta nufi gidan Sala mafarauci,, tana tafiya sannu sannu a hankali harta kawo bakin k'ofar gidan ta kalli k'ofar da idanunta wani farin haske ne ya fito daga idanunta ya bugi k'ofar ta bud'e kanta tayi zuruf zuruf ta shige cikin gidan Sala mafarauci da saurinta.........

_Share&Comments_
[7/2, 7:36 PM] Mugiratmusa66: 🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥
*MAYYA CE*
🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥

*INTELLIGENT WRITER'S ASSOCIATION ®*✍🏻
_[Onward together]_

*Written by Mugirat Musa*

*DEDICATED TO SIS NAJER'ART*

_Bismillahir rahamanir rahim_

*PAGE 20*

Ta shige cikin gidan Sala mafarauci da saurinta,, tana shiga bata tsaya b'ata lokaci ba sai cikin d'akin Sala mafarauci da Inna Yashe sunata barcin rana,, ashe kafin taxo itace tayi amfani da tsafinta ta sanyasu barcin rana,,, batareda b'ata lokaci ba Gwamma ta kamayin wasu surutai na tsafi ba'a jima saiga wata irin mahaukaciyar guguwa da k'arfi! Tana zagayarsu Inna Yashe na tsawon lokaci can naga guguwar gaba d'ayanta ta shige cikin jikinsu kaf,,, tana gama shigewa Gwamma mayya tayi amfani da sihiranta ta b'ace a cikin gidan baki d'aya kamar wani halitta bai tab'a wanzuwa a cikin gidan ba,,, ta barsu nan kwance suna barcin sihiri da tsafi..
Bayan wasu awanni saiga sallamar baba Labaran da Ummaru atare suka shigo cikin gidan,, bawai tare suke ba baba Labaran ya had'u da Ummaru ne a hanyar dawowa gida shine yace bari ya biyosa saboda ya k'ara ganin yadda jikin d'an uwansa yayi sauk'i sosai,, suna zuwa sukayi sallama basu  amsa ba baba Labaran ya umurci Ummaru daya shiga cikin d'akin yaga shin lafiya,,, Ummaru bai tsaya wasa ba ya shiga yana shiga ya tayar dasu daga barci yana cewa "baba lafiyarku k'alau kukeyin barcin rana? ".Suka kalli juna Sala mafarauci da Inna Yashe sunajin maganarsa amma sun kasa mayarda martani,, ganin haka ne yasa Ummaru ya sake tambayarsu sukayi shiru,, dalilin haka da sukayi ne yasa hankalin Ummaru ya d'unguma gabansa ya dinga bugawa da k'arfi dummmmm! Yaji wani irin d'aci da zafi a cikin zuciyarsa ga wani abu ya tokare masa mai nauyi a k'irjinsa,, can dai ya tattaro dauriya da hak'urinsa ya fito bakin k'ofa ya kira baba Labaran yace "masa baba kazo kaga wani abu ".To Ummaru ".Inji baba Labaran tareda shigowa cikin d'akin,, yana shiga shima saida gabansa ya bada rasssss! Yace "Sala lafiya naga kunyi shiru ne? ".Babu amsa ai kuwa baba Labaran da Ummaru suka dubi juna cikin tsoro da fargaba akan rashin maganarsu Inna Yashe.

Babu b'ata lokaci suka ga naman sassan jikin Sala mafarauci ya fara rabuwa filla filla,, kamar yadda kukasan ake raba sassan naman kaza idan za'a dafa misali k'afa daban kai daban bayanta da fiffikenta daban,, suka tsorace da rikicewa babu abinda ke tashi kuwwa da kururuwar Sala mafarauci cikeda matuk'ar zafi da rad'ad'in mutuwa,, ga jini sai bulbulowa yakeyi

kamar an yanke sa! Ummaru da baba Labaran suka fashe da wani irin matsiyacin kuka mai cikeda bak'in ciki da tashin hankali ,, ga Sala mafarauci da Inna Yashe suna cikin mayuwacin hali amma basuda ikon taimakonsu! Sala ya sake buga gigitacciyar k'ara namansa ya rabu ga kansa agefen d'aki sai hawaye suke fitowa daga cikin idanunsa! Inna Yashe itama ta buga wata irin kuwwa tana fisge -fisge da soshe soshe can ta fad'i k'asa d'immmmm naman jikinta ya rabu filla -filla kamar yadda na Sala mafarauci yayi,, abin babu k'yawon gani d'akin gaba d'aya ya garwaye da jininsu Inna Yashe!.
Baba Labaran da Ummaru suka rungume juna akan tsananin tashin hankali da firgicewa! Babu abinda sukeyi sai zubar hawayen bak'in ciki,,, sun rud'e sun d'imauce basu tab'a ganin tashin hankali ba kwatankwacin wannan ba,,, zuciyarsu sai rad'ad'i takeyi da tafasa sun kasa cewa komai balantana suje neman agajin mutane ko taimako akan rikicewa da gigicewa! Bayan sassan naman jikinsu Inna Yashe ya gama yin filla -filla kwatsam sai suka ga tsutsotsi k'anana suna yawo a cikin jinin da sassan jikinsu Sala mafarauci,, can taga tsutsotsin suna shiga cikin wata k'wara d'aya tsutsar ita kuma tana rikid'a tana k'ara girma,, suna gama shigewa gaba d'aya tsutsar ta koma guda wargajejiyar k'atanya,, tayi amfani da bakinta ta kama shan jinin da cin namansu Inna Yashe tana k'ara zama k'atuwa!Taci naman taci taci saida ta cinye naman da kuma shanye jinin kaf baki d'aya! Sannan ta dubisu baba Labaran ta dinga feso musu wuta tana bugunsu gefen hagu da dama tayi musu lik'is da matsiyacin duka,, babu abinda ke tashi sai kuwwarsu da kukansu idan zasu gudu tayi amfani da tsafinta ta mayardasu cikin d'akin, haka dai ta cigaba da gana musu azaba da uk'uba iri iri daban daban na tsananin zalunci da rashin tausayi! Idanunta sunyi jawur kamar barkono jijiyoyin tsutsar ya tashi rud'u rud'u acikin fuskar tsutsar ana hango fuskar Gwamma mayya yana yawo,, amma su basu lura ba saboda tashin hankali da bala'i! Kunsan jikin wanda ya kwana biyu basa d'aya dana tsoho sai naga baba Labaran ya kama shure shuren mutuwa! Yana kururuwar zafin ciwo gashi ji yakeyi kamar ana soka masa allura ko wuk'a a cikin jikinsa,, nan da nan naman jikinsa ya daskare yana yin gunduwa gunduwa ya mutu dis batare da b'ata lokaci ba!.

Ummaru yana ganin abinda ya faru da baba Labaran ya buga kuwwa da gigitacciyar k'ara da k'arfi! Ya tunkaro tsutsar domin yayi mata kisan gillah,, tsutsar tana ganin ya nufota ta hura masa wani abu acikin fuska ya shiga cikin idanunsa yana fara lalube tayi amfani da sihiranta ta jujiyashi a sama! Sannan ta nunasa da yatsa yaje ya bugi bangon d'akin gauuuuuu! Ya fad'i k'asa d'immmmm kansa ya fashe da jini sannan ya suma.

Tsutsar tana ganin irin rashin imani da zaluncin data aikata,, ta bushe da mahaukaciyar dariya tareda rikid'a zuwa ainahin siffarta Gwamma! Ta dubi Ummaru tareda da nunasa da yatsa tace"yanzu muka fara wasar ni da kai na rantse da jinin mahaifiyata baxan tab'a barin kaji dad'i a cikin rayuwarka ba! Kafin ka zamo ajalina saina cusa maka bak'in cikin da har abada ba zaka tab'a mantawa dani a rayuwarka ba! Zuri'arku saina kassarasu baki d'aya munafiki azzalumin ubanka Sala ya ja maka ,,,saboda haka ni babu ruwana da kowa laifin Sala mafarauci ya shafesa! ".

Tana gama fad'in wannan maganar ta girgiza sannan ta rikid'a,,, ta b'ace b'at daga cikin gidan Sala mafarauci,,, suui suuu suuuu kawai kakeji alokacin da ta b'ace.
Tana barin gidan saida taje gidajen mutane tana kashe musu mata da d'iya,,,,,,amma fa wad'anda sukayi walimar murna na mutuwar Inna Talatu MAYYA da kuma wad'anda sukayi farin ciki sosai akan mutuwarta! Duk saida ta bisu gida gida tana kashe d'iya da mata,, wannan ta kashe matarsa wannan ta kashe masa wancan ta kashe masa d'iya haka dai ta kamayi saida ta kashe kusan mutum ishirin gamidasu Sala mafarauci ishirin da uku! Ina lillahi wa inna ilaihirraji'un! Wannan masifa tayi yawa sosai,,, bayan ta kamalla kashe duk wanda ya dace ya d'and'ani zafin mutuwa! Ta b'ace b'at ta koma gidanta ko nace na iyayena,,, tana komawa gidan tayi wanka sannan ta dawo ta shirya domin ta kwanta kawai sai ganin mutum zaune tayi a saman gadonta yayi kwance rashe rashe,,, kallonta kawai yakeyi yana lasar baki dak'yar ta bud'a baki tace "wai Sule miyasa bakajin magana ne? Kace kana sona nace maka bana sonka to mi ye na bibiyata aduk inda naje ,,,,miyasa bakada lura ne kai aganinka iyayenka zasu bari ka aureni bayan sun san ni d'iyar mayya ce ".

"nidai nace ina sonki ba iyayena ba sannan nine zan zauna dake ba wasu ba,,, mi ye nayi miki kika tsaneni ko ganina bak'ya sonyi inzo wurinki? Ina sonki sosai babu wanda ya isa ya rabani dake Gwamma ni koda kece mayyar ba mahaifiyarki ba ina sonki a hakan ".Cewar Sule cikeda matuk'ar lallashi da dad'in baki.

Kalaman Sule sunyi matuk'ar tasiri a zuciyar Gwamma jikinta duk yayi mugun sanyi sosai,,, can ta nisa tace "bazaka tab'a gane matsalar tarayyarka dani sai nan gaba kad'an Sule,, ni nan da kake ganina rayuwata tana cikin matuk'ar hatsari akodayaushe akowane lokaci za'a iya kasheni! Amma ba komai na yarda da soyayyarka Sule na aminta ".

Sule yayi murmushi yace "nagode sosai da kika amshi soyayyata hannu bibbiyu ina sonki aduk yadda kike,,, sannan ai mutuwa dole ce kowa lokacinsa yake jira ".Ya fad'a shi bai gane inda maganar Gwamma ta dosa ba,, na cewa akwai lokacin da zaizo  akasheta ba.

Gwamma tace "babu damuwa Sule duk yadda kace haka za'a yi saboda bazaka tab'a gane manufar maganata ba ".

Yace mata "aiko ni nake gane inda maganarki ya dosa saboda k'auna da soyayyar da nake miki daban yake a cikin zuciyata ".

"da gaske na kuwa gode da soyayyarka agareni Sule ".Tace tareda d'auko man shafi ta fara shafawa a jikinta tana shafawa Sule ya matso kusa gareta gab da gab sunajin numfashin juna yace "babu godiya a tsakaninmu masoyiyata,, ya amshi manshafin daga hannunta ya cigaba da shafa mata jikinta tareda tab'a duk wasu gab'ob'i da sassan jikinta 'har wani lumshe idanu takeyi akan dad'i sosai sannan b'ata tsintsar kanta cikin irin wannan yanayi ba ya bita da shafe shafe duk ya kashe mata jiki,,, ai dayake tsakanin baligi namiji da baliga mace idan suka keb'e a tsakaninsu na uku d'insu shed'an ne nan da nan yasa hannunsa ya jaye mata zane suka afkawa juna suna lashe lashe da kisses,, ina ganin sun  sun fita cikin hayyacinsu naja k'afafuna nayi waje naja musu k'ofa.

Bayan wasu mintuna kad'an na jiyo ihu da kururuwar Gwamma tana kuka mai cike da zafi da rad'ad'in zama cikakkar mace,, hmmmm aikin gama ya gama Sule ya kwashi gararsa da jin d'adi.

¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤

Baba Labbo ne ya shigo aguje cikin gidansa da gudun bala'i duk jikinsa yayi faca faca da zawo da fitsari,,, yana shigowa ya d'unguje Inna Tani da sauri ya afka cikin d'akinsa garaffff garaffff garaffff ya rufe,, Inna Tani ta wintsilo k'asa bakinta ya fashe d'immmmm ta tashi tsaye tana share d'an jinin da ya fito daga cikin bakinta,,
Inna Tani ta bushe da mahaukaciyar dariya sosai harda rik'e ciki akan dariya tace "maigida lafiyarka k'alau kuwa,, ka fito waje ka gayamin abinda ya faru dakai bayan kaje d'auko Gwamma,, ko acan ne aka baka tsoro ne? ".Tace tanata k'yalk'yalar dariya sosai........
[7/2, 7:56 PM] Mugiratmusa66: 🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥
*MAYYA CE*
🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥

*INTELLIGENT WRITER'S ASSOCIATION ®*✍🏻
_[Onward together]_

*Written by Mugirat Musa*

*DEDICATED TO SIS NAJER'ART*

_Bismillahir rahamanir rahim_

*PAGE 21*

Inna Tani ta bushe da mahaukaciyar dariya sosai tace "maigida lafiyarka k'alau kuwa,,, ka fito waje ka gayamin abinda ya faru dakai bayan kaje d'auko Gwamma,,, ko acan ne aka baka tsoro ne? ".Ta k'yalk'yale da dariyar mugunta.

Baba Labbo ya lek'o ta tagar d'akin yana wuru wuru da idanu,,, da nishin wahala alamar yasha wuya sosai da yake fitarwa yace "wallahi Tani danaje can d'auko Gwamma domin ta dawo gidan nan,,, bayan munyi magana da Gwamma ta shiga cikin d'akin saboda ta d'auko kayanta mu wuce ,,,tana shiga kafin ta fito daga cikin d'akin macijiya ta fito daga cikin d'akin Gwamma tana ta tsoratani!........ ".Ya kawo labarin komai ya sanar da ita duk irin abubuwan da ya faru a cikin gidan Gwamma,,,, ya sanar da ita babu abinda ya b'oye mata dangane da irin tashin hankali da bala'in daya gani...

Yana gama fad'ar wannan magana,,, bayan ya kawo k'arshen magana Inna Tani ta kama salati tana wuru wuru da idanunta cikeda matuk'ar tsorata da kid'emewa! "Ina lillahi wa inna ilaihirraji'un!!! Lallai kaga tashin hankali da bala'i maigida,, Allah kawai ne yasa da rabon zaka kawo labari da ka mutu tunda dad'ewa,,,, dama saida nace karkaje kaje da yanzu ni aka bari cikin bak'in cikin rayuwa da kuka ".Inji Inna Tani cikeda matuk'ar sanyin jiki da tsananin tsoro!.

Baba Labbo yace "nima Tani banyi zaton Talatu xatabar macijiya domin tayi gadin Gwamma ba,,, saboda naga wanda ya mutu ya riga ya mutu har abada ".

Inna Tani ta fyace majina tace "haka ne amma dan Allah kada ka sake zuwa gidan nan,,, saboda ina tsoron kada macijiyar ta kasheka a banza da yofi! ".

"wa! Ni in kikaga naje gidan to saidai gawata ce aka kai,,, to ko gawata ban yarda akaita gidan ba idan har na mutu ".Cewar baba Labbo cikeda matuk'ar tsoro da fargaba!.

Inna Tani tace "Allah dai ya tsare gaba maigida,, to fito waje in wanke maka jikinka naga duk ya b'aci da zawo sosai ".

"inajin tsoro Tani ayau d'in nan naga tashin hankali da bala'i wanda ban tab'a gani ba,,,,bazan iya fitowa ba tsoro nakeji sosai ".Inji baba Labbo cikeda matuk'ar tashin hankali!.

Inna Tani tace "babu abinda zai sake faruwa sai alkhairin Allah,, kuma idan Allah ya yarda ba zaka sake mugun gani ba,, saboda wannan tashin hankali da rikicewa yaja ma harsu maigari gudu da sauran mutanen gari fargaba da zullumi! ".

Baba Labbo yace "nikam bazan fito ba inajin tsoro sosai wallahi Tani "..Dak'yar da lallashi,, rok'o,,, gamida da magana mai dad'i sosai Inna Tani ta samu baba Labbo ya fito daga cikin d'akin,,, yana fitowa ta tara masa ruwa a bokiti takai mishi cikin toilet,, ta d'auko towel irin na zane ta bashi ya shiga wanka kayan da duk suka b'aci sosai da zawo tasa klin da sabulun wanki ta wanke tass zad sha'awa,,,, tana gama wankewa ta shanya kayan a saman igiyar wanki,,,, ta shimfid'a tabarma ta zauna tana jiran fitowar baba Labbo daga cikin makewayi..

Ba'a jima sosai ba saigashi ya fito daga cikin toilet,, ya shiga cikin d'akin ya shafa manshafi

sannan ya d'auko wasu kaya ya sanya,,, bayan ya sanya kayan ya fito waje ya zauna kusa ga Inna Tani,,,, ta tashi taje ta kawo masa abincinsa da ruwa masu sanyi cikin jug,,, yayi bismillah ya fara cin abincinsa cike da natsuwa da walwala,, ita Inna Tani sai firfita takeyi masa da fai -fai tana kallonsa cikeda matuk'ar tausayi da k'auna matuk'a..

¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤

Ab'angaren Sule da Gwamma bayan ya gama biyan buk'atarsa,,, babu abinda Gwamma keyi sai hawayen ciwo da rad'ad'i,,, yaje ya d'ebo ruwa a randa ya aza mata ruwan zafi a saman murhu,,, bayan ruwan sunyi zafi sosai yazo ya surka da ruwa masu sanyi ya kai mata ruwan acikin toilet,,,, yazo ya taimaka mata ta tashi tsaye ta dafa kafad'arsa,, ya kaita har cikin toilet ya gwada mata yadda zata gasa jikinta sosai da ruwa masu d'umin ya fito daga cikin toilet d'in.

Yana fitowa ta kama gasa jikinta sosai tareda zama acikin ruwan zafin,,, tana kuka a hankali cikeda matuk'ar rad'ad'in ciwo da zafi,,, haka dai ta daure ta cigaba da gasa jikinta sosai lungu da sak'o ko'ina a cikin jikinta,,, bayan ta gama ne taji zafi da rad'ad'in da takeji ya ragu sosai

acikin jikinta,,,, sannan daga baya ta fito daga cikin toilet d'in ta shiga cikin d'akin ta shirya.

Bayan ta kammala shiryawa ne Sule ya bata maganin rage rad'ad'in zafi,,, ta amsa tasha da ruwa masu sanyi ya dubeta yace "sannu Gwamma nagode sosai da kika sanyani cikin farin cikin da ban tab'a jin irinsaba,, kika bani abu mafi daraja da tsada a rayuwarki,, kika sanyani cikin nishad'i da jin dad'i sosai matuk'a,,,, Allah ubangiji ya baki lafiya kuma yabarmu tare har abada ".

Saida Gwamma ta dubi Sule cikeda takaicin rabata da budurcinta da yayi,, acikin zuciyarta sai sak'e sak'e takeyi na irin mugun hukuncin da zatayi wa Sule can ta nisa tace "hmmmmm babu komai ai wannan yana daga cikin irin soyayyar danake yi maka har acikin zuciyata,,,, kuma kafi k'arfin komai a wajena Sule ".

Yayi murmushi yace "haka ne gaskiya masoyiyata dama haka so yake,,, gamon jini ne shi kuma

farat d'aya yake shiga acikin zuciya babu sallama ko neman izni ".Cewar Sule cikeda matuk'ar yaudara da dad'in baki..

Gwamma tace "babu k'arya acikin maganarka masoyina,,, abin sona akodayaushe ".

Sule yace "Allah ubangiji ya baki lafiya da k'arfin jiki masoyiyata,, ni zan wuce zuwa gida ".Yace tareda mik'ewa tsaye alamar zai wuce. Tace "amin amin Sule ".Ta tashi tsaye domin ta rakashi a waje,,, suka nufi k'ofar gida ta kaishe har waje tana yi masa sai wata rana

Sule yayi tafiyarsa ita kuma tayi dawowarta cikin gida,,, ta zauna saman tabarma tayi tagumi tace "hmmmm Sule kajawa kanka masifa da bala'i wlh!,Budurcina daka amsa baka amshesa ga banza da yofi ba,,,, saina kasheka in kasheka banza! Saika d'and'ani  zafin fitar rai amma ba yanzu zan kasheka ba saina k'ara shan zumarka ".

Hhhhhhhh haka dai ta bushe da mahaukaciyar dariya sosai,,, sannan ta murtuk'e fuska ta cigaba da surutunta na son rai da haukahhhh...

¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤

*BAYAN KWANA BIYU*

***Bayan faruwar mutuwarsu baba Labaran da Sala mafarauci da matarsa,,, garin duk ya rikice da kacamewa da mutuwar mutane ishirin acikin garin Gumi! Ko'ina ka duba acikin garin kukan mutane da ifface iffacensu,,, yara da mata sai kuwwace-kuwwace kawai sukeyi da kuka harna tashin hankali da bak'in cikin mutuwar mutane kusan ishirin.
Ganin haka ne yasa suka k'ara tsoracewa akan al'amarin mayyu,,, tsoro da fargaba ya bayyana k'arara akan fuskar mutanen gari,,, kowa ka kalla kuka sukeyi kamar ransu zai fita daga cikin gangar jikinsu saboda bak'in ciki da matuk'ar fargaba akan lamarin mayyu.

To da yake mutum biyu sun rasu daga cikin danginsu Sala mafarauci da baba Labaran,, shiyasa mutane suka fara zuwa gidan baba Labaran domin su sanardashi abinda yake faruwa,,, Innar Lado kawai suke iske zaune tayi tagumi zuciyarta sai fad'uwa takeyi da k'arfi da k'arfi rassssss! Sukayi mata sallama ta amsa mutum guda kawai ya shigo cikin gidan ya sanar da ita abinda yake faruwa acikin gari,, hankalinta ya k'ara tashi zuciyarta ta cigaba da bugawa da k'arfi d'immmmm! Dak'yar ta sanarda mai aike baba Labaran bai dawo gida ba,, tana ganin yana gidan Sala mafarauci suje can zasu samesa itama anan shi take jiran ya dawo,, dan aiken ya juya waje yaje ya sanardasu maigari abinda yake faruwa..

Batare da b'ata lokaci ba suka d'unguma gaba d'ayansu kusansu goma sha biyar zuwan gidan Sala mafarauci,, domin su sanardasu shida baba Labaran abinda yake faruwa acikin garin,, bada jimawa ba suka kawo bakin k'ofar gidan Sala mafarauci sukayi sallama a waje,, shiru babu amsa sukayita sallama babu adadi sunyi tsaye shiru harna tsawon minti talatin sannan daga baya suka yanke shawarar shiga cikin gidan gaba d'ayansu,, suna shiga filin gidan babu motsin komai saina awaki da kaji babu kowa nan ma saida sukayi shiru sannan daga baya suka yanke shawarar shiga cikin d'akin gabansu sai fad'uwa yakeyi yana bugawa da k'arfi da k'arfi! Tsoro ne da tashin hankali ya bayyana a fuskokinsu k'arara! Maigari shine shugaba amma yafi kowa tsoro da rawar jiki,, dak'yar suka daure suka afka acikin d'akin.

Suna shiga cikin gidan saida numfashinsu ya kusa d'aukewa,, tashin hankali da rikicewa ne akan fuskokinsu k'arara saboda ganin Ummaru sukayi kwance ya some sannan ga k'asusuwan mutane nan su baba Labaran yasshe acikin d'aki,,, sukaje wurin Ummaru domin su bashi taimakon gaggawa babu abinda ke fita daga cikin bakinsu ila "Ina lillahi wa inna ilaihirraji'un! Allahumma ajirni fi musibati wa'akhalufni khari minha!.......

_Share&Comments_
[7/2, 8:15 PM] Mugiratmusa66: 🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥
*MAYYA CE*
🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥

*INTELLIGENT WRITER'S ASSOCIATION ®*✍🏻
_[Onward together]_

*Written by Mugirat Musa*

*DEDICATED TO SIS NAJER'ART*

_Bismillahir rahamanir rahim_

*PAGE 22*

"Ina lillahi wa inna ilaihirraji'un Allahumma ajirni fi musibati wa'akhalufni khari minha!!!".Suka fad'a atare cikeda matuk'ar tashin hankali da rikicewa! Bayan sunje wurin Ummaru da sauri d'aya daga cikinsu yaje ya d'ebo ruwan sanyi a cikin randa,, ya kawo akayima ruwan addu'a mai tsawo sannan aka juye masa ruwan gaba d'aya ajikinsa saida ko'ina a jikinsa ya jik'e da ruwan,,, ganin da sukayi zasu gaji da tsayuwa yasa dole aka d'auko tabarmi guda biyu kowanensu ya zauna akai,,, sukayi jugum duk jikinsu yayi matuk'ar sanyi da fargaba akan abinda idanunsu suka gani,, sannan kuma ga k'asusuwansu Sala mafarauci nan yayyasshe ko'ina a cikin d'akin k'arnin jini kawai yake tashi,, ,,babu dad'in ji balantana gani sunyi shiru na tsawon lokaci da tagumi gabansu sai fad'uwa yakeyi da sauri da sauri,,, can dai sukaji Ummaru yaja dogon numfashi tareda yin tari yana farfad'owa ya tashi zaune yana kallonsu d'aya bayan d'aya,,,,, ganin ya farfad'o ne zuk'atansu suka cika da farin ciki da murna sosai sannan kowanensu ya matso kusaga Ummaru suna yi masa sannu,,, yana amsawa bayan d'an wani lokaci ne maigari Garba ya k'ara matsowa kusa ga Ummaru yace "Ummaru munzo wurin iyayenka da yayan babanka Labaran,, saboda in sanardasu abinda yake faruwa acikin garin Gumi na mutuwar mutane ishirin,,,,, biyu daga cikinsu 'yan uwanku ne,, amma sai muka tarar da kai ka suma sannan bamuga mahaifanka ba da yayan babanka,,,,sanardamu mi yake faruwa yakai Ummaru? ".Alokacin ne Ummaru yaji wani irin turirin bak'in ciki ya tokare masa gaba,,, wani abu ne ke yawo a cikin jinin jikinsa idanunsa sukayi jawur hawaye kawai ke fita daga cikin idanunsa,,, zuciyarsa sai tafasa takeyi da k'una sosai babu abinda kake hangowa sai tsananin b'acin rai da bak'in ciki acikin idanunsa,,, maigari ne ya sake cewa"kayi hak'uri ka sanardamu duk abinda yake faruwa,,, komai yayi zafi maganinsa Allah kuma komai yayi farko yanada k'arshe zaizo ya wuce kamar ba'a tab'a yinsa ba ".Wani dake gefen maigari mai suna Tukur,,, ya karkace baki yace "haka ne maganarka  maigari Allah yaja zamaninka,,, hak'uri zakayi Ummaru ka gaya mana abinda yake faruwa saboda kaga anan babu wanda yasan abinda ke faruwa ".Madu yace "mu kanmu jikinmu duk yayi sanyi hankalinmu duk ya tashi! Saboda bamuga alamarsu Sala mafarauci da matarsa da yayansa a cikin wannan d'akin ba,,, kuma matar Labaran ta tabbatar mana yana nan yazo gurin Sala mafarauci domin ya k'ara diba yadda jikinsa yayi sauk'i sosai ".

"k'warai da gaske haka maganar take Ummaru,,, ba kai tsaye mukayo nan ba saida muka biya gidan babanka Labaran ".Inji maigari cikeda matuk'ar sanyin jiki da lallashi. Ummaru ya d'ago ya kallesu idanunsa sunyi matuk'ar ja,,, ya bud'i baki dak'yar yace "kuyi hak'uri bawai na k'yaleku bane saboda baku isa gareni ba,,, na k'yaleku ne saboda zuciyata k'una da tafasa

takeyi alokacin amma yanzu zan sanardaku irin mummunan k'addarar data sameni nida iyayena da baba Labaran,,, k'addarar da ban tab'a zaton ko a mafarki zata afku gareni ba,,, mugun al'amarin da har abada bazan tab'a mantawa dashi ba ko bayan raina....... ".Ummaru ya kwashe labarin irin ta'adancin da tsutsar tayima iyayensa da baba Labaran harta kashesu,,, ya sanardasu yadda tayi masa mugunta har ya some baisan inda kansa yake ba,,, yana kawo k'arshen maganarsa ya fashe da wani rikitaccen kuka mai ban tausayi da tarin bak'in cikin rayuwa.
Gaba d'ayansu suka k'ara saka salallami "ina lillillahi wa inna ilaihirraji'un Allah ubangiji ya jik'ansu Sala mafarauci! Yasa sun huta acikin kabarinsu ".

Maigari yace cikeda matuk'ar tashin hankali da rikicewa! "kayi hak'uri Ummaru Allah yana tareda masu hak'uri,,, amma wannan abin ya zamo d'aukar fansa ne ga Inna Talatu MAYYA saboda kasan babanka shine ya zamo ajalinta,,, kaga kuwa kenan tanada 'yan uwa ko abokiya wadda ta d'aukar mata fansar jinin Talatu harta kashe mutane ishirin da uku gamida iyayenka! ".

Madu yace "wannan abin babu shakka haka yake,, saboda kashe rayuka da akeyi acikin garin Gumi yayi yawa sosai wlh,,, ada muna ganin abin da sauk'i ayanzu yazo yaci uban na da ".

"ai wannan mayyar da ta kashe mutane ishirin da uku to ta wuce Talatu MAYYA,,, awurin hatsibibanci da zalunci! Saboda Talatu bata tab'a kashe rai kusan ishirin lokaci guda ba ".Cewar Tukur cikeda matuk'ar bak'in ciki da takaicin abinda ke faruwa..

Maigari yace "haka ne gaskiya amma zamu d'auki babban mataki acikin garin Gumi,,, na duk inda aka kama MAYYA akasheta saboda abin yayi yawa sosai idan ba haka harmu zasu shiga cikin gidajenmu suna kashemu da iyalenmu,,, kunga kenan muma bamu tsira ba akodayaushe akowane lokaci mutum za'a iya kame masa kurwa a cinye ,,,yanzu dai Madu tashi ka tattara k'asusuwan nan muje ayi musu sallah arufesu mak'abarta "..

"to maigari ".Cewar Madu ya tashi tsaye ya samo buhu ya tsince k'asusuwan baki d'aya,,, ya sanya cikin buhu ya dawo ya zauna.

Tukur ya dubi Madu yace "ba zama zamuyi ba tashi zamuyi yanzu nan muje can cikin gari,, akaisu tareda da sauran gawarwakin dake can ana jiranmu ".

Dogarawan sukace"maganarka haka take Tukur angaisheka".

Suka mik'e tsaye gaba d'ayansu harda Ummaru,,, suka fito daga cikin gidan cike da matuk'ar bak'in ciki da jimamin mutuwarsu Sala mafarauci da mutane ishirin,,, suka d'unguma zuwa inda aketa yima gawarwakin mutane wanka.

Koda sukaje har angama musu wanka da sallah,,, za'a kaisu gidansu na gaskiya maigari ne ya umurci mutane da su tsaya,,, suna tsayawa ya umurci Ummaru ya basu labarin da ya basu na mutuwarsu baba Labaran da Sala mafarauci sannan aka gwada musu yadda mayya ta cinye musu nama har ya dawo k'asusuwa,,,, ai kuwa mutane suka k'ara rikicewa da d'imaucewa! Akan mummunar annobar mayya data zarce Inna Talatu akan rashin imani da shahara a cikin maita! Haka dai sukayiwa k'asusuwan sallah sannan suka d'unguma zuwa mak'abarta domin akaisu makwancinsu na gaskiya.

Mutane kowa ka diba hawaye ne ke gangaroya daga idanunsu,,, tsoro da tsananin tashin hankali ne bayyane afuskokinsu saboda kowa yasan zai iya fad'awa cikin tarkon k'ursugumar mayya gagararriya acikin mutane da aljannu! K'arin takaici da haushi basusan ko wa ce ce sabuwar mayyar dake kashesu abanza tareda jaddada fitina a tsakaninsu ba..

*********************

Bayan sun dawo daga kaisu Sala mafarauci gidansu na gaskiya,, to alokacin ne maigari yayi sanarwa akan mutanen gari su taru bakin k'ofar gidansa,,, bayan mutane sun gama taruwa ne ciki kuwa harda baba Labbo,,, sannan maigari yayi bayanin cewa duk inda aka kama mayyu acikin garinsa to akashesu,,, sannan ya juyo ya dubi baba Labbo ya tambayesa rannan miye ya sanyashi gudu har ya kawo wurinsu da matsiyacin gudun ceton ransa,,, baba Labbo ya duk'ar da kansa ya kwashe labarin irin yadda macijiyar ta bashi tsoro da kuma gargad'insa akan kada ya sake dawowa gidan yayansa marigayi Malam Mamman.

Mutane sunka k'ara tsoracewa da rikicewa akan wannan labari da baba Labbo ya sanardasu,,, maigari yayi magana ya nuna musu za'a saka matakan tsaro acikin garin baki d'aya sannan za'a sanyawa Gwamma ido matuk'a,, saboda yadda take rayuwar cikin gidan batare da tsoro ko wani shakku ba.

Su kansu mutunen gari zuciyarsu ta basu akwai wani abu ab'oye ko lauje cikin nad'i,,, saboda sunsan babu mai iyawa zama cikin gida shi kad'ai idan ba hatsabibi ba,, aka umurci Malamai gaba d'ayansu dasu k'ara dagewa akan Allah ubangiji ya tonama mayyu asiri,,, mutane sukace amin sannan sukayi addu'o'i kowa ya kama gabansa cikeda matuk'ar zullumi da rad'ad'in ciwon mutuwar mutane ishirin da uku..

Musamman yafi kowa jin zafi da rad'ad'in ciwo har cikin zuciya ,,,,,yasha alwashin kowaye ya kashe masa iyayensa da yayan babansa sai ya d'auki fansar jininsu,,,, ab'angaren Innar Lado wato matar baba Labaran tanajin labarin mutuwar mijinta dana Sala mafarauci da matarsa ta

fad'i k'asa ta some,,,,mata mak'wabtanta sukazo kawo mata agajin gaggawa kafin ace wani abu zuciyarta ta buga ta rasu! Haka dai itama akayi mata wanka aka kaita gidanta na gaskiya..

Ina lillahi wa inna ilaihirraji'un!!!.

**Ab'angarensu Sule da Gwamma haka suka cigaba da mu'amalarsu kamar mata da mijinta,,, akodayaushe yana manne da ita,,, ita kuma ta cigaba da cin naman mutane dana aljannu komai cikin sirri da b'oye takeyinsa,,, shi kansa Sule baisan wa ce ce ainahin Gwamma ba kawai yana tare da ita ne........

_Share&Comments_
[7/3, 2:53 PM] Mugiratmusa66: 🍥🍥🍥🍥🍥🍥

🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥
*MAYYA CE*
🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥

*INTELLIGENT WRITER'S ASSOCIATION ®*✍🏻
_[Onward together]_

*Written by Mugirat Musa*

*DEDICATED TO SIS NAJER'ART*

_Bismillahir rahamanir rahim_

*Hak'ik'a ban tab'a zaton zan samu tarin masoya a rayuwata ba,,, ban tab'a zaton novel d'ina yanada farin jini da masoya masu yawa sai yanzu,,, nagode da soyayyarku masoyana aduk inda kuke a fad'in duniya,, inasonku ina k'aunarku kamar yadda kuke k'aunata*.

*PAGE 23*

Shi kansa Sule baisan wa ce ce ainahin Gwamma ba kawai yana tare da ita ne,,, ita kuma bata

yarda ya gano ita mayya ce ba saboda batason ya baza ta acikin gari,,, kowa yasan mummunan dabi'ar da take aikatawa na kashe rayukan mutane....

*BAYAN KWANA BIYU*

Bayan kwana biyu da faruwar wannan mummunan al'amari,,,mutanen gari gaba d'aya kowa ya k'ara tsoracewa akan lamarin mayyu gashi sunga ankashe musu babban mafarauci,,,, wanda ya shahara a wurin kamun namun daji da kuma maganin mayyu,,, sun riga sunsan cewa Inna Talatu MAYYA tabar mai d'aukar mata fansa amma basu gano ainahin wa ce ce ko wa ye yake d'aukar ran mutane,,, kamar ran dabba shiyasa maigari bayan yasa matakan tsaro ya kuma samu amintattun mutanensa asirrance,,,, su dinga lura sosai da shige da ficen Gwamma,,,, babu wanda ya sani daga maigari sai wad'annan amintattunsa,,, ita kanta Gwamma bata sani ba balantana sauran mutanen gari...

Ab'angaren Ummaru   kuwa bayan rasuwarsu Sala mafarauci ya shiga cikin matsanancin hali na bak'in ciki da k'uncin rayuwa,,, kullum kullum idan kaga Ummaru sai ya baka tausayi yayi bak'i sosai ya rame,,,, saboda damuwa da yawan tunani gashi yanxu shi kad'ai yake kwana acikin gidansu,,,, domin bayason yaje wani wurin ya kwana saboda kada yabar gidan babu kowa acikin gidan nan....
  Wata rana Ummaru yana zaune shi kad'ai acikin gidan yayi tagumi,,, zaune yake saman tabarma ya fad'a duniyar tunani,,, kallo d'aya zakayi masa kasan yana cikin wani hali domin yayi babban rashi na har abada! Ya rasa iyayensa da yayan babansa da kuma matarsa alokaci guda,,, duk wani farin ciki ko walwala nasa ya tsaya cak sai dai ya zauna shiru shiru babu magana,,, ganin haka ne yasa Kabiru abokinsa yana yawan zuwa wurinsa domin ya d'ebe masa kewa da kuma bashi kalamai masu dad'i...

Can dai bada jimawa ba saiga sallamar Kabiru ya shigo cikin gidan,,,, yaji shiru ba'a amsa ba ya sake sallama ya shigo har kusaga Ummaru yasa hannunsa ya jaye hannun Ummaru daga yin tagumi,,, sannan ya zauna alokacin ne Ummaru ya dubi Kabiru yace "mutumena yaushe ka shigo cikin gidan nan ban sani ba? ".

"ya za'ayi ka sani inata sallama kanacan kana tunani Ummaru,,, wai miyasa ba zakayi hak'uri ka fallamawa Allah komai ba,,,, ka daina yawan tunani domin kada ka kamu da wani ciwon ".Inji Kabiru cikeda tausayin abokinsa.

Ummaru ya bud'i baki yace cikeda matuk'ar bak'in ciki da takaici "idan Allah ya yarda zan rage tunani Kabiru,,, amma har abada bazan tab'a mantawa da iyayena ba dasu baba Labaran domin sune jigon rayuwata,,, na zama maraya gaba da baya ba wanda zan kalla inji sanyi a raina Yaya Lado shima ita ta fara kashesa ".

"addu'a zakayi musu akan Allah ubangiji yasa sun huta kuma yakai haske kabarinsu,,,, sannan maigari Garba ya aikoni wurinka Ummaru ".Cewar Kabiru.

Ummaru yace "wa ne sak'o ne ya baka ka gayamin?,,, sanardani inajinka Kabiru ".

Kabiru yaja dogon numfashi yace "Maigari ne ganin halin da kake ciki na bak'in ciki da damuwa,,, gashi kuma kai kad'ai kake rayuwa acikin gidan nan kaga kuwa dole damuwa ta k'ara maka yawa,,,, sannan nayi nayi dakai kazo mu dinga kwana tare ka nunamin bakayi saboda inada mata,,, to maigari ya baka auren 'yarsa Ummu Salma wani sati idan ya zagayo za'a d'aura muku aure idan har ka yarda,,, saboda haka yace kaje ka samesa idan ka amince kanason 'yarsa ".

Ummaru yayi shiru na tsawon lokaci yana nazari da tunanin maganar Kabiru,,, ya lula duniyar nazari da tunani...

Babu jimawa ya d'ago kansa ya kalli Kabiru yace "hmmm to kai mi ka gani akan wannan maganar,,, na amince ko yaya abokina ?".

"ka amince mana Ummaru maigari yana sonka da alkhairi sannan ta haka ne idan kayi aure zaka rage damuwa da yawan tunani,,, domin sadaki kawai zaka biya ad'aura aure sannan kaga idan kayi aure sai mu fara shirin d'aukar fansar rayukan iyayenka da sauran mutanen gari,,, saboda ni jikina ya bani idan ba macijiyar da ake labari acikin gari wadda Talatu MAYYA tabar fakon Gwamma ta kashe maka iyayenka ba da sauran mutane,,, to mi Gwamma take tink'aho

dashi dahar zata zauna ita kad'ai a cikin wannan gida mai cikeda sihiri? ".Inji Kabiru cikeda matuk'ar nazari da tunani.

Ummaru yace "na amince da auren Ummu Salma d'in zanje in samu maigari ,,, domin mu tattauna sannan inyi magana da yarinyar,,, kuma maganarka akwai alamun k'amshin gaskiya acikinta  amma ba komai kowaye ma zan kamasa da hannuna saina kashe duk wanda yakeda sa hannun  acikin mutuwar iyayena! ".

Kabiru yace "haka ne gaskiya ai da sannu koma waye Allah zai tona masa asiri,,, kowa ya gano mai aikata wannan mummun d'abi'a ta maita! ".

Ummaru yace "ai bawai haka na k'yale ba ina nan ina saka idanu akan shige da ficenta ita Gwamma,,, sannan idan ma itace wlh bazanyi mata sassauci ba ".

"sassauci kuma? Ai mayyu babu su babu sassauci har abada acikin rayuwarsu,,, saboda basu aikata alkhairi ba taya za'a yi musu da k'yau idan aka kamasu ".

Ummaru yace "haka take maganarka Kabiru ".

Haka suka cigaba da tattaunawa akan yadda zasu b'ullowa al'amarin mayyu,,,da kuma maganar aurensa da Ummu Salma d'iyar maigari....

¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤

Bayan gari ya waye Ummaru ya tashi yayi wanka ya shirya,,, sannan yaje gidan Kabiru suka d'unguma zuwa gidan maigari.

Suna zuwa sukayi sallama a k'ofar gidan ,,,,Zubairu k'anen Ummu Salma,,, shine yayi musu jagora har cikin gidan zuwa wurin maigari,,, suna shiga cikin gidan suka iske maigari Garba zaune saman kujera ga tabarma shimfid'e gaba garesa,,, suna zuwa suka duk'a har k'asa suka gaida maigari,,,, ya amsa musu fuskarsa asake cikeda matuk'ar farin ciki da nishad'i sosai..

Maigari ya bud'i baki yace "Ummaru ina fatar sak'ona ya isa zuwa gareka,,, da fatar zaka bani had'in kai akan auren da nakeson in had'a ku kaida Ummu ".

Ummaru ya duk'ar da kansa cikeda matuk'ar ladabi da girmamawa yace "eh baba sak'onka ya iso gareni ".

"kayi hak'uri Ummaru komai ya samu bawa muk'addari ne daga Allah,,,, sannan bawa bai isa ya gujewa k'addararsa ba kuma komai nufin Allah ne shine masanin gaibu,,, saboda haka na baka auren 'yata Ummu Salma wani sati za'a d'aura aurenku ".Cewar Garba maigari.

Sai asannan Kabiru ya d'ago kansa yace "hak'ik'a baba babu abinda zamuce maka Allah ubangiji ya saka maka da mafificin alkhairi,,, sannan mun amshi auren 'yarka hannu bibbiyu kayi mana abinda bazamu daina yi maka addu'ar gamawa lafiya ba,,, mun gode sosai Allah ubangiji ya k'ara nisan kwana ".

Ummaru yace "amin ya rabbi na yarda na amince da auren Ummu Salma baba,,, kayimin abinda har abada bazan tab'a mantawa da halaccinka agareni ba,,, sannan ka nunamin nima d'an gata ne a wurinka duk da yake banida iyaye,,, ka nunamin k'auna azahiri da bad'ini Allah ubangiji ya k'ara girma da d'aukaka ".

"karku damu duk abinda nayi maka nayi maka ne domin Allah mad'aukakin sarki,,, sannan ba fad'uwa bane komai mutum yayi ladarsa tanaga Allah,,,, saboda haka ku daina yimin godiya kunfi k'arfin haka a wajena sai dai ku jira har lokacin biki ".Inji Garba maigari cikeda matuk'ar farin ciki sosai.

"tabbas haka ne gaskiya baba ".Cewar Kabiru.

Haka dai ya cigaba da yi musu nasihohi masu ratsa zuciya,,,, sannan ya nuna musu muhimmanci hak'uri da juriya da kuma zamantakewar rayuwa.

Bayan maigari ya gama yi musu nasiha mai ratsa jiki,,, sannan ya tashi tsaye yace musu "shi zai tashi ya kira Ummu Salma domin su gaisa da juna ".

Kabiru yace "to baba muna jiranta ".

Maigari ya tashi tsaye ya shige cikin d'aki domin ya kira Ummu Salma,,,, yana shiga ba dad'ewa ba saiga Ummu ta fito daga cikin d'akin ta duk'a har k'asa ta gaidasu,,, sannan suka amsa mata cikin fara'a da walwalar fuska.

Kabiru ya dubi sama da k'asan Ummu Salma da k'yau ba laifi tanada k'yau matuk'a ba k'arya ,,, sannan daga baya yace "Ummu Salma ina fatar kinsan dalilin da yasa mukazo wurinki,,,, saboda ku fahimci juna keda Ummaru ".

"baba ya sanardani komai dangane daku,,, saboda haka na amince da duk abinda babana ya gindayamin".Cewar Ummu Salma cikeda matuk'ar kunya ..

Ummaru yayi murmushi yace "masha Allah komai yayi k'yau matuk'a naji dad'i sosai da kika amince da kina sona,,, nima ina sonki fiye da tunaninki kuma ba za'a samu wani matsala ta wajena ba,,, zan rik'e ki amana da hannu bibbiyu Salma saboda haka kada kiji wani shakku ko kwankwanto akaina ".

Salma tace "babu matsala nima awajena zan kasance mai biyayya da ladabi agareka matuk'ar ina raye a cikin duniya,,, zan sanyaka cikin farin ciki da nishad'i mai d'orewa".........

_Share&Comments_

~Kuci gaba da bina ni Mugirat~
[7/4, 11:20 PM] Mugiratmusa66: 🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥
*MAYYA CE*
🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥

*INTELLIGENT WRITER'S ASSOCIATION ®*✍🏻
_[Onward together]_

*Written by Mugirat Musa*

*DEDICATED TO SIS NAJER'ART*

_Bismillahir rahamanir rahim_

*PAGE 24*

"Zan sanyaka cikin farin ciki da nishad'i mai d'orewa,,, zan zamo fitila mai haskaka rayuwarka zan sadaukar da farin cikina domin samun farin cikinka,,, biyayya ga iyaye ya zamo wajibi agareni domin samun aljannata agobe k'iyama ".Cewar Salma cikeda matuk'ar natsuwa da hankali. Alal hak'ik'a Ummaru yaji dad'in kalamanta sosai wani sanyi ne da jin dad'i ke kwaranya acikin zuciyarsa,,, ayanzu ya tsinci kansa cikin tsananin farin ciki da murna mara misaltuwa,,, ya kuma k'ara tabbatarwa da yayi dace da masoyiya ta gari abar alfahari ga kowane d'a namiji,,, ya riga ya sadak'ar idan Allah ya yarda ba zaiyi nadamar auren Salma ba a rayuwarsa,,, saboda daga ganinta kasan yarinya ce mai tarbiya da natsuwa gata da hankali da girmama na sama gareta,,, gata da sanyin hali da k'yakk'yawar d'abi'a ta ko'ina tayi batada matsala a rayuwa,,, tanada tausayi da jink'ai musamman akan yara ko nakasassu,,, batada girman kai ko kad'an..

Cikin tsananin farin ciki da shauk'in so,,, Ummaru ya d'ago idanunsa ya kalleta cikeda matuk'ar farin ciki da samun mace tagari yace "hak'ik'a Allah ubangiji abin godiya ne daya had'a ni da mace tagari d'iyar mutanen kirki,,, wadda takeda tarbiya da girmama manya,,, nima zan rik'eki amana bisa gaskiya da tsoron Allah zan zama jigon rayuwarki abar alfaharinki akodayaushe,,, zan kasance inwa agareki domin kada rana ya illatamin ke ".Cewar Ummaru cikeda matuk'ar nishad'i sosai.

Salma tayi murmushi wanda ya k'ara bayyanar da tsantsar k'yawon fuskar da Allah ya bata,,, sannan tayi masa kallon soyayya tace "naji dad'i matuk'a Allah ubangiji ya gwada mana lokacin auren lafiya,,, sannan idan muka zamo miji da mata Allah ya bamu zaman lafiya da kuma juriya da hak'urin xama da juna ".

Sai asannan ne Kabiru ya sake magana yana murmushin jin dad'i,,, saboda yadda suka amince da juna farat d'aya ya matuk'ar bashi sha'awa.
Yace "hak'ik'a nayi farin ciki matuk'a ta yadda kuka fahimci juna batare da wata matsala ba,,, sannan kukayi biyayya ga maigirma baba maigari,,,, ku masu biyayya ne da bin maganar manya Allah ubangiji ya gwada mana lokacin aure lafiya,,, sannan kuma ya baku yara masu albarka da biyayya agareku ".

"Amin amin abokina amma fa ka iya addu'a mai k'yau,,, Allah ya sauki matarka Hanne lafiya".Inji Ummaru cikeda zolayar Kabiru.

Salma tace "amin ya rabbi ".Kanta duk'e tana mai wasa da yatsun hannunta.

Alokacin ne Kabir ya harari Ummaru da wasa,,, sannan ya d'auko dubu hud'u daga cikin aljihunsa ya mik'awa Salma yace "gashi ta sayi kayan kwalliya ba yawa tayi hak'uri ".
Salma ta nok'e tak'i amsa,,, tana jijjiga kai alamar a'a ba zata amsa ba,,, "bangane mi kike nufi da haka ba Salma ".Cewar Ummaru.
"ai shine na gani ina bata tana wani jijjigar kai kamar mage ".Inji Kabiru cikeda fara'a.
"ina nufin ni bazan amshi kud'inka ba saboda babana ya gargad'eni akan na daina amsar kud'in samari ".Inji Salma cikeda ladabi.

Kabir yace "dama kin saba amsar kud'in wasu ne? Kuma naga Ummaru ba wani bane mijinki ne idan Allah ya yarda ".

"a'a nidai kawai ku barshi baba zaiyimin fad'a agida wlh nagode sosai da soyayyarka agareni,,, ina sonka ba domin abin hannunka ba Ummaru idan kukaje gida ina gaida Hanne da sauran mutanen gida,,, na barku lafiya cikin aminci da k'auna ".Inji Salma cikeda natsuwa tana gama fad'ar wannan magana tayi shigewarta cikin gidansu,,, batare da tsaya ta saurari kalaman da zasu fito daga cikin bakinsu ba..

Sukayi tsaye suna mamakin irin tarbiyar da Salma takedashi,, sannan ga iya tsara magana mai ma'ana da muhimmanci.

Can dai Kabiru ya dubi Ummaru yace "abokina mu wuce zuwa gida Allah ne ya tausaya maka,,, ya baka mace mai tarbiya da sanin ya kamata ".Yace tareda mayarda kud'in cikin aljihunsa ya ajiye.

"haka ne Kabiru mu wuce zuwa gida yanzu,,, aini nayi matuk'ar farin ciki domin kakata ta yanke sak'a ".Cewar Ummaru tareda da jan hannun Kabiru suka d'unguma zuwa gida,,, suna tafiya suna fira cikeda matuk'ar farin ciki da walwala sosai..

********************

***Bayan sati d'aya ya zagayo mutane da dama aranar assabar,,, suka shaida d'aurin auren Ummaru Sala mafarauci da Ummu Salma Garba maigari akan sadaki dubu talatin lak'adan,,,,d'aurin auren ya samu halartar mutane da dama daga wasu garuruwan daga nesa abokanin maigari,,, anyi taro lafiya an watse lafiya cikeda mutunci da karamci,, anyi abinci kala kala aka rabawa mutane k'yauta ,,,,an raba lemun k'walba irinsu fanta,, coke da dai sauransu.. Komai na bikin anyisa a wadace cikin rufin asiri da wadatar zuci,,, amarya tasha kwalliya da chanza kaya kala kala masu k'yawo sosai..

'Yan uwa da abokan arzik'i sunzo na nesa da na kusa,,, dare nayi da misalin k'arfe 9:00pm na dare dai dai aka d'unguma akaje aka kai amarya d'akin mijinta,,, sai dai muce Allah ubangiji ya basu zaman lafiya da zuri'a d'ayyiba mai tarin albarka.

¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤

*BAYAN SHEKARU UKU*

Bayan shekaru uku abubuwa da dama sun faru ciki kuwa harda k'aruwar haihuwar da Ummaru mafarauci ya samu,,,,,matarsa Salma ta haifi d'a namiji na farko mai suna Habibu,,, ta biyu kuwa ba'a dad'e da haihuwarta ba mai suna Husna. Shima Kabiru d'iyansa biyu da Hanne matarsa ta farko Yusrah na biyu Yusuf shima dai k'arami ne,,, haka dai suke kula da iyalansu tareda basu kulawa da nuna soyayya na gaskiya,,, zumuncinsu ya k'ara k'arfi sosai a tsakaninsu komai tare suke yinsa cikeda yarda da aminta da junansu,,, idan kaga yadda sukeyin zumunci saikayi mamaki sosai saboda kana rantsewa da Allah kace 'yan uwan juna ne amma abin ba haka yake ba sone gamon jini da kuma k'auna matuk'a..

Ba laifi Kabiru da Ummaru yanzu sun zama shahararrun masu kud'i,, musamman Ummaru da ya zamo shahararren mafarauci wanda ya gaji ubansa Sala mafarauci,,,,,yafisa zamowa babban mafarauci a cikin garin Gumi da sauran k'auyukkan dake kewayenta,,, babu inda labarin jarumtarsa da shaharsa baije ba,,, kowane irin daji komai hatsarin daji da aljannunsa yana iya shiga ciki yayi farauta ya dawo gida lafiya k'alau,,, babu dabbar da take gagararsa kamawa ba sai dai idan baiyi idanu biyu da dabbar ba,, alk'awarin daya d'auka na fansar jinin iyayensa dana baba Labaran bai manta ba yana nan dai yana shirye shiryen d'aukar fansa!.

¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤

***Ab'angarensu Sagiru,, Ila da Lawwali sun zama shahararrun 'yan kasuwa masu kud'i dai dai gwargwado,,, ganin sunyi kud'i yasa suka gina gidajensu kusaga juna,,, sannan kowane daga cikinsu ya nemo mata budurwa baba Labbo yayi musu auren soyayya.
Lawwali sunan matarsa Aliya,, Sagiru Adama,, shi kuma Ila Ladidi haka dai aka d'aura aurensu cikin wadatar zuci da rufin asiri sosai,,, d'aurin aurensu ya tara mutane da dama 'yan uwa da abokan arzik'i duk sunzo wurin bikinsu Lawwali,,, haka aka kai kowace amarya gidan mijinta cikin mutunci da lumana..

_Allah ubangiji ya bada zaman lafiya da zuri'a d'ayyiba mai tarin albarka,,, wad'anda basuda aure ya kawo musu mazajen aure nagari masu halayyar k'warai._

Gwamma kuwa haka dai ta cigaba da cin naman mutane da mu'amalar iskanci da Sule,,, duk da irin matakan tsaro da aka sanya mata bai hana mata aikata maita ba! Babu abinda ta bari na naman mutane dana aljannu kowa bata bari ba,, gashi mutane sai tsoronta sukeji saboda amintattun maigari sun tabbatar masa da Gwamma *MAYYA CE* babba kuwa,,, komai na Gwamma cikin wayo da dabara takeyinsa na kamun kurwar mutane da aljannu!.

Maigari yanajin wannan maganar hankalinsa ya d'unguma sosai gabansa ya bada rasssss! Jikinsa sai makarkatar tsoro yakeyi saboda yaga alamar Gwamma ta zarce Inna Talatu MAYYA rashin imani acikin maita,,, ya aika dogarinsa guda ya kira masa surukinsa wato Ummaru d'an Sala mafarauci,,, batare da b'ata lokaci ba sukazo tare maigari ya kwashe labarin komai ya gaya masa cewa Gwamma ce shahararriyar mayyar da ta addabi rayuwar mutane sosai,,,

Ummaru ya nuna masa ya kwantar da hankalinsa shine zai kamata da hannunsa sannan daga baya ya kasheta har lahira,, Ummaru yaba maigari shawarar asanarda mutane domin susan irin abubuwan da suke faruwa agari,,, maigari ya sanardasu komi gameda Gwamma mayya da kuma irin tsafe tsafen da take aikatawa ya gaya musu tafi mahaifiyarta shahara da gunguma akan maita,, domin ita har naman aljannu ci takeyi bawai ga mutane kawai ta tsaya ba.

Mutane suka k'ara rikicewa da d'imaucewa akan tashin hankali,,, gashi yanxu sun k'ara tabbatarwa Gwamma tafi mahaifiyarta shahara da gunguma akan maita da mugunta iri iri daban daban,,, sannan batada tausayi da imani ko kad'an,, bayan maigari ya gama nasa jawabi. Ummaru yayi nasa jawabi inda ya nuna musu dasu kwantar da hankalinsu zai d'auki babban mataki akanta sannan zai kamata ya gana mata azaba sannan ya kasheta! Ya k'ara nuna musu dasu k'ara dagewa da yawan yin addu'a domin Allah ubangiji ya kawo musu k'arshen zaluncin Gwamma,,, kuma su kulada iyalansu tareda yin taka tsan tsan domin gujewa afkawa cikin tarkon Gwamma mayya,, yana kawo k'arshen maganarsa suka umurci mutane kowa ya watse ya kama gabansa,,, kallo d'aya zakayiwa mutane ka hango tashin hankali da rikicewa k'arara akan fuskarsu,,, masu raunin zuciya banda hawayen bak'in ciki da k'uncin rayuwa babu abinda sukeyi,,, suna tafiya suna jimamin abinda yake faruwa marasa dad'in saurare da kuma ji,, ga kuma zullumi da fargabar akan kodayaushe mutum ana iya kame masa kurwa ya mutu har abada.........

_Share&Comments_
[7/4, 11:36 PM] Mugiratmusa66: 🍥🍥🍥🍥🍥🍥

🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥
*MAYYA CE*
🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥

*INTELLIGENT WRITER'S ASSOCIATION ®*✍🏻
_[Onward together]_

*Written by Mugirat Musa*

*DEDICATED TO SIS NAJER'ART*

_Bismillahir rahamanir rahim_

*PAGE 25*

**Mutum ana iya kame masa kurwa a cinye ya mutu abanza,,,, batare da anyi saurin ganowa ba sai daga baya ai kuwa mutane suna komawa gidajensu,,, maganar Gwamma k'usurgumar mayya ce ya bazu ko'ina a cikin garin Gumi,,, mata da k'ananan yara suka tsorace da rikicewa! Wasu ma babu abinda sukeyi sai kuka da zubar da hawayen bak'in ciki da tsoron mutuwa,,,, gashi babu halin mutum yace zai gudu yabar gari yayi gudun hijira,,, to ganin haka ne yasa mutane suka rage yawan fitar dare ko irin gungu nan da samari da dattijawa keyi acikin dare

suna fira yanzu babu shi,,, saboda kowa yana tsoron masifar Gwamma da kuma ta cinye mutum a banza babu me cetonsa,,,, Ummaru mafarauci shi kad'ai kawai ke fitowa acikin tsakar dare yana yawon farautar kamun Gwamma mayya,,, kullum kullum yake fitowa nemanta amma har yanzu shiru Allah bai bashi ikon kamata ba,,, domin duk yawon nemanta da yakeyi tana ganinsa acikin madubin tsafinta,,,,, idan taga yadda Ummaru d'an Sala mafarauci yake yawon nemanta kamar yadda mafarauci ke neman namun daji saita bushe da muguwar dariya sosai tace "hhhhhhhhhhh Ummaru kenan ba zaka iya kamani cikin sauk'i sosai ba sai kasha bak'ar wahala,,,, kafin ka kamani sannan kashe mutane yanzu na fara! Babu ubanda ya isa ya hanamin cin naman mutane dana aljannu duk duniya,,, kafin na mutu sainayi abubuwan da har abada ba zaku tab'a mantawa dani ba,,,,,,saina shayar daku ruwan guba da bak'in cikin da zai kasheku d'aya bayan d'aya,,,, babu gudu babu ja da baya wannan alk'awari ne na d'auka araina kuma saina cikasa,,, saina cikasa! ".
Haka dai takeyin maganganu iri iri daban daban na d'aukar fansar jinin mahaifiyarta,,,,,saboda ita Gwamma duk da mutane sun gano ita mayya ce bata damu ba,,, sannan hankalinta kwance yake alokacin ne ma ta k'ara k'aimi wurin cin naman mutane da aljannu,,,,, mutum sai yana zaune cikin kasuwa ko majalisarsu akirasa ace 'yarsa ko d'ansa ko wani d'an uwa nasa ya mutu! Kullum safiyar Allah idan gari ya waye saita kashe kusan mutum goma ko fiyeda hakan,,, ganin mutuwar da akeyi ne yasa maigari da sauran mutanen gari suka fita cikin hayyacinsu,, tsoro,, tashin hankali,, fargaba duk suna taredasu akodayaushe akowane lokaci,,, Ummaru ma abin yana matuk'ar damunsa na yadda Gwamma take shammatarsa ya kasa kamata,,,, amma sai ya nasa acikin zuciyarsa duk daren dad'ewa sai ya kamata sannan komai b'oye b'oyenta da sihirinta tabbas wata rana sai dubunta ya cika..

**Washe gari da safe misalin k'arfe 11:00am na safe,,, bayan Gwamma ta share gidan gaba d'ayansa tsab,,, dayake nan Sule yake kwana acikin gidan akodayaushe sukayi wanka tare,,, sannan tayi musu breakfast tea da bread suka karya.
Bayan sun gama karyawa ne kowanensu ya shirya cikin sabbin kayansu mai k'yau,,, sannan Sule da Gwamma sukazo har bakin k'ofar gidan zatayi masa rakiya,,, suna zuwa bakin k'ofar Sule ne ya dubeta cikeda so da yaudara yace "farin cikin rayuwata mi kike buk'ata ne,,,, Idan zan dawo in sayo miki ?".

Gwamma tayi murmushi tace "zumana ka siyomin kifi mara k'arni da lemu da ayaba,,, sannan ka biya wurin Iya Abu mai saida langab'u ka sayomin shi ".

"hmmm duk a ina zaki saka wad'annan abubuwan da kika lissafo?,,,mata dai akwai ku dason cin dad'i da kwad'ayi".Cewar Sule cikin zolaya da wasa.

Gwamma ta hararesa da wasa sannan tace "duk acikin cikina kaidai ka sayomin babu ruwanka,,, muradinka dai kada nak'i ci ya lalace a banza aiku maza bakuda son dad'i ko kad'an sai d'aci ".

"ke ni ban iyawa da masifarki wasa nake nakeyi miki,,, zan siyo miki duk abinda kike buk'ata Gwammata,,, ai bakisan yadda nake sonki ba saboda haka ki daina shakku akan zan sayo ko bazan sayo ba ".Cewar Sule cikeda matuk'ar lallashi da dad'in baki.

Gwamma tace "to naji yanzu dai kayi magana mai ma'ana sosai ".

Sule yace "to ni dai yanzu zan wuce saina dawo ko ".

"to saika daw...... ".Bata k'arasa maganar ba saiga Lawwali yayi musu sallama,,, Sule ya amsa masa cikeda fara'a da murna sosai yayinda Lawwali ya dubesa ya tamk'e fuskarsa alamar bayason wata magana da Sule,,, Sule ya hango k'iyayyarsa acikin idanun Lawwali saboda haka batare da b'ata lokaci ba yaja k'afafunsa yayi wucewarsa zuwa inda zaije,,, Gwamma kuwa tana ganin irin kallon da Lawwali keyiwa Sule dole itama tasha masa toka tareda da yi masa jagora zuwa cikin gidanta.

Suna shiga cikin gidan ta d'auko tabarma ta shimfid'a masa,, tareda da kawo masa ruwa masu sanyi cikin jug,,, Lawwali ya zauna saman tabarma tareda yin bismillah sannan ya dubeta duba na fahimta da natsuwa yace "yaya Gwamma mun yini lafiya,,, ya bayan rabuwa? ".

"lafiya k'alau bayan rabuwa kuma ai kasan inda nike baka nemeni ba,,,, sai yau ka tuna dani ashe dai naka naka ne duk yadda ya lalace ".Cewar Gwamma cikeda jin haushin maganarsa .

Lawwali yaja dogon numfashi yace "Allah ubangiji ya huci zuciyarki yaya Gwamma,,, niba tashin hankali ya kawoni wurinki ba magana ce mai matuk'ar muhimmanci da amfani ta sanya nazo gareki,,, sannan kuma ai nasan hannunka  bai tab'a rub'ewa ka yanke kayarsuwa ".

"to ina saurarenka mi yake tafe dakai? ".Inji Gwamma.

Lawwali ya nisa yace"da farko dai inason komai zakiyi a duniya ki sanya tsoron Allah azuciyarki,,, sannan duk abinda mutum zaiyi arayuwarsa yasan Allah ubangiji yana ganinsa koda lullub'e yake acikin rami,,,, shaidun duniya shine shedun lahira yaya Gwamma aikata alkhairi komai k'arancinsa arayuwarki ta duniya ki guji aikata masha'a komai k'arancinsa,,, amatsayina na d'an uwanki kuma k'ane agareki ya zamo dole in sanardake gaskiya koda zakiji haushina ki tsaneni,,, koda hakan zai zamo silar b'acin ranki abinda kike aikatawa acikin garin nan dai bai kamata ba,,, sana'ar maita bata dace dake ba !Ko'ina acikin gari maganarki kawai akeyi ana cewa ke *MAYYA CE* sannan abin takaici da bak'in cikin rayuwa gashi yanxu na gani da idona har namiji kike kawowa acikin gidan nan kuna aikata abinda kuka gadama,, ansha kawomin gulma da jita jita amma ban yarda ba gaskiya sai yanzu ,,,,ki ji tsoron Allah domin ina guje miki yin mummunan k'arshe! Duniya bakiji wani dad'i ba hakama lahira ba zakiji dad'i ba ".

Gwamma ta hararesa tareda jan mugun tsoki mtsssss! Sannan tace "ka gama tsohon munafiki wato an turoka ne domin kazo ka cimin mutunci ko,, wallahi kam baka  isa ba kayi d'an k'arami da kai Lawwali maita kuma bazan daina ba! Duk ubanda zaka gayawa jeka gaya masa bana

tsoron uban kowa ciki kuwa harda kai! Shege wanda baisan d'an uwa ba ".

Lawwali yayi hucin mai cikeda takaici da bak'in cikin Gwamma,,,sannan yace "Alal hak'ik'a na k'ara tabbatarwa da wanda yayi nisa bayajin kira acikin aikata masha'a da mummunan dabi'a,,, daga fad'in gaskiya ayau shine zaki cimin mutunci ki nunamin ni ban isa in gaya maki gaskiya ba,,, Allah ubangiji ya shiryeki yasa ki gane gaskiya gaskiya ce kuma k'arya k'arya ce ".

"aini ashirye nake kuma kowa shiriyar Allah yake nema bata mutum ba,,, ehehhh maita ce da kuma yin zina bazan daina ba koda kuwa mutum zai fad'i k'asa ya mutu har lahira! ".Cewar Gwamma cikeda jin haushin maganarsa da bala'i..

Lawwali yace "to yayi miki k'yau matuk'a duk dai abinda kikeyi marasa k'yawo,,, Allah yana sama yana kallonki kuma shi zai musu sakayya tun anan duniya ina k'ara tabbatar miki muddin baki daina aikata miyagun ayyuka ba,,, karshenki bazaiyi k'yawo ba !".

"kar yayi k'yau d'in ina ruwanka idan har nayi mummunan k'arshe? To idan aljanna taka ce ka hana in shigeta,,, kuma tun yanzu kazo kasa inyi mummunan k'arshe mara mutunci wawan banza dolo wanda babu tunani da nazari acikin kansa ".Inji Gwamma cikin takaici da haushi..

Lawwali ya tashi tsaye yana cewa "to tunda bak'yajin nasiha na k'yaleki,,, kije kiyita aikata duk abinda kika gadama babu abinda ya shafeni! ".Yana k'arasa maganar yayi tafiyarsa batare da ya tsaya ya saurarin irin martanin da zata mayar masa ba.

"aikin banza yima karen mak'wabta wanka mtssssssss kai har ka isa kace zakayimin wa'azi ko nasiha,,,, to wallahi ka kiyayeni idan ba haka ba barin ganin uwarmu d'aya ubanmu d'aya ina iya kasheka in cinye namanka d'anye! Kuma ba'a komai babu maija dani Gwamma mayya ".Inji Gwamma ta kama sambatu tana zage zage na cin mutunci da tozarci.

¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤

Baba Labbo ne zaune da Inna Tani suna fira cikeda matuk'ar farin ciki da nishad'i sosai,,,

saboda su yanzu Alhmdlilah babu abinda suka nema suka rasa komai su Sagiru kawo musu sukeyi,,,, na dangane kayan masarufi da mak'ulashe abinci kala kala sukeyi wani buhun shinkafa,,, masara,,,wake da dai sauran kayayyakin abinci wani saiya tadda wani,,, nama sai sun ture da kuma kayan marmari..

Inna Tani ta karkace baki tace "Hhmmm maigida ashe dai Gwamma ta zama k'usurgumar mayya,,, shiyasa rannan ta zama macijiya ta koraka daga cikin gidan yayanka ".

Baba Labbo yace "aike wallahi lamarin akwai ban mamaki da al'ajabi da maigari yana gaya mana,,, ba kiga irin yadda mutane suka rikice suna hawaye ba!Wai ashe ta zama babbar mayya tafima uwarta shahara ".

"ai Allah yasa kanada k'arar kwana agaba da yanzu Gwamma macijiya ta lak'umeka zama guda,,, ni wallahi abin har mamaki yake bani wai cin naman mutane takeyi ".Inji Inna Tani tana kallon baba Labbo tana masa dariyar k'eta.

Baba Labbo yace "haka ne gaskiya da yanzu ina can  cikin kabari kwance,,, aini yanzu ko bakin k'ofar gidan nan bazan iya k'ara giftawa ba saboda in tsira da rayuwata ".

Inna Tani ta bushe da dariya sosai tace "maigida akwai ka da tsoron bala'i,,, ai b'oye b'oye baya maganin mayyu saboda ko'ina kake suna ganinka,,, addu'a itace maganin mayyu kuma takobin mumini ce "............

_Share&Comments_😘
[7/6, 5:42 PM] Mugiratmusa66: 🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥
*MAYYA CE*
🍥🍥🍥🍥🍥🍥

🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥

*INTELLIGENT WRITER'S ASSOCIATION ®*✍🏻
_[Onward together]_

*Written by Mugirat Musa*

*DEDICATED TO SIS NAJER'ART*

_Bismillahir rahamanir rahim_

*PAGE 26*

"Addu'a itace maganin mayyu kuma takobin mumini ce,,,, sannan mace mai yara k'anana da basu iya yin addu'a ba,,,, ya zama dole ta dinga yi musu addu'o'in neman tsari tana shafe musu jiki akodayaushe,,,, ba wai mace ta nuna son jiki ko k'yuya ba ".Inji Inna Tani,,, "tabbas maganarki gaskiya ce Tani,,, babu yadda zaka saki baki bakason yin addu'a sannan kace wani abin cutarwa bazai tab'a cutarka ba ".Cewar baba Labbo yana murmushi,,, Inna Tani ta dubesa tace "aini yanzu lamarin duniyar nan tsoro yake bani sosai,,, yanzu kaga mutum lafiya k'alau jibi ace maka ya zama mayye cin naman mutane yakeyi ko takeyi ".Baba Labbo yace "kwarai da gaske ma ai kinga yanzu idan da ace Gwamma lafiyarta k'alau,,,, bai dace ace na barta zaune ita kad'ai tana aikata abinda ta gadama ba ,,,,saboda naji ance yanzu har namiji yake shigowa cikin gidan nan yana tayata kwana,,, to daga barcin tare da k'ato saimi zai faru? Sai iskanci da abinda ba'a so shine zai iya biyowa baya "."Af ai iskanci da yin maita yanzu ya zama ruwan dare,,,,, saboda yanzu yanada wuya kaga wanda baya aikata d'aya daga cikin wad'annan abubuwan dana ambata,,,,, kaga kuwa saidai mu dage da yawan yin addu'a akan Allah ubangiji ya karemu daga muyagun k'addarori muda iyalanmu ".Inji Inna Tani cikeda matuk'ar sanyin jiki

da natsuwa,,, baba Labbo yace "amin ya rabbi Tani lamarin mutanen yanzu sai a hankali,,,, ai Gwamma ta koyar dani darasin rayuwa idan kace ka faye shiga cikin abinda bai shafeka ba,,,, matsalolin rayuwa mutum zai jefa kansa ciki kuwa "."Hmmm maigida kenan wata rana kana bani mamaki sosai,,,, ai duk abinda ya shafi Gwamma ya shafeka saboda koba komai 'yar yayanka ce uwa d'aya uba d'aya ba lafiya bane,,, sannan kuma ko kwatance za'ayi sai dai ace yanzu d'iyar Mamman da Talatu,,, Mamman yayan Labbo mijin Tani mai wake kaga kuwa anan hannunka bai tab'a rub'ewa ka yanke kayar ,,,,ka dai k'yaleta ne saboda kaima tafi k'arfinka ne,,,, amma ako'ina akaje kaine ya kamata ka rik'eta amatsayinta na marainiya domin kaine dolenta ".Baba Labbo yayi dariya yace "babu k'arya a cikin maganarki Tani shiyasa nake k'ara sonki,,, saboda kinada natsuwa da hangen nesa Allah ubangiji yayi miki albarka kuma ya barmu tare "..

Inna Tani taji dad'in addu'arsa k'warai da gaske,,,, wani farin ciki da nishad'i ne ke wanzuwa acikin sassan jikinta gaba d'aya,,, tayi murmushi tace "amin amin maigidana ".

Firarsu suka cigaba da yi mai dad'i da ma'ana sosai,,, daga ganin yadda suke gudanar da rayuwar aurensu babu abinda suka nema suka rasa a cikin zamantakewarsu...

********************

***Aliya ce matar Lawwali zaune tana tankad'ar garin tuwo,,, ga d'iyarta nan mai suna Hajara tana wasar k'asa agefe,,,, ita kuma uwar ta mayarda hankalinta kacokam wurin aikinta,,, can

bada jimawa ba saiga sallamar Lawwali ya shigo cikin gidan,,, fuskarsa murtuk'e babu alamun fara'a ko walwala ana hango b'acin rai acikin k'wayar idanunsa ,,,,Aliya dai ta amsa masa sallamarsa cikin sanyin jiki ta kawo tabarma ta shimfid'a masa cikeda ladabi da girmamawa,,,, bayan ya zauna ne ta kawo masa ruwa masu sanyi cikin kofi ya d'auki ruwan yasha,,,, sannan yayi ajiyar zuciya yace "Alhmdlilah Allah ubangiji yayi miki albarka ".

Aliya tayi murmushi tace "amin baban Hajara amma mi ye yasa ka shigo cikin gida da b'acin rai?Har baka iya b'oye b'acin ranka kafin ka shigo cikin gida ".

Lawwali yaja dogon numfashi sannan yace "kede bari Aliya abin ne akwai matuk'ar b'acin rai da ban takaici,,,, wai nine zanje wurin yaya Gwamma in bata shawara akan abinda take aikatawa bai dace ba,, shine ta kama yimin fad'a da cin mutunci abin babu dad'in ji balantana saurare ".

"ayyah baban Hajara hak'uri zakayi domin koba komai itace sama da kai,,, kuma yayarkace kaine ya zama dole kayi mata biyayya kuma shiriya tana hannun Allah,,, da kad'an kad'an sai kaga ta daina yin duk abubuwan da takeyi ".Inji Aliya cikeda matuk'ar lallashi da ladabi..

Lawwali ya nisa yace "Aliya kenan bakisan ainahin halayyar yaya Gwamma ba,,, mace ce mai matuk'ar taurin kai da tsattsauran ra'ayi kuma duk abinda ta sama gaba komai rashin k'yawonsa,,,, ba zata daina ba yanzu ma bari in sanardake gaskiyar lamari maigari yace idan aka kama mayyu akashesu! Sannan Ummaru d'an Sala mafarauci yawon nemanta yakeyi ruwa a jallo saboda itace ta kashe masa iyayensa da yayan babansa,,,, ta cinye namansu ni kuwa ina jiye mata mummunan k'arshe da mugun hukunci ".

Aliya tace"hmmmm amma kam wannan hukuncin yayi tsauri da yawa gaskiya,,,, ana kama mutum kenan ana kashesa! To ka cigaba da hak'uri kana zuwa kana lallashin yaya Gwamma har ta daina maita,,, kafin hukuncin maigari ya hau kanta akasheta abar mana abin gori da fad'a,,, surutu,,, gulmace gulmace ko munafurci ".

"abin gori da surutu na nawa kuma saboda ni idan na fita waje,,, har nunani akeyi ana zund'ena da nunena da cewa ga k'anen Gwamma mayya can tafe,,, wasu ma har guduna sukeyi wai saboda basu yarda niba mayye bane domin Innarmu wai gadon maita tabar mana! ".Cewar Lawwali cikeda matuk'ar takaicin yadda rayuwar Gwamma ke tafiya tana cin naman mutane da aljannu!.

Aliya tace "hak'uri zaka k'ara yi ai mutane iyawa dasu sai Allah,,, sannan ya zama dole ka toshe kunnuwanka daga jita jitar mutane da tseguminsu,,,,,,saboda haka ka daina damuwa akan anyi ance da surutun mutane ".

"idan banyi hak'uri ba mi zanyi musu? Kedai Allah ubangiji ya sawwak'a yasa mu dace ".Inji Lawwali..

Aliya tace "amin baban Hajara Allah ubangiji ya sanyaya maka zuciyarka ".

Aliya ta cigaba da yi masa kalamai masu dad'i,,, sannan kuma ta k'ara nuna masa muhimmanci hak'uri da juriya akan zamantakewar rayuwar duniya,,,,, ta dinga lurar dashi ya dinga toshe

kunnuwansa daga jita jitar mutane......

Allah ubangiji yaba kowa abokin rayuwa nagari..

¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤

*BAYAN SHEKARU HUD'U*

Abubuwa da dama sun faru ciki kuwa harda kama sauran mayyu,,, da suka addabi rayuwar mutane ana kashewa,,, Ummaru ya kama mayyu kusan ishirin yana kashewa acikin wad'annan shekarun da suka wuce,,, yayi yayi ya kama Gwamma shahararriyar mayya amma ya kasa saboda ita yanzu ta k'ara shahara da gunguma akan harakar maita! Duk wanda takeso take kwad'ayin namansa kamesa kawai takeyi,, duk da yake Lawwali yayi zuwa kusan goma yana yi mata nasiha akan ta daina maita! Amma wanda yayi nisa bayajin kira sai dai taci masa mutunci tana zaginsa,,, zuwa na goma da yayi tayi masa kashedi da inya k'ara takowa gidanta da sunan wa'azi saita kashesa ta cinye namansa! Yabar ganin uwarsu d'aya ubansu d'aya,,, jin ta fad'i haka dole yasa Lawwali yajawa k'afafunsa linzami ya daina zuwa kwata kwata saboda yasan duk abinda Gwamma tace tanayi,,, to tabbas zata iya aikatawa domin yasan halinta batada tsoro tanada dakakkiyar zuciya.

To acikin wad'annan shekarun ne Gwamma ta haifi 'yan biyu mace da namiji da Sule saurayinta,,, namijin sunansa Hassan macen sunanta Suhaila,,, bayan yaran sun fara girma da tasawa taga ai amfanin Sule ya k'are koba komai tagama morarsa,,, gashi taga yanzu shima har nasiha da wa'azi yakeyi mata akan ta daina maita! To ita kuma da mutum ya dameta akan tabar maita gara yahau risho da wandon leda,, ganin da tayi Sule yana neman takurawa rayuwarta yasa dole ta kame masa kurwa  ta mayar ita zakara,,, arannan ne ta yanke zakaran ta cinye abinta tasha ruwa tayi gyatsa.

_Ina lillahi wa inna ilaihirraji'un! Allah ubangiji ya rabamu da aikata masha'a da kuma biyewa *SON ZUCIYA*..._

Aka wayi gari Sule ya mutu abin kamar almara,,, akayi masa wanka aka kaisa makwancinsa na gaskiya,,, Allahu Akbar duniya ba matabbata bace duniya mai cikeda bak'in ciki da k'uncin rayuwa,,, Gwamma ta cigaba da gudanar da rayuwarta cikeda kwanciyar hankali da jin dad'i,,,tareda da kula da yaranta cikeda matuk'ar k'aunarsu batason ko k'uda ya tab'asu idan da son ranta ne,,, babu abinda take so da k'auna fiyeda yaranta.

Ita dai cigaba da cin naman mutane dana aljannu kawai takeyi wata rana ta mayarda kurwar mutane zakara ko rago taje can kasuwar wani gari,,, inda ba'a santa ba tana samun kud'inta cikeda wayo da 'yan  dabaru ta haka ne take samun kud'ad'e tana ciyarda yaranta da kashewa kud'i .......

_Share &Comments_
[7/6, 6:05 PM] Mugiratmusa66: 🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥
*MAYYA CE*

🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥

*INTELLIGENT WRITER'S ASSOCIATION ®*✍🏻
_[Onward together]_

*Written by Mugirat Musa*

*DEDICATED TO SIS NAJER'ART*

_Bismillahir rahamanir rahim_

*PAGE 27*

**Ta haka ne take samun 'yan kud'ad'e tana kashewa da kuma kula dasu Hassan,,, haka dai take gudanar da rayuwar gidan da maitarta,,,, Lawwali kuma ganin irin walak'anci da korar kare da Gwamma tayi masa ya watsar da ita gaba d'aya ya fita harakarta,,, saboda yasan tunda ta bud'i baki tace zata kashesa to tana iya kashesa abanza da yofi yabar yaransa da matarsa cikin k'unci da tsananin maraici,,,, baba Labbo ne dama ya tsorace gameda lamarin Gwamma mayya,,, domin tun lokacin da yaje domin ya dawo da ita gidansa ta rikid'a ta koma macijiya ta koresa,,,,,to tun daga lokacin nan bai sake giftawa ko bakin k'ofar gidan nan ba,,,, balantana yaje ya shiga cikin gidan kunsan yadda baba Labbo yakeda masifar tsoron mutuwa da mayyu!. Ummaru mafarauci dai yana nan yana cigaba da bibiyar duk wani motsi na Gwamma,,, sannan duk inda taje yana hankalce da ita yana kallonta babu inda zataje ko tayi wani motsi ba'a kan idon Ummaru ba,,, ya damu sosai ta yadda take azabtar da mutane da cin namansu amma ya gagara kamata! Shiyasa dole wata rana yayi zaune yana tagumi da bak'in cikin rashin kama

Gwamma mayya,,, domin zaluncinta da cin amanar mutane sai k'aruwa yakeyi,,, bata tunanin abinda zaije ya dawo a rayuwa bata tunanin ai wata rana dubunta zai iya cika,,, bata tunanin wata rana zata bar duniya baki d'aya taje can ta girbi abinda ta shuka? Ita dai Gwamma gatanan dai kamar ba mutum ba zuciyar nan babu d'igon imani da tausayi,,, ta k'ek'eshe zuciyarta daga barin tsoron kowa bata gudun abinda zai faru,,, bata tunanin kamar yadda aka kama sauran mayyu 'yan uwanta to ita ana iya kamata!.
Mutanen gari kuma kowa ya shiga taitayinsa,,, saboda kada su afka cikin tarkon Gwamma mayya,,,, kowane daga cikinsu ya tashi tsaye tareda dagewa da yawan addu'ar Allah ubangiji ya kawo musu k'arshen zaluncin Gwamma,,, domin susan Ummaru yana iya bakin k'ok'arinsa na ganin ya kamata amma abin yaci tura! Ya kasa kamata saboda yadda takeda k'arfin sihiri da gunguma acikin harakar maita,,, kunsan ta zarce mahaifiyarta Inna Talatu awurin shahara da bunk'asa domin ita har aljannu tsoronta sukeji balantana bil Adama,,,, bata shakkun tunkarar kamun kurwar kowa acikin garin Gumi,,, Ummaru kawai ne take d'an tsoronsa domin kada wata rana dubunta ya cika ya chafketa!.

¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤

Ummaru ne zaune yayi tagumi cikeda matuk'ar bak'in ciki da damuwar rashin kama Gwamma,,, ya rasa yadda zaiyi ya kamata.

Salma ce ta jaye hannun Ummaru daga yin tagumin da yakeyi,,, sannan ta dubesa tace "lafiya baban Husna kana tagumi?Babu k'yawo ka daina sama kanka damuwa ".

Ummaru ya d'ago idanunsa da sukayi jawur akan  damuwa,,, yace "Salma ina cikin damuwa wai ace wadda tayi sanadin mutuwar iyayena da baba Labaran,,, na kasa kamata sai yawo da hankali takeyimin ta mayardani mahaukaci ko mara sa'a a rayuwa ".

Salma ta kallesa cikeda matuk'ar tausayawa da k'auna matuk'a,,, tace "haba farin cikin rayuwata miyasa zaka damar da kanka,,,akan abinda akodayaushe akowane lokaci kana iya kamata,,,kai bakasan komai yanada lokaci da k'addara ba? Idan Gwamma ce zaka kamata duk ta gama guje gujenta da b'oye b'oyenta sai dubunta ya cika! ".

"ni ba haka naso ba so nayi in kamata yanzu in gana mata azaba,,, sannan daga baya in kasheta kamar yadda ta kashemin iyayena! ".Cewar Ummaru d'an Sala mafarauci.

Salma tace "kayi hak'uri maigidana zaka d'auki fansar jinin mahaifanka,,, kuma ka daina saka damuwa da tunanin abinda bana damuwa ba,,, ni nasan komai daren dad'ewa zaka kama Gwamma ka kasheta har lahira! Lokaci yana nan zuwa ka daina damuwa ".

Ummaru yace "to babu damuwa Ummu Husna,,,, zan daina saka damuwa acikin raina da zuciyata ".

"da kam yafi baban Husna ka saki zuciyarka,,, komai yanada lokaci kuma zaizo ya wuce kamar ba'ayi ba ".Cewar Salma cikeda matuk'ar lallashi.

Ummaru yace "tabbas haka ne gaskiyar maganarki ".

Salma ta cigaba da bashi maganganu masu sanyi,,, da kuma lallashinsa da yayi hak'uri akowane lokaci zai iya kama Gwamma..

********************

**Bayan shekaru goma ne alokacin ne  su Hassan suka girma,,, sunada shekara ashirin da uku,,,, Suhaila ta samu miji mai k'aunarta tsakani da Allah ya aureta,,, amma saida suka kafta tashin hankali da bala'i da Iya Gwamma domin nuna tayi ita ba zata aurar da Suhaila ga Salihu ba,,,, shi kuma dayake yana sonta itama tana sonsa shiyasa ta nace saita auresa,,, babu irin kashi da zagin da Suhaila bata sha ba akan son da takeyiwa Salihu saboda itama Gwamma so takeyi ta gajeta a cikin maita! Ita kuma tak'i bin umurninta domin bataga wata ribar da mayyu suke samu ba idan suka zama mayyu,,, ganin irin haka ne yasa shima Hassan ya bid'i kud'in aure ya fara kasuwanci,,, ya nemi wata Aisha nan mak'wabciyarsu yayi aurensa,,, sannan ya kwashi matarsa ya samu wani gida madaidaici ya saye suka shige shida matarsa hankalinsu kwance..

Iya Gwamma ganin d'iyanta sun watse sun barta akan bala'inta da masifarta,,,, rana guda ta kama zaginsu tare da tsine musu albarka su suna can gidajensu basusan abinda yake faruwa ba,,,,, to dayake batada rik'o arayuwarta nan da nan ta fita harakar d'iyan tareda cigaba da cin naman mutane da aljannu,,, babu tsoron Allah ko kad'an a cikin zuciyarta..

¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤

*CIGABAN  LABARI*

Mama Sa'ima da Alhaji Suleiman ganin yawon Maryam yayi yawa,, dole yasa uwar take sakawa 'yarta idanu da hana mata yawon zuwa ko'ina idan ba makaranta ba,,, saboda gudun kada mayyu su kamata basusan sun riga sunyi fad'a da Iya Gwamma k'usurgumar mayyar da ta addabi rayuwar mutane shekara da shekaru ba,,, Ummaru ya kasa kamata alamar sai taci zamaninta,,, shi dai bai hak'ura ba yana nan yana bibiyar rayuwarta kuma yasan yanzu duk d'iyanta sun gudu sun barta,,, saboda mummunan dabi'ar da take aikatawa wato yin maita da rikid'e rikid'e da tsafe tsafen da bayada k'yau ko addinin musulunci..

Mama Sa'ima ce zaune tana tsintar k'asa acikin shinkafa,,, Mubarak yana zaune gefenta yana tayata suna fira cikin natsuwa da kwanciyar hankali..

Alokacin ne Mubarak ya dubi Mama Sa'ima yace "amma yau ana zafi sosai agarin nan,,, baba yana can kasuwa kuwa gashi akwai rana sosai ".

"zafi ai lokacinsa ne Mubarak ai fita kasuwa ya zama dole ga Alhaji,,, saboda kaga yanzu idan bai fita ba yaran yanzu masu tsaron shago ba kowanensu keda amana ba,,, sai 'yan kad'an daga cikinsu sukeda amana da gaskiya ".Cewar Mama Sa'ima.

Mubarak yace "ai Alhaji yanada hak'uri da juriyar zama da mutane,,, musamman idan mutum ya samu masu tsaron shago ko marasa gaskiya sai yakai zuciyarsa nesa ko ya koresu".

Mama Sa'ima tayi murmushi tace "ai zaman duniya iyawa ne gaskiya idan baka iya zama da mutane sai zama ya gagareka da mutane,,,,, mutum yazo yana fad'a da mutane kowa ya tsanesa,,, ai rayuwar da kake ganinta gaba d'aya sai mutum yayi hak'uri da juriya a rayuwa ".

"haka ne gaskiya Mama ni abinda yake bani tsoro da takaici shine,,, yadda zamanin nan namu ya lalace kowane ka gani ya zama mayye ko mayya,,, saboda tsananin kwad'ayi da son abin duniya da dogon buri! Ni abin yana cimin tuwo a k'warya bansan yadda abubuwan suke faruwa ba? ".Cewar Mubarak cikeda jimamin abinda ke faruwa cikin gari.

Mama Sa'ima tayi murmushi taja numfashi,,,, sannan tace "ai lamarin mayyu sai addu'a saboda yafi k'arfin Al'umma,,, saboda haka koni abin yana damuna babu yadda zamuyi sai hak'uri akan lamarin mayyu! Sai addu'a da neman tsari daga sharrinsu".

Mubarak yace "Allah ubangiji ya karemu daga sharrin masu sharri a cikin mutane da aljannu ".

"Amin ya rabbi Mama ".Inji Mubarak.

*BAYAN KWANA BIYU*

Bayan faruwar wannan al'amarin tsakanin Iya Gwamma dasu Fatima,,, na rashin mutuncin da Fadila tayiwa Iya Gwamma saiya zamo iyayensu Fatima sun hana musu zuwa ko'ina kamar yadda aka hanama Maryam,,,, domin aran nan da suka kama yiwa su Fadila fad'a kamar zasu dokesu  da yake Fatima tanada tsoro sosai shine ta sanardasu irin abinda ya had'a su da Iya ta aikesu,,, da kuma rashin kunyar da Fadila tayi mata duk saida ta gaya musu.

To sunsha fad'a sosai rannan akan rashin kunyar da Fadila tayi ma Iya Gwamma,,,,, kamar abasu mugun kashi saboda abinda Fadila tayima Iya Gwamma,,,,,Fadil yayan Fadila kamar ya bata kashi akan rashin kunyar Fadila tayi yawa da kuma tsiwarta..

Amma Iyayennasu mata suka hana ya bugeta saboda sunsan bugu baya horar da yara,,, sai dai addu'a da yawan jama yaro kunne ,,,to wannan maganar dai anan atsakaninsu Iyayen mata suka bar maganar,, basu sanarda Iyayen maza ba saboda sunsan sune da laifi,,, sannan su mazajen zasu yiwa fad'a kunsan ance laifin d'a baya wuce mahaifiyarsa.

Ana nan dai kwatsam! Fadila da Fatima rashin lafiya ya kamasu kusan atare,,, ita Fatima amai da zawo ne takeyi duk ta rame tayi bak'i sannan ta fige babu k'yawon gani,,, ita kuma Fadila ciwon zazzab'i da ciwon kai ne ya kamata sannan ga wasu k'ananan k'uraje nan da suka fara fitowa a jikinta,,,ciwon yayi matuk'ar ramar da ita yasa ta fita cikin hayyacinta k'warai da gaske,, Iyayensu hankalinsu yayi k'ololuwar tashi sosai,,, babu abinda sukeyi sai kukan zuci dana zahiri ga bak'in ciki da k'uncin rayuwa.........

_Share&Comments_
[7/9, 11:55 PM] Mugiratmusa66: 🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥
*MAYYA CE*
🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥

*INTELLIGENT WRITER'S ASSOCIATION ®*✍🏻
_[Onward together]_

*Written by Mugirat Musa*

*DEDICATED TO SIS NAJER'ART*

_Bismillahir rahamanir rahim_

*PAGE 28*

Babu abinda sukeyi sai kukan zuci dana zahiri ga bak'in ciki da k'uncin rayuwa,,, saboda suna matuk'ar k'aunar d'iyansu da gaskiya basa son ko k'uda ne ya tab'asu idan da son ransu,,, haka dai suka cigaba da jinyar yaransu tareda da basu kulawa ta musamman,,,, batare da sanin iyayensu maza ba.
Ab'angaren gidansu Maryam itama ta kamu da tsananin rashin lafiya sosai,,, wato ciwon ciki mai tsananin gaske da hanasu barcin dare shine Iya Gwamma mayya ta tura mata,,, alokacin da ciwon cikin ya fara tashi Mama Sa'ima da Mubarak hankalinsu yayi k'ololuwar tashi sosai ga zuciyarsu sai bugawa takeyi da k'arfi da k'arfi! Kallo d'aya xaka yi musu kasan basa cikin kwanciyar hankali da jin dad'i,,,idan ciwon cikin Maryam ya taso har shure shure takeyi da kukan zafi da rad'ad'in ciwo,,,, su kuma su Mama Sa'ima babu mai kama wani akan hawaye kuka kawai sukeyi cike da tsananin damuwa da bak'in cikin rayuwa,,, wata rana idan ciwon ya lafa mata harda wasa takeyi da cin abinci sosai,,, idan ciwon ya tashi kuwa haka zata kama yin fisge fisge da shure shure kamar mai aljannu har kumfa ke fitowa daga cikin bakinta,,, saboda tsananin bala'in sihiri da magagin ciwo,, kunsan wani ikon Allah shine dukansu Allah ya mantar dasu su sanar da Alhaji Suleiman irin ciwon da yake damunta,,, domin shi bayada masaniya akan komai duk lokacin da baya nan gida to alokacin ne ciwon Maryam ke tashi..

Aranar nan suna zaune gefe saman tabarma sunyi tagumi,,, ga hawaye sai kwaranya yake daga idanun Mama Sa'ima,,, shi kuma Mubarak idanunsa sunyi jawur kamar barkono saboda damuwa da bak'in ciki,,, alokacin ne ya bud'i baki dak'yar yace mata "Mama inaga fa matsalar nan ya kamata asanar da Alhaji duk abinda ake ciki gameda ciwon Maryam,, idan muka sanardashi nasan zaice muje asibiti idan mukaje can duk abinda ake ciki gameda ciwon Maryam zasu sanar damu,,, ko mi ne ne shawararki? ".

Mama Sa'ima ta fyace majina sannan tace "haka za'ayi Mubarak domin barin kashi a a ciki baya maganin yunwa,,,, kuma ya zama dole babanku yasan wannan abu ".

"nima shine na gani amma munyi shiru munata b'oyon ciwo,,, kamar bamusan zafinta ba idan shiru yayi yawa gaskiya wani ciwon yana iya shigowa  bamu sani ba ".Inji Mubarak cikeda jimamin rashin lafiyar k'anwarsa Maryam.

Mama Sa'ima ta nisa tace "duk abinda ka fad'a haka ne Mubarak,,, babu k'arya a cikin maganarka Allah ubangiji yaba Maryam lafiya da itada dukkan kullumin musulmi baki d'aya,,, amma ni agaskiya wannan ciwon nata yana matuk'ar bani tsoro da fargaba,,, sai ina ganin kamar ba ciwon Allah da annabi bane ".

"amin Mamanmu kiyi hak'uri karkice haka domin kada kiyi sab'on Allah,,, dukkan abinda kikaga ya samu bawa to muk'addari ne daga Allah,,, bawa bai isa ya cutar da d'an uwansa bawa ba sai yardar Allah mad'aukakin sarki,,, shiyasa akeson mutum ya kasance mai hak'uri da tawakalli akan lamuran duniya,,, da iznin ubangiji Allah Maryam zata samu lafiya ta warke garau kamar bata tab'a yin wannan cuta ba " .Cewar Mubarak cikeda da tunani da hangen nesa.

Mama Sa'ima tace "haka ne Mubarak Allah ubangiji ya k'ara mana juriya da hak'uri da kuma tawakalli da dukkan k'addarar da zata samemu,,, ita kuma Allah ya bata lafiya ".

Mubarak yace "Amin ya rabbi ".

Mubarak ya cigaba da kwantar mata da hankali,,, tareda bata hak'uri da kalamai masu sanyaya zuciyar mai sauraro..

*Allah ubangiji ya bamu d'iya nagari masu tausayinmu ,,,,da yi mana addu'a idan babu mu a duniya*.

********************

**Ummaru da Kabiru ne zaune suna firar duniya data mayyu,,, cikeda matuk'ar natsuwa da kwanciyar hankali..

Kabiru ne ya dubi Ummaru yace masa "abokina kana fa k'ok'ari sosai sai rage mana mayyu kakeyi a cikin garin nan,, amma har yanzu ka kasa kashe Gwamma mayya wadda ta addabi rayuwar mutanen gari da k'auyukkan dake kewaye damu ".

Ummaru d'an Sala mafarauci yace "hmmm Kabiru abin ba'a cewa komai wlh,,, kadai sha kuruminka da yardar Allah k'arshen Gwamma mayya ya kusa zuwa,,,, ai komai b'oye b'oyenta na kusa kamata in kasheta ai jinin mahaifana bazai tab'a zuba a banza ba ".

Kabiru yace "haka ne gaskiya ai ka rage mana annoba cikin garin Gumi,,, saboda ka kashe mayyu fiyeda d'ari kaga kuwa sauran da suka rage nasan basuda yawa sosai,,, ai barin irinsu Gwamma acikin Al'umma bala'i ne da tashin hankali! ".

"wama zai barta a raye cikin duniya,, ai idona idonta k'aryarta ta k'are,,, sainayi mata kisan gillah saina banbance mata tsakanin wuta da ruwa,,,, har abada babu tausayi ko rahama atsakanina da ita ".Inji Ummaru d'an Sala mafarauci cikeda tunanin rayuwarsa ta baya tareda

da iyayensa.

Kabiru ya dafa kafad'ar Ummaru cikeda tsananin tausayin abokinsa,,, domin shi har azuciya yana matuk'ar k'aunar Ummaru.

Sannan yace "kayi hak'uri Ummaru domin shi mai hak'uri wata rana zai cimma nasara da ribar hak'urinsa,,,,, sannan tabbas da yardar Allah zaka kashe Gwamma mayya kamar yadda ta kashe maka iyayenka! ".

Ummaru yace "na sani ai shiyasa kaga akullum akowane lokaci acikin shiri nake,,, domin bana fatar ranar ta riskeni ba ashirye ba saboda irinsu Gwamma shahararrun mayyu dole mutum yayi musu shirin tunkararsu na musamman ".

"wannan haka yake gaskiya ai rana dubu ta b'arawo rana d'aya tamai kaya ".Inji Kabiru.

Ummaru yace "haka ne tabbas ".

¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤

Ganin irin ciwonsu Fatima yak'i ci yak'i canyewa yasa,,, uwayen hankalinsu ya k'ara d'unguma sosai gabansu sai fad'uwa yakeyi yana bugawa rassssss! Rasssss!.

Umma Nusaiba ce ta dubi Mama Nafisa cikeda raunin zuciya da damuwa,, tace "Nafisa wannan ciwon yayi yawa fa ya kamata mu sanardasu baban Fadila domin akaisu asibiti da gaggawa,,, kada muyi shiru muzo mu rasa yaranmu akan zurfin ciki da gudun laifi wurin mazajenmu ".

Mama Nafisa ta d'ago idanunta da sukayi ja akan kuka da damuwa,,, tace "ai ya zama dole mu sanardasu komi domin gujewa afkawa cikin nadama da dana sani,,, ni wallahi yanzu k'irjina sai ciwo yakeyi ga wani abu daya tokare min k'irji mai nauyi,,, sai nake ganin kamar bazasu tashi ba mutuwa zasuyi! ".

"Subhanalillah! Nafisa ba'a yanke k'auna daga rahamar ubangiji kedai keyi fatar samun sauk'i da waraka,,,nima hankalina ba kwance yake ba amma ya zamuyi sai hak'uri da dangana,,, da kuma addu'ar Allah ubangiji ya basu lafiya ".Inji Umma Nusaiba cikeda matuk'ar sanyin jiki da damuwa.

Mama Nafisa tace "amin amin ya rabbi haka ne gaskiya lamarin duniya sai hak'uri da juriya ".

"bari adauko waya akira d'aya daga cikin  mazajenmu ".Cewar Umma Nusaiba ,,,,, ta tashi tsaye ta shige cikin d'akinta,,ta jima kad'an tana waya da baba Nura tana sanardashi abubuwan dake faruwa,,, baba Nura yace mata gashinan nan zuwa yanzu yanzun nan karta damu,,, tace to sannan ya katse wayar ita kuma ta fito waje tace "Nafisa ga baban Fatima nan tafe yanzu je ki shirya ki fito kafin yazo,, yana zuwa wucewa kawai zamuyi ".

"to yaya Nusaiba ".Inji Nafisa ta tashi tsaye ta shige cikin d'akinta domin ta shirya.

Babu b'ata lokaci su dukansu suka shiryo cikin kayansu masu k'yau,,, suka tsaya jiran baba Nura bada jimawa ba saiga sallamarsa shida Fadil sun shigo kusan atare suka shigowa daga cikin gidan matan suka amsa musu sallama ,, babu b'ata lokaci aka kwashi su Fatima aka sanya cikin motar baba Nura,,,Fadil ya shiga gaban mota su kuma su Mama Nafisa a bayan mota,, baba Nura yaja motarsa ya nufi hanyar zuwa asibiti..

Suna zuwa asibitin aka amshi su Fatima domin afara basu taimakon gaggawa,,, gadajensu suna kusaga juna itama Maryam har babanta da mamanta sun kawota asibiti,, baba Nura yana

ganin   Alhaji Suleiman suka yi musabaha suka gaisa cikeda matuk'ar girmamawa da nishad'i sosai..

Umma Nusaiba ce ta dubi Mama Sa'ima tace"a'aaaa Sa'ima kece a cikin asibiti,,, wa ye ba lafiya? ".

"hmmm Maryam ce babu lafiya wlh ".Inji Mama Sa'ima.

Umma Nusaiba tace "to Allah ubangiji ya bata lafiya mu kuma su Fadila da Fatima muka kawo basuda lafiya sosai ".

Sai da gaban Mama Sa'ima ya buga da k'arfi d'immmmm sannan ta tattaro dauriya tace "to 'yan uku duk sun kamu da rashin lafiya alokaci guda,,, Allah ubangiji ya basu lafiya yasa kuma ba abinda nake tunani bane ya faru dasu ".....
[7/10, 12:17 AM] Mugiratmusa66: 🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥

🍥
*MAYYA CE*
🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥

*INTELLIGENT WRITER'S ASSOCIATION ®*✍🏻
_[Onward together]_

*Written by Mugirat Musa*

*DEDICATED TO SIS NAJER'ART*

_Bismillahir rahamanir rahim_

*MAYYA CE FANS hak'ik'a ina godiya matuk'a da comment d'inku masu dad'i sosai,,, Allah ubangiji yabar k'auna da zumunci har abada nagode masoyana*

*PAGE 29*

Saida gaban Mama Nafisa ya buga da k'arfi rassssss! Hankalinta yayi k'ololuwar tashi sosai zuciyarta tana yimata k'una da tafasa,,,, ta mik'e tsaye cikeda matuk'ar fargaba da tashin hankali tace "ban gane mi kike nufi da Allah yasa ba abinda kike tunani bane ya faru? "."Nima kaina ya d'aure wlh,,, na kasa gane inda maganarki ta dosa ".Inji Umma Nusaiba cikin tsoro da fargaba akan rashin lafiyarsu Fadila. Mama Sa'ima tayi shiru na tsawon lokaci sannan can tayi doguwar ajiyar zuciya tace "yanzu kuwa zanyi muku bayani yadda zaku fahimta sosai,, ina nufin Allah yasa ba mayya ce ta kamesu ba saboda wannan lokaci na yanzu yanada hatsari sosai,,, musamman ga yara su rink'a fita yadda suka gadama batare da mayyu sun kamesu ba

"."Hmmm Allah ubangiji yasa ba mayya ce ta kamasu ba,,, dako mun shiga uku mun lalace! Wayyo ni Allah kaiconmu da wannan mummunan al'amarin daya samemu ".Inji Mama Nafisa cikeda da tashin hankali da *RUD'ANI*,,,,Umma Nusaiba tayi matuk'ar ajiyar zuciya da k'arfi! Tace "ina lillahi wa inna ilaihirraji'un! Dako haka ne gaskiya muna cikin matsalar rayuwa,,, saboda yadda mayyu suke addabar mutane agarin nan ya wuce misali,,, su kashe mutum su cinye namansa ba'a bakin komai yake ba "."karku damu idan Allah ya yarda abin zai zo mana cikin sauk'i sosai,,, zasu samu lafiya insha Allahu ".Inji Mama Sa'ima cikeda matuk'ar sanyin jiki da zullumi,,, Umma Nusaiba tace "to Allah ubangiji ya basu lafiya,,, ya kuma yaye musu abinda ke damunsu "."Amin ya rabbi ".Cewar Mama Nafisa cikin fargaba da zullumi..

*BAYAN KWANA UKU*

Jikinsu Maryam baiyi wani sauk'i ba gaskiya,,, saboda ciwon ya k'ara tsananta sosai sun k'ara bak'i da ramewa k'warai da gaske,, duk mai imani idan yayima su Fadila kallo d'aya saiya tausaya musu,,, musamman akan yadda ciwon yake hanasu barcin dare da iyayensu,,,, idan ciwonsu ya tashi har kuwwa da kururuwar zafin ciwo da rad'ad'i sukeyi! Duk asibitin gaba d'aya saiya gameda kuwwarsu da ifface iffacensu,,, kowa da yake asibitin saiya tausaya musu har zuwa ganinsu akeyi akan matuk'ar tausayawa rayuwarsu Fadila,,, ni kaina ganin yadda suka k'anjame da ramewa saida suka bani tausayi sosai,,, an canza musu yanayin kamanni sun koma kamar skeleton babu k'yawon gani,,, ganin haka ne yasa hankalin iyayensu mata da maza ya k'ara tashi fiyeda misali.

Suna zaune duk sunyi jugum sun fad'a duniyar tunani! Tashin hankali da bak'in cikin ne bayyane afuskokinsu k'arara saboda rashin natsuwa da kwanciyar hankali duk sun rame sosai. Can saiga doctor Sageer ya fito daga cikin office d'insa,,, yazo wurinsu Alhaji Suleiman dasu baba Nazifi ya kallesu na tsawon lokaci yana nazari can ya bud'i baki yace "Alhaji kaine baban

Maryam? "(dayake yasan Alhaji Suleiman tun dad'ewa ).Alhaji Suleiman yace "nine Likita bokan turai ".Sageer yayi murmushi sannan yace "to ina iyayensu Fatima Nura da Fadila Nazifi suke? ".Sukace"gamu nan "atare da juna.
"OK i want see you now all of you,,, muje office akwai maganar da nakeson in sanardaku mai muhimmanci ".Inji doctor Sageer bai tsaya jiran jin maganarsu ba,, ya k'ara gaba su baba Nura da Alhaji Suleiman suka mik'e tsaye sukace matansu su jirasu yanzu zasu fito,,,, su Mama Sa'ima sukace to babu matsala Allah yasa muji alkhairi,,, baba Nazifi yace "amin "suka nufi office d'in doctor Sageer da saurinsu.

Suna shiga suka iske doctor Sageer saman kujera ga takardu masu yawa asaman table,,, yana rubuce rubuce sallamar da sukayi ne yasa ya d'ago kansa ya amsa musu cikin sakin fuska da walwala,,, yayi musu bismillah dasu zauna saman kujerin dake cikin office d'insa suka zauna.

Yayi musu duba na fahimta da natsuwa sannan yayi ajiyar zuciya yace "Alhaji Suleiman ina fatar zaku saurareni da k'yau kuyimin fahimta na natsuwa da ganuwa,,, sannan kuyi hak'uri da irin kalaman da zasu fito daga bakina ".

Alhaji Suleiman ya dubi baba Nura,,, shima baba Nura ya dubi Alhaji Suleiman sannan sukace atare "insha Allahu zamu fahimceka sannan duk abinda Allah ya k'addara mai k'yau ne ".Shi dai baba Nazifi babu abinda yace kansa aduk'e yake,,, saboda k'irjinsa sai zafi yakeyi masa sosai ga wani irin zogi da rad'ad'i da zuciyarsa keyi masa.

Doctor Sageer ya numfasa yace "agaskiya ciwon yaranku bana asibiti bane,,, domin munyi bincike bincike ta hanyoyi da dama saboda mu gano kan matsalar ciwonsu ko bakin zaren,,, amma ciwonsu yak'i ci yak'i canyewa sai k'ara cigaba yakeyi saboda haka amatsayina na doctor ina baku shawarar,,, da kuje gida ku gwada na malamai ku gani ko za'a dace ".

"Alal hak'ik'a munji dad'in bayaninka da yardar Allah zamuje mu gwada na malamai ".Inji Alhaji Suleiman cikeda matuk'ar sanyin jiki da fargaba.

Baba Nazifi ya bud'i baki dak'yar cikin rashin kwanciyar hankali da tashin hankali! Yace "babu wani taimakon da zaka iya yi mana ayanzu ".

Baba Nura ya juyo ya dubi baba Nazifi yace "haba Nazifi miyasa bakada hak'uri ne,, bakaji bayanin da yayi mana bane ko baka gamsu da bayaninsa ba? ".

Doctor Sageer ya tari numfashinsu yace "kayi hak'uri Malam Nazifi insha Allahu idan kuka gwada na islamic za'a dace,,, kudai ku dage da yawan addu'a akan Allah ubangiji ya basu lafiya "."Amin amin doctor Sageer mun gode k'warai da gaske Allah ubangiji yabar zumunci ".Inji Alhaji Suleiman.

"Amin ".Cewar baba Nura doctor Sageer ya basu hannu d'aya bayan d'aya sukayi sallama da juna,,, sannan su baba Nura suka fice daga office d'insa.

Kai tsaye wurin matansu suka wuce direct batare da b'ata lokaci ba,, suka sanarda iyalansu an sallamesu daga asibiti sun fara had'a kayansu kenan saiga nurse Umaima ta kawo musu takardar sallama,,, daga wurin doctor Sageer itace ta tayasu suka gama had'a kayayyakinsu duka,,, sukayi mata godiya sosai sannan suka shige cikin motocinsu sunka nufi hanyar komawa gidajensu,,, cikin rashin kwanciyar hankali da jimamin ciwon yaransu.

¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤

Iya Gwamma ce ta aza tukunyar tsafinta tsakar gida,,,,tana ta tsubbace tsubbacenta ga wasu irin surutai da takeyi na sihiri marasa dad'in saurare da ji,,, wani irin tururin hayak'i da rugugin tsawa fasss fasss fasss! Ya bayyana da k'arfin gaske ga wata irin razananniyar guguwa ta taso da k'arfi ta game wurin yadda ko tafin hannu ba'a iya gani akan duhu! Idanun Iya Gwamma sukayi jawur kamar wuta halshenta ya zazzago ya k'ara tsawo kamar maciji,,, jikinta gaba d'ayansa gashi ya tsiro zago zago kamar dodanniya! Can dai guguwar ta tsaya cak ta daina yawo tsawa da hayak'i suka tsaya wuri d'aya,,, tayi nuni da hannunta zuwa cikin tukunyar wani irin bak'in abu ya shige cikin tukunyar batare da b'ata lokaci saiga photonsu Maryam ya bayyana k'arara acikin tukunyar,,, duk abinda ya faru dasu tun daga lokacin da ta tura musu ciwon da kuma kaisu asibiti da komai ma saida ta gani da idanunta!.

Wata irin mahaukaciyar dariya ce ta bushe da ita sannan tace"hhhhhhhh saini Gwamma d'iyar Talatu k'usurgumar mayya na rantse da jinin mahaifiyata da kuma gadon maita! Yara yanzu kuka fara wahalar  ciwo akan rashin kunyarku,,, musamman ke Fadila babu uban da ya isa ya hana in kasheki! In kashe ki!! In kashe ki!!! ".

Ta sake karanta d'alamisai na tsafi da sihiri,,, gidan gaba d'ayansa da tukunyar suka kama rawa da girgiza da k'arfi! Ga wata irin wuta jawur da ta tsago akan tsakiyar tukunyar can batare da b'ata lokaci ba boka LOK'ORO ya bayyana acikin  tukunyar yana k'yalk'yalar dariya sosai!.

Iya Gwamma ta dubesa tace "boka LOK'ORO jikina ya bani na kusa mutuwa,, ajalina ya kusa gabatowa gareni! Saboda haka saina kashe yaran nan guda uku kafin inbar duniya! ".

Boka LOK'ORO yace mata "tabbas haka ne gaskiya baki fad'i k'arya ba Gwamma,,, kin kusa mutuwa har abada nima nasan bazasu tab'a barina in rayu ba,,, saboda haka ki zama cikin shiri domin Ummaru d'an Sala mafarauci yana gab da tunkaroki domin ya kasheki ya d'auki fansar jinin mahaifansa! "Da wata shegiyar murya tasa kamar tusar kare.

"zan zama cikin shiri akodayaushe ya mai girma boka LOK'ORO,,, na rantse da gadon tsafi da maita! Shima Ummaru bazai tab'a iya kasheni cikin sauk'i ba saiya sha bak'ar wuya sosai a rayuwarsa wadda bai tab'a shan irinta ba! ".Inji Iya Gwamma mayya.

Boka LOK'ORO ya bushe da mahaukaciyar dariya yace "karki damu zaki basa bak'ar wahala kafin ya zamo ajalinki! Kedai kiyi taka tsan tsan da Ummaru d'an Sala mafarauci ".Yana rufe bakinsa photon dake cikin tukunya ya b'ace b'at kamar k'iftawa da bismillah.

"to ya mai girma boka LOK'ORO zanyi biyayya agareka zan kiyaye da duk irin abinda zai biyo baya ".Cewar Iya Gwamma cikeda shed'anci da ta'addanci.

*********************

Komawarsu Alhaji Suleiman gida yasa dole kowane daga cikinsu ya tashi tsaye,,, domin ganin sun nemawa 'ya'yansu magani saboda su samu waraka daga cutar,,, haka yasa sukayi ta kashin kud'i ana kawo musu magani na malamai iri iri daban daban,, to kunsan ciwo farat d'aya yake shiga samun sauk'i kuwa da sannu sannu yake shiga,, ganin haka ne yasa hankulan iyayen suka k'ara tashi sosai! Saboda ana shan magani amma ciwon sai k'ara anzama yakeyi,, su dukansu aman jini kawai sukeyi sannan basu iya tashi a tsaye a zaune suke kashi azaune suke fitsari babu k'yawon gani.
Haka iyayen nasu mata suke cigaba da kulawa dasu tareda zubar da hawayen bak'in ciki da k'uncin rayuwa,,, domin su kansu ciwon yaran har tsoro yake basu saboda aganinsu kamar ba zasu tashi ba mutuwa zasuyi,,, hmmm duniya ina zaki damu hak'ik'a ta'asar da mayyu sukeyi da kashe rayuka cikin Al'umma baki d'aya yayi yawa sosai,,, saboda su mayyu da kuke ganinsu basuda d'igon imani da tausayi ko kad'an a cikin zuciyarsu,,, komai suna iya aikatawa domin ganin burinsu ya cika,, jama'a mu kiyaye dan Allah mu yawaita karatun qur'ani da addu'a akan neman tsari daga shairin masu sharri,,, da iznin ubangiji Allah idan mutum ya kiyaye yawan addu'a da karatun qur'ani babu abinda mayyu ko aljannu zasu iya yiwa mutum da iznin Allah........
[7/10, 11:50 PM] Mugiratmusa66: 🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥
*MAYYA CE*
🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥

🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥

*INTELLIGENT WRITER'S ASSOCIATION ®*✍🏻
_[Onward together]_

*Written by Mugirat Musa*

*DEDICATED TO SIS NAJER'ART*

_Bismillahir rahamanir rahim_

*PAGE 30*

Da iznin Allah ba zasu iya cutar da mutum da komai ba,,, saboda haka mu kiyaye mu tashi tsaye da dagewa da yawan yin azkar,,,, da yardar Allah babu abinda zai iya cutardamu komai tsafinsa da sihirinsa.

Ciwon Maryam ya tsananta sosai ayanzu,,, duk da yake magani kala kala iri iri daban daban ake bata domin samun dacewa da waraka,,,, duk ta k'ara lalacewa da k'anjamewa babu k'yawon gani,,, Mama Sa'ima da Mubarak hankalinsu ya k'ara tashi matuk'a saboda irin wahalar da Maryam kesha akan wannan ciwo!.

Mama Sa'ima ce zaune tana shafar kan Maryam tana zubar da hawayen bak'in ciki da takaici,,, domin aganinta kamar ba zata warke daga wannan mummunan ciwon ba,,, Mubarak agefe yana lallashinta shima kansa idanunsa sunyi jawur jijiyoyin kansa sun tashi rud'u rud'u! Saboda rashin kwanciyar hankali da tashin hankali,,, amma ganin mahaifiyarsa tana kuka dole yasa ya b'oye damuwarsa,,, ya tattaro natsuwarsa cikin dauriya yace "kiyi hak'uri Mama ki daina zubar da hawayenki,,, babu abinda Maryam ke buk'ata yanzu idan ba addu'arki ba,,, sannan cikin tsanani akwai sauk'i komai mai wucewa ne insha Allah ".

Mama Sa'ima ta d'ago jajayen idanunta,,, b'acin rai da bak'in ciki ne k'arara akan fuskarta tace "ya zama dole in yi kuka Mubarak,,, idan Maryam ta mutu bansan yadda rayuwata zata iya kasancewa ba,, duk nice silar faruwar hakan saboda ban hanata fita ba alokacin da zataje wasa ba ".Ta sake fashewa da wani irin rikitaccen kuka mai cike da k'unci da bak'in cikin rayuwa.

"bakida laifi Mama ina son ki sani komai ya samu bawa muk'addari ne daga Allah,,, sannan wannan ciwo da ya samu Maryam *K'ADDARA CE* bakida laifi ko kad'an,, ya kamata ki daure ki sassautawa zuciyarki domin ki samu sauk'in rad'ad'i da zugin da kikeji acikin zuciyarki ".Inji Mubarak cikeda matuk'ar tausayin kansu da Maryam.

Mama Sa'ima tace "bawai ban yarda da k'addara bane Mubarak,, wallahi na yarda da k'addararmu amma har cikin zuciyata ina jin tsoron mayyu saboda zasu iya aikata komai,,, domin babu imani acikin zuciyarsu ".

Mubarak ya dafa kafad'arta yana share mata hawayenta,,, shi kansa zuciyarsa sai tafasa takeyi da k'una amma ya zama dole ya b'oye damuwarsa,,, agaban mahaifiyarsa domin kada ya k'ara tayar mata da hankali,,, shi kansa yasha b'oyewa acikin d'akinsa yana zubar da hawayen bak'in ciki da k'uncin rayuwa,,, ga tunane tunane da fargaba akan ciwon Maryam!.

Ya numfasa sannan yace "ki daina cewa haka Mama mayyu basu isa cutar da d'an Adam ba saida yardar Allah mad'aukakin sarki,,,, sannan inason ki daure ki dinga hak'uri akan wannan lamari,,, tabbas zata samu waraka ta warke kamar bata tab'a yin wannan ciwo ba ".

"Mubarak kenan nasan kana cikin damuwa,,, amma kake daurewa kana bani hak'uri tabbas kai mai albarka ne a rayuwa,,, sannan Alhaji yace zaizo da wani shahararren Malami mai suna Malam Usama,,, domin shima yayi nasa maganin ko za'a dace ".Inji Mama Sa'ima cikeda matuk'ar fargaba da zullumi!.

Mubarak ya nisa yace "za ma adace da yardar Allah dama ciwo farat d'aya yake shiga acikin jiki,,, lafiya kuma da sannu sannu take shiga jiki saboda haka ki kwantar da hankalinki,,, babu abinda zai faru sai alkhairin Allah ".

Mama Sa'ima taja doguwar ajiyar zuciya da k'arfi! Tace "haka ne gaskiya amma zan daure inga idan zan iya,,, domin kasan tsakanin uwa da d'a sai Allah ".

"tabbas haka ne Mama amma zaki iya daurewa domin gujewa kamuwa da wani ciwon ".Cewar Mubarak cikeda tausayi da *SOYAYYAR GASKIYA* na tsakanin uwa da d'a.

Mama Sa'ima tace "to zan gwada Mubarak ".

"dako kin k'yautamin mahaifiyata ".Inji Mubarak.

Mubarak ya cigaba da kwantar mata da hankali,,, tareda lallashinta yana gaya mata maganganu masu dad'i matuk'a,,, ita kanta taji bak'in ciki da rad'ad'in da takeji acikin zuciyarta ya ragu sosai saboda Allah ya bata d'a nagari na kowa..

¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤

Suma Fatima da Fadila ciwonsu ya k'ara tsananta sosai,,, duk da yake suna nan suna shan magani iri iri daban daban daga malamai kala kala,,, amma ciwon sai k'ara cigaba yakeyi,,, k'urajen da suka fitowa Fadila ajiki sun k'ara girma sosai sai wani ruwa ruwa yake fitowa daga jikinta mai shegen wari da d'oyi! Bakinta har wani kumfa yake fitarwa akodayaushe akowane lokaci idan ciwonta ya tashi.
Ciwon Fatima da Maryam yanada sauk'i bisa ga na Fadila! Saboda ciwon Fadila yafi tsanani da firgitarwa!.

Ganin haka ne yasa hankalinsu Umma Nusaiba ya k'ara tashi matuk'a!.

Mama Nafisa ce take zubar da hawayen bak'in ciki da takaicin rayuwa,,, idanunta har sun kumbura sosai akan kuka! Ga wani irin abu da takeji daya tokare mata k'irji,,, gabanta sai yawan fad'uwa yakeyi da k'arfi da k'arfi! Zuciyarta sai zafi takeyi mata sosai.

Shesshekar kuka takeyi tana cewa "wayyo Allah ni Nafisa mun shiga uku mun lalace! Ya zanyi da rayuwata da wannan mummunan al'amarin daya samemu ".

Umma Nusaiba tana jiyo kukanta da maganganunta ta fito daga sauri cikin kitchen,,, ta nufi wurin Mama Nafisa tana cewa "haba Nafisa,, haba Nafisa miyasa bakida hak'uri ne,,, miyasa baki yarda k'addara ba? Ai komai na duniya hak'uri akeyi da kuma dauriya akan abinda Allah ya k'addari bawa dashi ".

"wallahi yaya Nusaiba ba haka bane,,, zuciyata zafi da rad'ad'in ciwo takeyimin,,, hankalina yak'i kwanciya gabana sai yawan fad'uwa yakeyi,,, sannan jikina ya bani akwai mummunan k'addarar da zata samemu! Dan Allah ki fahimceni laifin zuciyata da gangar jikina ce! ".Cewar Mama Nafisa ta sake fashewa da wani irin rikitaccen kuka,,, mai ban tausayi da tsuma zuciyar mai sauraro.

Umma Nusaiba jikinta yayi matuk'ar sanyi da fargaba akan kalaman Mama Nafisa,,, ta faikaci idon Mama Nafisa ta share hawayen da yake fita daga cikin idanunta!.

Sannan ta tattaro natsuwarta da dauriya tace "kiyi hak'uri Nafisa dukkan tsanani yana tare da sauk'i,,, komai na duniya yanada farko yanada k'arshe hak'uri da yarda da k'addara shine jigon zaman duniya,, da yardar Allah zasu samu lafiya ".

Mama Nafisa tasa hannu ta share hawayenta,, sannan tace "shikenan yaya na daina kuka Allah ubangiji ya basu lafi.........."Bata k'arasa maganar ba suka jiyo kuwwa da kururuwar Fadila mai matuk'ar tashin hankali! Suka shek'a da gudu suka nufi d'akin dasu Fadila ke kwance,,, suna zuwa suka iske sai kumfa da jini ke fita daga cikin idanunta,,, sannan idanunta sai k'ak'k'afewa da juyewa sukeyi akan rad'ad'i da zafin ciwo,,, can dai Fadila ta bud'i baki dak'yar tace "Umma,, Mama duk abinda nayi muku zamana na duniya ku yafemin,,, sannan ku rok'armin gafarارsu baba su yafemin duk abinda nayi musu! ".Mama Nafisa ta saki wani irin gigitaccen kuka mai cike da k'unci da tarin damuwa,,, Umma Nusaiba ce ke zubar da hawayen bak'in ciki da k'uncin rayuwa ta matso kusaga Fadila ta rik'i hannunta tace "a'aaa Fadila ki daina fad'ar wannan magana bakiyi mana komai ba,, koda kinyi mun yafe miki cuta ba mutuwa bace "."dan Allah Fadila ki daina cewa zaki tafi ki barmu zaki warke da yardar Allah,, bakiyimin laifin komai Allah ubangiji ya tashi kafad'unki ".Cewar Mama Nafisa tana kuka sosai mai tarin yawa,, Fatima dake kwance tana kuka ta amsa ak'asan mak'oshinta "amin".Fadila ce ta juyo ta kalli Fatima tana murmushi sannan tace"ina sonki Fatima keda Maryam har abada kuna cikin zuciyata da ruhina,,, ku kasance masu biyayya da ladabi ga manyanku kada ku kasance masu rashin kunya da tsiwa nasan rashin kunyata ne yaja muku silar wannan ciwon,,, ku gafarceni ya k'awayena na tub......."Bata k'arasa maganarta ba tari ne ya sark'eta idanunta suka k'ak'k'afe suna rufewa da juyawa,,, can ta kama fisge fisgen fitar rai harta mutu Mama Nafisa tana ganin abinda ya faru ta fasa razananniyar k'ara da gigitacciyar kuwwa da k'arfi! Ta fad'i k'asa ta some Fatima dake cikin ciwo numfashinta ya d'auke da sauri akan tashin hankali da magagin ciwo!.

Umma Nusaiba ta saki gigitaccen kuka mai cike da rikicewa da d'imaucewa akan rashin kwanciyar hankali da masifa! Ta kama fad'ar kalmar "ina lillillahi wa inna ilaihirraji'un!! Na shiga uku ni Nusaiba wannan bala'in dami yayi  kama?,,,, dan Allah ku tashi karku tafi ku barni cikin bak'in cikin rayuwa da k'unci ".Ta shek'a da gudu ta d'auko wayarta ta dialling numbar baba Nura cikin tashin hankali da rikicewa! Tana kuka ta sanardashi abinda yake faruwa cikin gidan yace mata gashi nan zuwa shida su baba Nazifi,, ya katse wayar ita kuma ta dawo wurinsu Mama Nafisa tana wani irin rikitaccen kuka jikinta sai rawa da makarkata yakeyi akan tsoro da fargaba!.

Babu jimawa sosai sai gasu baba Nura sun shigo cikin gidan cikeda matuk'ar sanyin jiki da tashin hankali,,, damuwa ce da bak'in cikin rayuwa da ya bayyana akan fuskokinsu suna zuwa wurin gawar Fadila sukace "ina lillillahi wa inna ilaihirraji'un Allahumma ajirni fi musibati wa'akhalufni khari minha!!.

Baba Nura ne yayi k'arfin halin d'ebo ruwa ya yayyafawa Mama Nafisa da Fatima,,, sannan ya umurci Fadil da yaje ya sanarda mutane da kuma maigari abinda yake faruwa,,, Fadil ya fice da saurinsa cikeda k'unar zuciya da tashin hankali!.

Baba Nazifi ya shiga cikin wani yanayi mai cikeda tashin hankali da rikicewa! Ya kasa koda k'wakk'waran motsi akan ya shiga cikin yanayi mai ban tsoro da tausayi,,, baba Nura yaja hannunsa ya zaunar dashi sannan su Mama Nafisa suka farfad'o daga suman da sukayi,,, babu abinda yake tashi sai shasshekar kukansu cikeda matuk'ar damuwa da bak'in ciki!.

Bada jimawa ba saiga Fadil ya dawo da mutane akayiwa Fadila wanka,,, sannan baba Nura da baba Nazifi sukayiwa gawar addu'a suna zubar da hawayen tausayin kansu,, Umma Nusaiba ma tayi mata addu'a itadasu Nabila amma Mama Nafisa kasawa tayi sai kuka takeyi mai cikeda bak'in ciki da k'uncin rayuwa,, haka dai aka sallaci gawar Fadila bayan angama sallar ne aka kaita makwancinta na gaskiya!.

Aranar nan iyalan gidansu Fadila sun kwana suna zubarda hawayen rashinta da bak'in ciki mara misaltuwa,,, ita kanta Fatima da batada lafiya sai kuka takeyi cikin k'unci da bak'in cikin rayuwa.

_Duniyar kenan Allah ubangiji yasa muyi k'yakk'yawan k'arshe yasa aljanna ce makomarmu_..

********************

Duk abinda yake faruwa Iya Gwamma tana gani acikin madubin tsafinta,,, babu abinda takeyi

sai k'yalk'yalar dariyar mugunta harda fad'uwa k'asa akan makirci da k'eta,,, saboda murnar ta kashe Fadila burinta ya cika wani irin farin ruwa ke fitowa daga cikin jikinta sosai ga wata sansanyar iska mai dad'i da take buso mata,,, babu abinda takeyi sai surutai da tsafe tsafenta can ta bud'i baki tace "dama na gaya maki ba'a ja da mayyu akwana lafiya,,, saboda haka yanzu na kasheki na kashe banza sauran k'awayenki suma na gama dasu saboda ni arayuwata babu tausayi ko sassauci acikinta !".

"amma bari yanzu inje insha iska in dawo sai inzo in d'ora daga inda na tsaya! In kashesu Fatima Hhhhhh hhhhhh".Inji Iya Gwamma tana gama fad'ar wannan maganar,,, ta b'ace b'at kamar bata tab'a wanzuwa awannan wurin ba......
[7/12, 1:17 PM] Mugiratmusa66: 🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥
*MAYYA CE*
🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥

*INTELLIGENT WRITER'S ASSOCIATION ®*✍🏻
_[Onward together]_

*Written by Mugirat Musa*

*DEDICATED TO SIS NAJER'ART*

_Bismillahir rahamanir rahim_

*Maman Ummi ina godiya sosai da soyayyarki gareni matuk'a da kuma halaccinki,,, hak'ik'a ke masoyiyata ce ta gaskiya kin nunamin k'auna a zahiri,, Allah ubangiji ya saka miki da mafificin alkhairi kuma ya biya miki buk'atunki na alkhairi.*

*PAGE 31*

Tana b'acewa b'at bata sauka a ko'ina ba sai a can bayan gari cikin d'an daji,,, tana bayyana a cikin dajin tayita yawonta da shawagi tana d'ebo wasu itacen da zata had'a tayi wani maganin sihiri,,, bayan ta kamalla d'iban duk abinda takeso daga cikin dajin,,, saita juyo ta fara tafiya domin komawa gidanta,,, tayi tafiya mai nisa harta kusa shiga cikin gari kwatsam! Babu zato babu tsammani taga Ummaru d'an Sala mafarauci agabanta kamar an jefosa,,, ta murza idanunta domin tabbatarwa idan ba mafarki takeyi ba,,, gabanta ya buga da k'arfi rassssss! Hankalinta yayi k'ololuwar tashi sosai amma ko a fuskarta bata nuna masa ba,,, tayi tsaye tana jiran taga irin abinda zai faru atsakaninsu. Ummaru ya dubeta yayi murmushin mugunta da jin dad'i,,, sannan yayi mata walak'antaccen kallo yace "kin gama b'oye b'oyenki da guje gujenki Gwamma mayya,,, dama na gaya miki idan kere yana yawo zabo ma yana yawo wata rana dole su had'u,,, saboda haka yanzu nan zan gana miki azaba sannan in shiga dake cikin gari kowa ya ganki a walak'ance! Sannan in kasheki kamar yadda kike kashe wasu ".Iya Gwamma ta bushe da mahaukaciyar dariya sosai sannan tace "Ummaru kenan ka d'auka kasheni abu ne mai sauk'i awurinka,,,ko ubanka Sala mafarauci na kashesa cikin sauk'i bale kai! Saboda haka k'aryarka tasha k'arya ka kaini a walak'ance cikin mutane,,, saina gana maka azabar da baka tab'a shanta ba a rayuwarka! "."yimin shiru bak'ar annoba dangin tsiya,,,, idan kin saba kashe mutane acikin sauk'i,, toni naci dubu sai ceto ba zaki iya jadani ba Gwamma azzaluma macuciya mai cin naman mutane da aljannu! ".Cewar Ummaru d'an Sala mafarauci cikeda matuk'ar hasala,,, Iya Gwamma ta dubesa da idanunta jawur kamar barkono,, jijiyoyin kanta suka tashi tsaye rud'u rud'u akan b'acin rai k'arara tace "hak'ik'a ka tafka babban kuskure daka tunkareni gaba da gaba,, yau zan shayar dakai d'acin mutuwa ayau sai dai uwarka ta haifi wani amma ba kai ba! ".Ummaru ya harareta yace "sai an gwada akan san na k'warai,, saboda haka yau zan gabatar dake durk'ushe agaban mutane domin kowa yasan Gwamma mayya,, shahararra azzaluma mara imani azuciyarta ".Kai! Ya isheka ayau zakasan ka zageni saikabi ubanka acan lahira! In yaso ka iskosa acan barzahu! "Cewar Iya Gwamma cikeda hasala da jin haushi,,, Ummaru yace "karki kuskura ki gayamin maganar banza shegiyar karuwa! Annobar gari k'are dangi,,, wadda tayi abin kunya acikin gari ".

"yanzu kuwa zan nuna maka ainahin wa ce ce Gwamma ".Ta rufe bakinta ta afka masa suka rungutsume da azababban fad'a mai cikeda tashin hankali da bala'i! Naushin juna da bugun juna kawai sukeyi cikeda matuk'ar dauriya da zafin nama,,, Ummaru yana amfani da takobinsa domin ya kare kansa yayinda Gwamma ke jifarsa da ababen tsafi irinsu wuk'a,, mashi,, wuta,, kibiyoyi da dai sauran abubuwan mugunta iri iri daban daban,,, da bala'i yayi bala'i ta dinga feso masa wuta jawur yana kaucewa,, ta k'ara karanta d'alamisai na tsafi wata irin bak'ar guguwa ta bayyana,, ta d'auki Ummaru tana hajijiya dashi asama yasha wuya sosai sannan yayi wata addu'a,,, guguwar ta b'ace b'at kamar k'iftawa da bismillah,, ganin haka ne yasa ta k'ara yin wani sihirin k'aton rami da macizai ya bayyana a tsakiyarsu! Yana bayyana igiyar tsafi ta fito daga cikin ramin ta d'aure k'afafun Ummaru tana jansa da k'arfi,, yasha bak'ar wuya sosai sannan yayi wata addu'ar ramin ya b'ace b'at kamar bai tab'a wanzuwa ba! Iya Gwamma ganin ya tsira ne yasa ta k'ara harzuk'a da hasala ta feso masa ruwa tafasasshi suka zuba ajikinsa! Ummaru yayi kuwwa da kururuwar da k'arfi akan zafi da rad'ad'in ciwon ruwan zafi,, fatarsa jikinsa ta fara kwayewa akan masifa ganin ya fad'i d'immmmm ak'asa yasa Iya Gwamma ta bushe da mahaukaciyar dariya sosai tace "bazaka iya ja dani ba Ummaru,,, ubanka ma baisha d'a dad'i ba a wajena! ".Tana gama yin magana ya taso cikeda matuk'ar zafin nama ya naushi fuskar Iya Gwamma cikin shammata,, ai kuwa ta fasa gigitacciyar k'ara da kuwwa da k'arfi! Bakinta ya fashe da jini tasa hannunta ta lakato jinin dake zuba daga cikin bakinta,, tana ganin abinda ya faru da ita rayuwarta ta k'ara b'aci idanunta suka k'ara ja ta girgiza sannan ta rikid'a ta koma gwaggon biri,,, ta sake afkawa Ummaru suka sake rungutsumewa da wani rikitaccen fad'a cike da bak'in rai da mugun nufi! Dajin gaba d'aya ya kama girgiza da rawa tanbal tanbal kamar zai kife acikin k'asa,, masifa tayi masifa bala'i yayi bala'i dajin gaba d'ayansa ya kama da wuta yana k'onewa,,,tsuntsaye da dabbobi sai hijira sukeyi suna barin dajin baki d'ayansa.

Haka dai suka cigaba da azababben fad'a cikeda tashin hankali! Ummaru ganin wankin hulla zai kaishi dare yasa ya k'ara k'aimi,, tareda tattaro dauriya da zafin namansa ya chanza salon fad'ansa nan da nan ya rikita hankalin Iya Gwamma,, ya samu ya yanketa a cinyar k'afar dama ihu da kururuwar Gwamma kawai kakeji ta fad'i k'asa cikeda matuk'ar zafi da rad'ad'in ciwo! Ummaru yayi hanzari da sauri yasa igiya ya d'aure Gwamma,,,, ya d'auketa ya azata saman kafad'unsa ya nufi hanyar zuwa cikin gari fadar maigari Garba.

*******************

Alhaji Suleiman da Mama Sa'ima sunje gaisuwar rasuwar Fadila cikeda jimamin mutuwa da sanyin jiki,, anan ne suke k'ara jajantawa juna hak'ik'a Mama Nafisa tayi matuk'ar basu tausayi sosai,,, saboda duk ta fita acikin hayyacinta kallo d'aya zaka yi mata kasan tana cikin rad'ad'in zafin mutuwar Fadila,, anan ne Alhaji Suleiman yake sanarda baba Nura akwai Malam Usama da zaizo gidansa yayiwa su Fatima magani,,, baba Nura ya nuna babu matsala ya umurci Fadil daya d'auki Fatima ya sanyata cikin motar Alhaji Suleiman,, Fadil ya d'auki fatima ya sanyata cikin motar baban Maryam,, shima ya zauna bayan motar rungume da Fatima Alhaji Suleiman yaja motarsa suka wuce direct zuwa gida.
Ya parker motarsa a waje sannan suka fito daga cikin motar gaba d'ayansu,, Fadil ya d'auko Fatima daga cikin motar suka nufi cikin gidan suna shiga suka iske Malam Usama zaune,, Alhaji Suleiman yayi murmushi tareda bayyanar da farin cikinsa da fara'arsa,, yaje wurin Malam Usama sukayi musabaha da sallama da juna,, Mama Sa'ima ta shige cikin d'akinta.

Malam Usama ya aje casbaharsa da qur'ani agefe,,, ya kalli Alhaji Suleiman yace "akawomin ruwa masu tsabta yanzun nan ".

Alhaji Suleiman yace" to Malam Fadil jeka ka kira Maman Maryam sannan kace tazo da ruwa masu k'yau".

Fadil yace "to baba ".Tareda mik'ewa tsaye ya nufi hanyar zuwa d'akin Mama Sa'ima,, babu jimawa sosai saiga Mama Sa'ima ta fito tareda Fadil d'auke da jug d'in ruwa a hannunta,, suna isowa ta aje ruwan agaban Malam Usama ta koma gefe ta zauna.

Malam Usama ya d'auki ruwan ya fara karatun qur'ani da addu'o'i na tsari da sihiri,, ya jima sosai yana yin addu'ar sannan daga baya ya tsaya ya d'auko gagarin maganin ya zuba acikin ruwan yana jijjigewa da sauri,,, yana gama jijjigar ruwan maganin ya watsasu ajikin Maryam da Fatima ,,,ai kuwa batare da b'ata lokaci ba sukayi wani irin gigitacciyar k'ara da kuwwa da k'arfi! Suka kama zabure zabure da shure shuren zafin magani,,, Malam Usama ya cigaba da yi musu karatun qur'ani da addu'o'i kala kala,,, kuwwa da kururuwarsu Maryam kawai ke tashi acikin parlourn su Mama Sa'ima jikinsu sai rawar tsoro yakeyi itada Fadil cikeda matuk'ar firgita da fargaba! Ya dad'e sosai yana yi musu karatu sannan daga baya kowacessu tayi atishawa da k'arfi sau uku nan da nan barci ya d'aukesu batare da b'ata lokaci ba.

Malam Usama yayi murmushi sannan yace "Alhmdlilah yaran sun samu lafiya Alhaji Suleiman dama mayya ce ta kamasu,,, sannan ta had'asu da miyagun aljanu domin kada suyi saurin samun waraka,, yanzu dai godiya ta tabbata ga Allah ubangijin talikkai wanda ya bani ikon k'ona aljannu da yardar Allah,,,, shikenan da sun tashi daga barci sun warke har abada,,, zan basu wani turare da garin maganin da zasu cigaba da shafawa garin kuma wanka akeyi dashi ".Yasa hannun cikin leda ya d'auko turare kwalba biyu garin magani leda biyu,,, kowacce su d'ai d'aya.

Tsananin farin ciki da murna ne suka bayyana a fuskokinsu k'arara mara misaltuwa,, Mama Sa'ima hawayen dad'i ne suka cigaba da kwaranya daga cikin idanunta,, Fadil ma sai kwallar murna yake fitarwa,, Mubarak daya shigo ayanzu cikin parlour amma yaji abinda Malam ya fad'a bakinsa yak'i rufawa akan murna da farin ciki sosai,, ya samu wuri kusa ga Fadil ya zauna fuskarsa d'auke da farin ciki da nishad'i sosai.

Alhaji Suleiman akan farin cikin dake d'auke afuskarsa har rungume Malam Usama yayi yanata zuba masa godiya,,, tareda da kwararo masa addu'o'i na gamawa lafiya. Can ya bud'i baki yace "hak'ik'a godiya ta tabbata ga Allah ubangijin sammai da k'assai wanda yake sanya ciwo alokacin da yaso,, sannan ya warkar da bawa aduk lokacin da yaga dama,, Malam Usama mun gode sosai Allah ubangiji ya saka maka da mafificin alkhairi yasa ka gama da duniya lafiya ".

Gaba d'ayansu yan parlourn sukace "amin amin ".Fuskokinsu d'auke da farin ciki da nishad'i sosai k'arara,, daga gani babu tambaya kasan suna cikin jin dad'i da farin ciki sosai.

"wannan ba wani abu bane Alhaji ai an zama d'aya,, Allah ubangiji dai ya tsare gaba ni yanzu zan wuce zuwa gida ".Ya aje ledar maganin ya tashi tsaye ya nufi hanyar fita daga cikin parlorn,, Alhaji Suleiman ne ya bisa a baya domin yayi masa rakiya,, bayan sunje waje ne Alhaji Suleiman ya bashi kud'i masu yawa wanda shi kansa baisan ko nawa bane,, dak'yar Malam Usama ya amsa sannan sukayi sallama da juna ya shige cikin motarsa,, Alhaji Suleiman shi ko ya juya zuwa cikin gidansa fuskarsa d'auke da farin ciki da annashuwa mara misaltuwa.

¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤

Ummaru d'an Sala mafarauci d'auke da Iya Gwamma akafad'arsa,, ya kawota ya ajeta saman k'asa agarkar maigari Garba cikin halin somewa,, jini sai zuba yakeyi daga cinyarta yana ajeta saman k'asa,, ya shiga cikin gidan maigari ya jima sosai sannan suka fito tareda da maigari da dogarawansa,, nan da nan maigari yasa akayi sanarwa acikin gari kowa da kowa ya taru mata da maza,,, yara da manya da tsofaffi,, bayan mutane gaba d'aya sun gama taruwa wani dogari ya ciko bokiti da ruwa aka juyesu ajikin Iya Gwamma mayya,,, batare da b'ata lokaci ba ta farfad'o daga suman da tayi jikinta d'aure da igiya,, kallon mutane kawai takeyi d'aya bayan d'aya,,,Maigari ne yayi gyaran murya sannan yace "muna godiya ga Allah daya bama Ummaru nasarar kama wannan k'usurgumar mayya wadda ta addabi rayuwar mutanen gari shekara da shekaru,, ta dad'e tana cin amana da zaluntar mutane da dama ta kashe mana iyaye,,mata,,,,'yan uwa,,, yara da abokan arzik'i,,,, dama duk abinda kakeyi wata rana sai dubunka ya cika komai yayi farko k'arshensa yana nan zuwa,,, mai hak'uri mawadaci ne saboda haka gashi yanxu Allah ya tona asirin Gwamma an kamata !Dama na gaya muku duk wadda /wanda aka kama yana yin maita hukuncin kisa shine ya kamacesa,,, saboda haka yanzu nan za'a yankewa Gwamma hukunci dai dai da abinda ta aikata,, ina dogari Tukur ne yake? ".

Tukur ya matso da sauri kusa ga maigari ya durk'usa yace "gani rankashi dad'e ".

"kaje cikin gida ka d'auko fetur da tayar mota yanzun nan ka kawomin ".Inji maigari. Tukur yace "angama ranka ya dad'e ".Ya mike zubur da saurinsa ya shige cikin gidan maigari Garba.

.

Maigari ne  ya bada umurnin a d'auki Iya Gwamma amatsa da ita kusaga icce a d'aureta,, nan da nan aka cika umurnin maigari tareda daureta tamau ga icce,, Iya Gwamma sai kuwwa da kururuwa takeyi tana cewa "ku sakeni ku sakeni wallahi idan na kwance kaina duk saina kasheku,, saina  kasheku ! Nayi alk'awarin bazan bar ko d'aya daga cikinku ya rayu yaji dad'i ba,, Garba tsohon munafiki dakai zan fara kaida shegen yaron nan Ummaru! ".Haka dai suka d'auketa d'aureta ga iccen,, bada jimawa ba saiga Tukur ya fito da tayar mota da fetur  yana kawowa Ummaru ya amshi tayar da fetur,,, ya sanyawa Gwamma taya a wuya sannan ya dubeta yana murmushin mugunta yace"dama na gaya maki duk daren dad'ewa saina kamaki da hannuna,, shiyasa akeson mutum ya kasance mai aikata alkhairi akodayaushe akowane lokaci baki tab'a jin ance gaskiyarka ta k'are ba,, sai dai ace k'aryarka ta k'are saboda haka yanzu nan zan aikaki can inda kika saba aika mutane da dama ".Gwamma ta kama kuwwa da k'arfi tana kuka tana cewa "wallahi baka isa ba nice zan kasheka da hannuna,, saina kashe duka mutanen garin nan saboda su suka duka munafukan......... ".Bata k'arasa maganar ba ya kyasta ashana tareda zuba mata fetur ajiki,,, Iya Gwamma ta saki wani irin gigitaccen kuka tana cewa "kada ku kasheni wallahi duk sainaga bayanku,,, saina zare muku rai daga cikin gangar jikinku wayyo Allah ni Gwamma na shiga uku na lalace! ".....haka dai wuta ya cigaba da cin jikinta bal bal bal sosai sai kuwwa da kururuwar neman agajin gaggawa takeyi,, mutane sai kuwwace-kuwwace sukeyi na tsananin farin ciki da murna sosai,, kowanensu ka kalli fuskarsa farin ciki da murna ne bayyane afuskokinsu saboda ganin k'arshen Iya Gwamma,, Hassan ne na hango wani wuri zaune.......
[7/12, 1:46 PM] Mugiratmusa66: 🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥
*MAYYA CE*
🍥🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥🍥
🍥🍥🍥
🍥🍥
🍥

*INTELLIGENT WRITER'S ASSOCIATION ®*✍🏻
_[Onward together]_

*Written by Mugirat Musa*

*DEDICATED TO SIS NAJER'ART*

_Bismillahir rahamanir rahim_

*Ina godiya sosai matuk'a da soyayyarku da kuma k'aunarku gareni,, hak'ik'a ina matuk'ar farin ciki da kasancewarku acikin group d'ina saboda kuna sanyani cikin nishad'i da farin ciki mara misaltuwa.*

*Maman Haneef*

*Suwaiba Danabu*

*Maman twince*

*Ummu Shaheeda*

*Maman Hanifa*

*Ummu Usman*

*Maman baffa*

*Aishat Salisu*

*Ummeen Amatullah*

*His priceless jewel*

*Mom Hauwee*

*Khadijat Lookman*

*Hajja Saki*

*Ayshat*

*Firdausi Muhammad da duk sauran wad'anda ban ambata ba ina godiya sosai matuk'a sister's.*

*LAST PAGE*

*PAGE 32*

Hassan ne na tsinkayo yayi zaune yana tagumi,,, hawayen bak'in ciki da k'uncin rayuwa sai shatata yakeyi daga cikin fuskarsa,,, jijiyoyin kansa sun tashi rud'u rud'u idanunsa sunyi jawur kamar barkono,,, baba Labbo ma kwallar takaici da bak'in cikin rayuwa ne ke zuba daga cikin idanunsa,,, tausayin Iya Gwamma ne da takaici ya mamaye zuciyarsa ga wani abu ya tokare masa acikin k'irjinsa,, Suhaila tana ganin irin kisan gillah da walak'ancin da akayiwa mahaifiyarta ta fasa gigitacciyar k'ara da razananniyar kururuwa da kuwwa da k'arfi! Wani irin kukan bak'in ciki da k'uncin rayuwa takeyi da k'arfi nan da nan ta kama fisge fisge kamar mahaukaciya sabon kamu,, 'yan uwanta mata sukazo zasu rik'eta cak numfashinta ya d'auke ta fad'i k'asa d'immmmm ta some,,,, ina lillahi wa inna ilaihirraji'un!!! Kawai mutanen wurin suke fad'a tana fad'uwa mata 'yan uwanta suka d'auketa sukayi gidan mijinta da ita!..

Tokar gawar tana gama k'onewa,, wata irin mahaukaciyar guguwa da razananniyar tsawa suka bayyana k'arara atare,,, mutane da suketa kuwwace-kuwwace da yin farin ciki da murna akan mutuwar Gwamma mayya,,, guguwar ta fara d'iban mutane tana yassuwa k'asa rikcham da majinjiwa dasu,,, mutane suna ganin irin abinda ke faruwa kowa yace k'afa mi naci ban baki ba suka ranci na kare dimm dimm dimm,,, kawai ke tashi k'arar gudunsu!. Guguwar ta daina bin mutane ta tashi sama ta lulluk'a a cikin sararin samaniya ta nufi hanyar zuwa gidan boka LOK'ORO da saurinta!.

Boka LOK'ORO yana zaune kwatsam tokar gawar Iya Gwamma,,,tazo ta shige cikin jikinsa da sauri boka ya buga wata irin gigitacciyar k'ara da mahaukaciyar kuwwa! Yana cewa "ni boka

LOK'ORO na shiga uku na lalace! Banyi kaina adalci ba saboda arayuwata ban aikata alkhairi ba,,, gashin tokar shegiyar nan Gwamma mayya tazo xata kasheni,, domin Ummaru ya k'oneta da ranta wayyo Allah wayyo Allah na tuba kiyimin rai! Baxan sake aikata mummunan dabi'a da kashe mutane ba,, yau ni boka LOK'ORO naga takaina yau nayi mugun gan..... ".Bai k'arasa maganar ba jini da mugun tari ne ya sark'esa ya fad'i kwance k'asa yana shure shuren mutuwa da kakarin fitar rai! Sai da jini gunduwa gunduwa ya zuba sosai acikin bakinsa sannan ya fad'i k'asa d'immmmm ya mutu,,, aikuwa nan da nan batare da b'ata lokaci ba gawarsa ta kama wuta bal bal bal tana ci! Sai da wutar ta k'onesa k'urumumus ya zama toka,,, acikin tokar kana hango macijizai da kunamai suna yawo wurin ya gameda wani irin mahaukacin wari da d'oyin masifa da bala'i!.

Wa iyazubillah ina lillillahi wa inna ilaihirraji'un!!! Allah ubangiji ya rabamu da aikata shirka ya kuma sa muyi k'yakk'yawan k'arshe.

********************

Bayan wani lokaci ne su Maryam da Fatima sun warke garau kamar basu tab'a yin irin wannan ciwo ba,,, suka cigaba da zuwa makaranta da kuma rage yawon banza,,, da sukaji cewa Fadila ta mutu ta barsu suka kama yin kuka babu mai kama wani,,, aranar sunyi kuka fiye da tunanin mai tunani idanunsu sukayi jawur akan bak'in ciki da rashin Fadila,, iyayensu ne suke lallashinsu tareda basu kalamai masu dad'i har suka dangana suka barwa Allah komai.

Mama Nafisa da baba Nazifi,, Fadil sun hak'ura da dangana akan rashin Fadila saboda sunsan

Allah da yabasu ita yafisu sonta ya amshi ran abarsa,,, saboda haka ne suka cigaba da binta da addu'o'i da yawan karatun qur'ani domin ta samu rahamar ubangiji Allah..

Bayan mutuwar Iya Gwamma mutane suka cigaba da gudanar da rayuwarsu cikeda matuk'ar farin ciki da kwanciyar hankali,,, komai zasuyi cikin natsuwa sukeyinsa saboda sunsan an riga an kashe Gwamma mayya wadda ta addabi rayuwar mutane da aljannu! Sai godiya da addu'a sukayiwa Ummaru d'an Sala mafarauci akan irin k'ok'arin da yayi wurin kamata da hannunsa da kuma nuna matuk'ar jarumta,,, garin ya dawo dai dai farin ciki,, annashuwa,, jin dad'i,, walwala,, nishad'i,, da dai sauransu duk sun dawo cikin garin Gumi..

*ALHAMDULILLAHI.*

Duka anan ne na kawo k'arshen wannan littafi nawa mai suna *MAYYA CE*,,, da fatar mutane zasu d'auki darasin dake cikinsa su watsar da abinda nayi kuskure,,, sannan alal hak'ik'a maganar mayyu gaskiya ce bawai k'age ne nayi ba,, naman mutane sukeci dana aljannu babu k'arya.

Ina rok'on Allah ubangiji ya yafe mini kurakurren da nayi acikin wannan littafi,,, abinda nayi dai dai Allah ubangiji ya bani sakamako mai k'yau.

Godiya ta tabbata ga Allah mad'aukakin sarki wanda ya bani ikon gama wannan littafi lafiya,, ina mai numfashi da cikakkiyar lafiya sannan ina godiya ga dukkan masoyana masu bibiyar labarina da k'aunar wannan novel nawa.

*Ina godiya sosai da mik'a dubun gaisuwa ta ga wannan k'ungiya tamu mai tarin albarka,, INTELLIGENT WRITER'S ASSOCIATION kungiya d'aya tamkar dubu wadda ta tara shahararrun marubuta masu matuk'ar ilmi,, hazak'a,, fasaha da kuma iya tsara labari mai fad'akarwa da nishad'antarwa,, ilimantarwa Allah ubangiji ya k'ara d'aukakaku yasa kufi haka shahara da d'aukaka har k'arshen rayuwarku,, ya kareku daga sharrin mahassada da mak'iya..*

_Ni Mugirat ina muku fatar alkhairi a rayuwa masoyana,,, sai kun jini asabon novel d'ina mai suna *SOYAYYAR GASKIYA* nan ba dad'ewa ba...._

Mugirat ce